[8/15, 11:42 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

1

Official

By
AsmaBaffa

BISMILLAH

Alhmdllh fans Allah ya kawo mu sabon Novel,Allah yasa mu fara Ify mu Gama Ify,Kuma Allah ya bada ikon amfani da fadakarwarsa.

Pls Sharhi nake so da Haka zanfi Jin dadi typing,Kuma zanyi kokarin yiwa kowacce reply inshallah.

Son Kai zanyi wannan page Na ASMABAFFA FANS CLUB ne, ku zan fara bawa.😍😍😍💋💋💋.

Gombe state Kauyen Dingawa Babban kauye ne kusan ma kamar Local Government ne Amma ba a bashi LGA ba, garine na fulanin asali kana Shiga ba sai an fada maka ba.

Fadila Tahir shine cikakken Suna na,Tahir Adam tukur shine Sunan mahaifina,Tahir Adam tukur Asalin fulani ne mu Amma yanzu ba shanu sun Kare,Tahir Su uku ne duk maza iyayensu suka Haifa Wanda har yanzu Suna Raye kakanni na na wajen uwa Dana uba duk ba Wanda ya rasu suna da ransu, Babana shine Babba wajen iyayensa daga shi sai kaninsa kawu Salisu da kawu Usman, gaba daya Allah ya wadatasu Alhmdllh a kauyen Nan Babu masu kudinsu,harkar noma da siyar da kayan masarufi ne sanaarsu,Babana Tahir har mota kurkura da Golf yake dasu duk Ana jigilar Kai Kaya kasuwanni daban daban,Kawu salisu ma Yana da kurkura,Haka Iyayensu Baffa da Yafendo suna Jin dadi ba yunwa ba rashin sutura,sai abinda suke so, daga kakannina har iyayenmu duk sun je aikin Hajji,mune kawai yaran bamu je ba.

Suna da matukar biyayya sai abinda kakanninmu suka tsara shi sukeyi,Tahir da kannensa duk auren zumunci akayi musu,Salisu da Usman matarsu daya Basu Kara aure ba,Salisu Yana

da Yara Biyar manya samari guda biyu Mahmoud 28yrs da Umar 26yrs samarine kyawawa farare kasancewar Family dinmu kaf Babu Baki kowa fari ne tas sai dai wasu sunfi wasu fari.
Bayan Umar akwai mace wacce mate Dina ce Saratu18yrs,sai Zainab,da Kuma Abida Yar auta.

Kawu Usman kuwa yaransa biyu Rak Matarsa Bata haihuwa sosai Duk Mata ne Aisha da me Sunan Yafendo Fatima Ana ce Mata Mama.
Babana Wanda shine Babba Tahir Matansa biyu Babata itace ta farko da akayi Masu hadin zumunci Hajiya Hadiza muna kiranta da Hajiyarmu,Bayan Sunyi aure Ta haifi Salman shine 28yrs saurayi saan Mahmood ne Kuma abokai ne,sai kaninsa Musa saan Umar 26yrs, sai Ni Fadila Yar auta a wurin Hajiyarmu Wanda Kuma Ni kadai ce mace a gidanmu,Sai kishiyar Babar mu Haj Balki Amarya tana da Yara hudu Amma duk maza ne Kuma yarana ne kanana Babban 15yrs Abdullahi,Ramadan 12yrs ,Shahid 9yrs sai Ahmad autanta a yanzu 5yrs.

Duk da a kauye muke muna zuwa makarantar Gomnati da Islamiyya,Haka Salman da Musa tare da yaran su Kawu Salisu duk sun Gama HND a garin Gombe Sunyi service Kuma yanzu aiki ake nema musu sannan sai suyi aure Amma har yanzu aiki Bai samu ba sai da hanya Babba.

Ni Kuma na kusa candy muna Ss3 jarabawa zamu zana ta fita,sauran kannena suna secondary wasu primary,muna da kokari gaba daya danginmu Babu dakiki,Sabo da Kawu Usman Yana dauko mana Yan bautar kasa iri iri suna koya Mana turanci karatu da rubutu shi yasa muka iya turanci duk da cewar ba kamar masu yin makarantar kudi ba,ko mutanen birni,iyayenmu suna son juna suna da hadin Kai Amma duk da Haka mu yaransu ba a fiye Zama Ify ba,sabo da munafunce munafunce irin na dangi musamman iyaye Mata su ke haddasa fitina iri iri.

Hajiyarmu Allah yayota Masifaffiya ce number 1 a kaf kauyen Nan an San da zamanta sabo da masifarta,har mu yaranta Bata raga Mana,ita Bata fiye tsokana ba Amma idan aka tabo ta ba mutunci,shima Babanmu Tahir Abbu balainsa yayi yawa Babu Wanda ya kyale Amma Kuma Yana da Dan saukin Kai,ga addini,Kuma Yana da nutsuwa kamar Hajiyarmu matsalarsu rashin Kara da kau da Kai komai masifa.

Kishiyar Babarmu wacce muke Kira da Anty ita Kuma tana da hakuri gata Shuru Shuru sai kisan mummuke,a boye take shuka tsiyarta ga tsokana,shi yasa kullum fadansu baya karewa dare da Rana Amma kowa mutan gari laifin Hajiyarmu ake gani Ana tunanin ita take zalintar Anty sabo da ita Bata kyalewa idan anyi mata.
Babanmu kuwa shima yafi ganin laifin Hajiyarmu,shi yasa ya tsaneta ya tsanemu mu yaranta,Yaran Anty da Anty yake kauna.

Matan su Kawu Salisu kuwa magulmata ne su ke haddasa rashin zaman Ify a dangi,Kuma Kakanninmu sunfi kaunar Matan Kawu Salisu da Usman sai Anty da yaransu,basa kaunar Babarmu ko kadan,muma yaranta abin ya shafemu basa kaunarmu,Hajiyarmu Har danginta ba

wani sonta suke ba sabo da halinta na Saurin fada da masifa,Bata da kawaici iyayenta kadai ke Dan sonta,muma kakannimu na wajen uwa basa wani sonmu Wai bamu da kunya Yan iska ne mu sabo da kawai muna karatun boko mun Dan waye muna Yar kwalliya mun banbanta da mutanen kauyen shine kawai suka ce mu Yan iska ne Haka mutanen gari ma Ware mu akeyi,kawayena kullum zagina da gulmata sukeyi  akan nace zanyi University bazan yi aure ba sai naci da biro, Hajiyarmu tana daura min tallan Dafaffiyar gyada Ina kaiwa makarantar boko da ta yamma,sannan Ina sai da goro da Sassafe kafin na tafi schl sai nayi tallan goro,Sabo da Abbu baya son Hajiyarmu Bai Hana a daura min tallan ba,Amma yaran Anty hanawa yayi a Dora musu talla.

Takaitattun matsalar mu kenan Nan gaba za kuji Wanda baku San dasu bama.

Allah yayi min baiwar hakuri ban gaji iyayena wajen masifa ba,sanyin Hali gareni,ga tsoro,sannan Ina da matukar addini,sannan kaf danginmu Babu me kyauna da kokarina,nafi kowa kyau da fata me kyau kamar jinin balarabiya wasu sun Dan fini haske da kadan duk da cewa Nima farace Amma hancina Bai cika tsini ba Kuma ba gajere ba,sannan Dan bakina karami jajir,gashina Baki sidik ga tsayi ko kitso baya yi,har gadon baya,idona farare tas Dara Dara,tun daga gaban goshina zaka ga gashina yalala ya kwanto, Ni ba rammiya ba ba Kuma me kiba ba,ga shape dirina abin  kallo ne duk Wanda yayi tozali Dani sai ya kara, sabo da tsananin kyau na, idan baka sanni ba zaka rantse balarabiya ce  ni, Amma duk kyan Nan nawa bani da saurayi bani da mashinshini sabo da halin Hajiyarmu Babu Wanda ke son hada zuria da Tata an Gama yadawa da sharri iri iri ake yi Mana kowa yazo wajena sau daya bazai dawo ba,a cikin dangi za a samu wasu munafukai suje su fada cewar Yar iska ce Ni har cikin shege na taba yi an zubar,sannan suce idan ya aureni zan mallakeshi,ga Masifar uwata,duk kawayena anyi musu aure tuni, sai Ni kadai Wanda a rashin miji ne yasa nake Karasa secondary Amma da ace na Samu miji ko jss1 bazan je ba za ayi min aure,yaran su Kawu Mata du Sunyi aure suna da Yara biyu Kuma mate Dina ne.

Dangi an Kara tsanata Wai ni nake korar samari sai talla da iskanci a garin Ina kwalliya Ina iyayi,Hajiyarmu ma da Abbu laifina suke gani shi yasa suke Kara Jin haushi na,dangi ko biki ko suna bana iya zuwa kullum daga schl sai gida sabo da irin ci min mutunci da akeyi Akan Wai naki aure Nasa yaudara a gaba,dangin uwata ma Haka ga mutan gari,Haka nake Addua Ina kuka kusan kullum Allah ya bani Mijin aure ko wanne irine aura zanyi na huta da bakin cikin da nake kunsa.

Yaya Salman ne kadai da Mahmood suke lallashina sannan suna matukar ji Dani,Mahmood ya taba furtawa zai aureni babarsa Matar Kawu Salisu tace zata tsine Masa shine yasa ma ya hakura Dani.

Takaitaccen tarihina kenan.

Ci gaban labari.

Rataye nake da Yar Jakar makaranta ta wacce Ya Salman ne ya siyo min a garin Kaduna lokacin da suka je service, Uniform dina fes dasu Allah yayoni da Tsafta sosai kullum fes nake

ko Ina kungu da sako na jikina,ga Mahmood Yana yawan bani kyautar turaruka masu kamshin gaske dake su Yan gayu ne sun Gama wayewa sabo da karatunsu a birni sukayi.

Ina hanya na mike titi zan dawo gida sai ga motar Abbu Yana tukawa Golf ya rarako wuta kamar zai tashi sama Yana kallona Ina kallonsa Ina daga Masa hannu ko rage min hanya yayi sabo da makarantar Tamu da Nisa sosai ga Rana Amma ta window ya leko sabo da rashin tausayi Yana min Dariya ya wani daga min hannu irin sai na taho,gaba kadan kuma kannena ne su biyu yaran Anty Suma sun taso a gabana ya tsaya ya dauke su a motar suka tafiyarsu tare da bula min kura.

Bansan sanda Hawaye ya tsiyayo min ba,kawai na bawa zuciyata hakuri har na Karasa gida,Ina sallama gida Kuma ko kayana ban cire ba Hajiyarmu ta fara fada uban me kika tsaya yi a hanya banza shashasha kina girma kina hauka,na bude Baki kenan zanyi magana ta dungure min Kai Dalla rufe min Baki sai ki dauki abinci kici kiyi Shirin Islamiyya ga gyada ta tana jiranki ki tabbatar kin siyar, sabo da takaici ban iya cin komai ba wanka kawai nayi tare da Shirin Islamiyya, Ya Salman ne ya shugo tare da kallona yayi Murmushi yace Sister kinci abinci kuwa? Ganin Hajiyarmu zata min fada kawai nayi Murmushin Dole nace sai na dawo bana Jin yunwa, da masifa Hajiyarmu tace me bakin Hali munafuka Wai fushi tayi Akan an Mata fada baza taci ba, Anty uwar tsokana tace kanki kika yiwa cikinki yarinya,gandareriya dake kice baza ayi Miki fada ba,idan Haka kike so ubanwa ya hanaki aure ki tafi dakin mijinki sai kiyi abinda kike so..

Hajiyarmu Bata so wani yayiwa yaranta fada sai ita ko Abbu Nan take ta hayayyakowa Anty da fada yarki ko tawa?,Ina ruwanki,kije kiji da yaranki uwar iya Yar shishigi, Musa ne ya taka musu birki Wai Dan Allah Hajiyarmu me yasa kuke Haka ne why? Kun girma Amma bakwa gani,Ubanka kayiwa turanci ba Ni ba,sabo da kaga bama Jin turanci zaka zagemu da yaren nasara cewar Anty,Hajiyarmu Kuma tace Wai shi Dan boko to Munga Nasara ma marar tarbiya fitsararre.

Salman dai Hannuna yaja Ni Kuma na daura faranti gyada ta a kaina na bishi muka fita tare, har bakin titi ya rakani muna hirarmu ya tsaya wajen masu soya doya da kwai tare da egg in to egg ya siya min na dari biyu harda lemon kwalba mirinda da ruwa pure water guda biyu ya bani a Leda sai ga Mahmood Dan Kawu Salisu suka rakani har schl sannan suka tafi zasuyi Shirin zuwa filin ball dake kauyen.

Naje schl Ina tunanin rayuwata ko karatun yanzu na daina fahimta burina na siyar da gyadar dana zo da ita schl Kar na koma gida Naci duka wajen Hajiyarmu.

Haka na dinga zaga class dake makarantun kauye ne na Gomnati ba damuwa akayi da ilmin ba Babu ruwansu.

Ajin Yara na Shiga lokacin anyi break Ina so su siye min gyada ta,na fara musu wayo kasancewarsu Yan primary, wani bench na Yara na Samu duk sun fito da kudinsu zasu fita break na zauna saman desk na washe musu Baki nace Yan Yara Yara gyada me sihiri Ina tafi dama sun San wakar sai ko suka fara Baki daya ajin Ana tafi Ina bawa Yara guda biyu,suna ci nace duk Wanda ya siyi gyadar Nan zan bashi alawa me dadi,Nan Yara suka dinga turuwar

siyan gyada da alawata a jaka Ina Basu daya daya,suna siya,kafin kace me sai ga wasu yaran ma na wani ajin muna rera waka,watarana ma idan na faki idon yaro kawai sai na kwace kudinsa na bashi gyada ta kudinsa Dole ya hakura yaci,Dan da Nan na siyar da gyada tas.

Wurin Magrib muka tashi daga schl sai gida,Ina dawowa ranar Girkin Hajiyar mu ne Haka tace yawwa maza je ki karasa min girkin can,Haka ba hutu na Karasa na Gama tuwon shinkafa miyar Danyar kubewa da kifinta dake gidanmu ba laifi muna cin me kyau,Kuma gidan mu ba na kasa bane na bulon siminti ne ko Ina a shafe sumul yasha fenti.

Ina gamawa zanyi wanka kenan na huta Anty ta Miko min katon botiki tace tuzuruwa ebo min ruwa a tuka tuka na waje,tsakanin uwa da danta sai Allah Hajiyarmu karaf a kunnenta fuuuuu sai gata ta fito ta kwace bokitin a Hannuna tayi ball dashi Nan take ya fashe,sai ga Abbu ya shigo daga masallaci,ganin Anty Amarya aka yiwa laifi ya fara masifa kamar zai cire bakinsa sannan ya kalleni tare da cewa zo ki tafi makarantar dare Dan ubanki mene amfaninki,ya kawo min duka Hajiyarmu ta Kare ya sameta a hannu, Hajiya ta kwalla ihu da uban karfi Wanda ya dawo da hankalin makwafta gidanmu,hannu aka ta Dora tana an tsaneni an tsani yarana,sai ka kasheni ka huta,azzalumi tunaninku ban son yarana,Anty tuni Sumi Sumi ta koma dakinta tayi luf tabar Hajiyarmu da babatu mutane suka cika gidan Ana kallon Hajiyarmu a Masifaffiya marar ilmi Ana ganin ita ce ke zaluntar Anty sai zaginta akeyi ita kuma tana ta faman hayaki da masifa.

Kunya tasa gaba dayanmu muka bar gidan  sai dare wurin 10pm muka fara dawowa mu kullum gidanmu ba zaman Ify.

Da Sassafe Abbu yace na fito ya aikeni na siyo Masa petrol,Salman yace tana mace Abbu ka bani Ni na siyo ko Musa duk ga Yara sai Fadila zaka aika,Abbu wata Harara ya watsawa salman Wanda yasa Salman yin shuru ba shiri, ita nayi niyyar aike idan ta gaji ta fito da miji tayi aure., Kudin kawai na karba da jarka na tafi naje na dawo sannan nayi Shirin schl.

Abin takaici an fara registration na waec da Neco Amma da na sanarwa Abbu sai yace karatun ya mace bashi da Amfani a duniya Fadila nasan baza ki taba ci gaba a rayuwa ba,baza ki wuce kauyen Nan ba ko aure zakiyi to mene amfanin biya Miki makudan kudi haka,Dana biyawa mace taci gaba da karatu gwara na zubar da kudin,mene amfanin karatun boko wajen ya mace, Hawaye na fara ,sanyi,iska etc Dana Sha a banza bazan karbi certificate ba,ko bazan ci gaba ba ai na karbi Certificate a Hannuna.

Da kuka na fito daga dakin Abbu,Hajiyarmu tasan me ya faru Baki ta tabe duk ke kika jawa kanki da kinyi aure ai da kin huta, Ina Hawaye tare da rakubewa a jikin bangon dakina kamar almajira nace Hajiyarmu Wai komai ba Allah ne yake tsarawa Dan Adam ba Amma kamar baku San hakan ba,ai aure lokaci ne komai dadewa idan da Rai zanyi, rufe mana Baki ai Baki niyya ba komai sai da niyya yake tabbata kiyi niyya ki gani idan bakiyi ba ehe cewar Anty tsokana,Mahmood ne ya shigo gidan wurin Mahmood ya Iskeni Ina kuka,Kanwata me akayi miki? Nace Abbu ne yace bazai biya min Waec ba,Kuma naje wajen kawun Salisu da Kawu Usman sunce baza suyi asarar kudi ba Wai aure ne kadai idan zanyi zasu kashe min kudi Amma boko ai zunubi zasu kwasa ma, dariya Mahmood yayi Dan an biya boko mace tayi shine

za a kwashi zunubi,  lallashina yayi sannan yace Zamu biya Miki Ni da Salman dasu Musa ki daina kuka,Nan take farin ciki ya mamayeni.

Washe gari kuwa da safe Salman da Mahmood suka je suka biya min Waec da Neco, zo kuga murna Ina ta gode musu, Salman Yana dariya yace ki Bari yarinya Allah yasa muyi kudi Zaki ji dadi,nace Allah yayana?yace sosai ma,to Allah ya hore suka ce Ameen sannan suka tafi daga schl din.

Koda Abbu yaji cewar an biya min kudin jarabawa sai ya dinga fada,da sauri ya shugo yace Ina Fadila,nasan halinsa da gudu na fito nasan halinsa yanzu na Sha Mari,yace naji kinje kin Sa an biya Miki jarabawa ko? Wato Ni ban Isa ba,kin shahara to wlh sai dai ayi asarar kudin Amma Baki Isa kin zana jarabawa ba,ni Zaki tozarta,to zanga me iko dake tsakanin Salman Dani,daga yau na soke zuwa makarantar taki har Islamiyya, Wai ke sai kin ci da biro ko? Ai naji me kike cewa a garin sai kinci da biro,Rokon Abbu na fara Ina kuka,Abbu yace Abu daya zakiyi na kyaleki ki zana jarabawa,da sauri nace me zanyi Abbu? Aure ya bani amsa na gaji da gorin da ake min gari,da maganganu da ake Akan zuriyata,wlh kika sake sunana ya baci wlh kinji na rantse sai na koreki daga Gidana,Anty zaraf ta leko tace wlh kuwa yo yarinya ta Gama balaga a gida,ace kamar Fadila ta fara haila a gida,ga nonuwa kamar me shayarwa Allah yasa ma ba maza bane suka jawosu ta karfi sai wukil ta koma daki, Hajiyarmu wacce ke wanke wanke a bakin rijiya ta mike ta fara surfawa Anty masifa iri iri,Abbu ya zazzageta Wai Bata da hakuri ai fada Anty tayi min.

Haka Abbu ya fice fuuu,Salman Yana dawowa yaga yanda idona ya kumbura sabo da kukan Dana ci,me ya sameki Fadila,labari na bashi yaji haushin Abbu Amma sai ya min Nasiha yace nayi biyayya Allah Yana kallo.

Washe gari Ina kwance a dakina Ina tunani Ina hawayen dan ban San Ina yi ba,ganin kuka bazai Kare ba kawai nayi Alwala nayi Nafeela tare da Kai kuka na wajen Allah,karshe Nace Allah ka bani Mijin aure ko wanne iri ne Allah ko Mahaukaci ne zan aureshi haka.

Anan nake Jan hankalin Yan uwa Da yawa Ana samu idan mutum Allah yasa Bai yi aure da wuri ba ko mace ko Namiji sai dangi da mutane su takura Masa,Ana gulma Ana aibata wasu ko ace ma fasikanci sukeyi,a garin haka sai mutum yaje ya zabowa kansa wahala ya aura,zaka ji da yawa hakan na faruwa Mata suna Allah ka bani Miji ko wanne irine aura zanyi Haka sabo da halin da suke Shiga wajen iyaye,Yan uwa,kawaye da mutan gari.
Ana nunawa mutum shine yaki yi Ana mantawa da Allah.

Bayan wata daya Cikin Yan uwanmu wata ta haihu yau Suna shiryawa nayi naci kwalliya ta kamar Yar birni dama gani da uban kyau kamar asace Ni,Hajiyarmu ce ta takura min ita baza taje ba sai Ni na wakilceta Kuma na zaga danginta Dana Abbu, Haka na fito na iske samarin gidanmu tare dasu Mahmood a majalisarsu suna ta tsokanata nayi kyau daddawar daki yau ta fito,dariya na danyi na wuce na tafi,Ina sallama a gidan mutane damkam Ana ta cin abinci tun kafin na Shiga aka fara gulmata Ana kus kus, Abin haushin dangina Yan uwa dasu ake

zagina,tunda na Shiga wasu da gayya suke min habaici,wasu Kuma su fake da Wasa,da kyar nayi 10mnt na bar gidan, na fara zaga dangin Abbu duk inda na Shiga sai na fito Ina goge guntun Hawaye,Haka dangin Hajiyarmu ba hadin Kai Sam.

Gidan kakannina na wajen uwa ma suka sani a daki ta inda suke Shiga ba tanan suke fita ba,kakannina Yafendo da Baffalo sune naje na karshe,Yafendo tana gani na tace oh yau kece a garin,gashi Nan duk kin tsufa a gida,yanzu Yar Nan baza kiwa kanki fada ba? Wlh Nan da wata Uku idan Baki fito da miji ba to ko da ubanwa daura Miki za ayi.nan suka Karaci surutunsu na taso na bar musu gidan Yafendo tace Yar bantan uba me kafa kamar tabarya.

Bayan wata daya Ina wannan Hali da yamma na fita tallan Goro na dawo Ina kan hanyata ta komawa gida katsam naga mutane damkam a kusa da gidanmu Yara da manya ka rantse masallacin idi ne Mata da maza har da masu leke ta cikin gida Mata saman katanga, Wani Almajiri na tambaya me ake kallo me ya ta faru,Almajiri ya washe jajayen hakoransa yace Bature ne yazo Amma kamar mahaukacine fa an kasa ganewa Yana da hankali ko babu, Baki ganshi ba Dan gayu Dan birni Baki ganshi ba je ki gani.

Jin ance bature ne nace Nima baza a barni a baya ba,Haka na kutsa cikin mutanen har na Shiga inda baturen yake, sai da na kusa Suma sabo da cikar zatinsa da haibarsa ban taba ganin me kyau Haka ba,ai sai na ganni na dawo baka a kansa,kyau kuwa kamar shi yayiwa kansa sai ka lalace wajen kallon wannan bawan Allah sai wani kamshi yakeyi,Shadda ce fara Kar a jikinsa me tsadar gaske tana sheki,sai dai ta danyi dirty kadan,Kuma gefenta ya Dan yage kamar ma kusa ce ta yaga wajen bana mutuwa bane.

Gashinsa yawansa ya baci gashi me santsi ga wani sajensa Wanda ya taru da Dan yawa sai bakin Nan Pink abin shaaawa.mutane suna ta kallonsa shi kuma Yana jikin bishiya a zaune ya turo lips dinsa gaba kamar wani shagwababbe,a gabansa na tsaya,Ina ta kallonsa Ina washe Baki,ganin kallon Bai isheni ba a gabansa na tsuguna tare da Kara tura Masa fuskata saitin tasa,kamar zan Shiga cikin fuskarsa.

Abin mamaki ko kallona baiyi ba kamar Bai San da mutum ba,rigarsa na Dan ja ai kuwa ya kalleni kadan ya Kara turo Dan lips dinsa ya tsuke shi tare da make kafadar Shagwaba,a fili nace ah..ah...tofa sai na tintsire da dariya mutanen ma dake kallo suka fara dariya kamar mahaukata,wani yaro cikin Yan kallo yace Fadila Dan tabo Mana gashinsa muji,a hankali na Kai hannu zan taba gashin a tsorace,ai ko ya make min hannu ba tare da ya kalleni ba,ban hakura ba na Kara Kai hannu ya bige Hannuna ya mike tsaye a fusace idonsa har ya canja kala daga fari zuwa red,Alawata na Ciro a Jakar da nake Tara kudin tallana na Mika Masa ita,kallo na yayi kadan kamar bazai karba ba sai ko ya karba,abin da ya bamu mamaki ba tare da ya bare ledar ba ya cinye har ledar a Nan muka ce yana da tabin kai,mutane kuwa Kara yanyame wajen suke an samu a tsakiya.

Kallon mutanen yayi sai ya fara toshe hanci Yana ja da baya,sai ya fara buya a bayana, idan

na matsa sai ya matsa ya boye a bayana Yana leken mutane ta bayana,tsoro ya shigeni na fito daga mutanen nayi hanyar gida a guje, Abin mamaki Mutumin ya biyo Ni Amma cikin takunsa na Isa da gadara.

Gudun na daina na tsaya kawai sai ya biyoni mutane na binmu Yana buya a bayana,ban Shiga gida ba kawai na dauki hanyar wani shago cikin kudin tallan na siya Masa pure water Yana tsaye kusa Dani kamshin sa ya cika ko Ina,na Mika Masa ruwan ya karba kawai sai ya jefar a kasa da yatsa ya nuna min ruwan jarka da ake siyarwa,Baki na hangame nace Kai almubazzari Dan asarar kudi sai na roba ko Ni ban Sha ba sai kai,to wlh baka Isa ba, kudin Hannunna ya nuna da yatsansa sannan ya nuna min ruwan roba,a Shagwabe nace Kai baka San Ba kudina bane! Na Hajiyarmu ne dukana zatayi daga wannan Ni dai bazan siya ma ba,Dole na mika kudi aka bani na roba na bashi,sai na ga ya kasa budewa Yana ta gwagwagwa,na karba Ina masifa Kato da Kai Amma baka iya abin duniya ba ungo na sa Masa bakin robar ai kuwa ya shanye ruwan tas,Allah sarki kishi yake ji, biscuits ya nuna min Nan na gane yunwa yake ji na siya Masa biyu, Dana bude na bashi Bai iya ci da kansa ba Haka na bashi da kaina ya cinye, nace to ka tafi yawonka Ni gida zanje duk ka cinye min kudi na Ina ta masifa Amma yayi mursisi ko a jikinsa, Dana tafi Nan ma Bina yayi a Haka har kofar gidanmu,nace ka biyo Ni su Salman zasu koreka ne yaro ba ruwana Ni.

AsmaBaffa
[8/15, 11:42 AM] +234 813 228 4370: 🏕HADIN KAI🏕

2

Official

By

AsmaBaffa

Bai ce kala ba Haka muka je har kofar gidanmu babu kowa duk suna Masallaci sallar Magrib, Haka na shige gidanmu bayan na dauki kudina Dana kashewa Dan Bature na biya Hajiyarmu da kudina da nake Tarawa,muna zaune a tsakar gida Ana cin abincin da dare kawai sai ga Dan Bature ba ko sallama ya shigo kamar gidansu,Anty da yaranta tare da Hajiyarmu tuni suka fada daki da gudu tunaninsu Bature ne Dan wani fari ne tas ga uban kyau kamar shi yayi kansa,harsu Salman sunji tsoronsa kasa motsi sukayi,Abbu dake gefe saman carpet jikin dakinsa shine yayi ta maza ya daka Masa tsawa Kai Ify gidan ubanwa zaka je Haka? Shuru Babu amsa sai ma toshe kunnansa da Bature yayi sannan ya hade Rai tare da turo lips irin an takura Masa baya son hayaniya, dube dube ya fara can ya Hangoni saman katuwar Shimfidar tabarma Ina cin tuwo,a hankali cikin takunsa na birgewa ga uwar gadara gefena ya zauna kusa Dani a saman tabarmar,Su Anty da yaran gida sai lekenmu sukeyi,mamaki ya kamasu ganin banji tsoro ba,Baki Bude Abbu yake kallon mu, Su Salman ma Haka,Kwanan tuwona na tura Masa gabansa,ya zubawa kwanon Ido tunawa nayi baya iya cin Abu da kansa,Hannu nasa na yanke tuwon sannan na Kai Bakinsa ai kuwa ya bude bakin na saka Masa ya fara taunawa kamar baya so da gani Bai Saba ci ba kawai Dan Yana Jin yunwa ne yake karba Yana ci.

Muryar Abbu ce ta bamu tsoro yanda ya daka Mana tsawa,Iskancin naki ya Kai Haka dama? Shi yasa nake murna  da Allah Bai bani Yara Mata ba sai maza ke kadai mace Amma sai jawo min magana kikeyi to Zaki ci ubanki aure zan Miki na Dole Kuma wlh kika sake da mahaukacin Nan zan hada ki.

Kayi Hakuri Abbu taimako fa nakeyi wlh yunwa yake ji,Dan Allah ku daina ce Masa Mahaukaci duk Wanda ka ciyar Allah zai baka Lada ko dabba ce,Jar uba lallai zan karyaki a gidan Nan Fadila cewar Abbu, Hajiyarmu ce ta fito daga daki a tsorace ta kalli Dan Bature tace Kai tashi ka fitar Mana a gida,kallonta yayi sai ya koma ta bayana ya buya Yana leko da kansa ta kafadata, yau nake ganin Dan iska wannan ko a fili tantiri ne sai shegen Jan kunne,ga uwar Suma kamar dakin bukkar fulani.

Salman ne yazo ya fara kokarin Jan Bature zai kaishi waje Amma ya kasa Kuma yaki fita sai ma like min da yake faman yi a bayana, rada Salman yayi min a kunne cewar tashi ku tafi waje ki jashi ki San yanda zakiyi ku rabu mu rufe gidanmu kafin ran Abbu ya baci wlh duka Zaki ci kin sani ko ya Miki auren Dole kuma Kinga mu baza muji dadi ba.

Mikewa nayi na dauki wani kwanon na zubo Masa tuwo da Miya na rufe da murfi,Hajiyarmu tace a kwano na me kyau Zaki zubawa Mahaukaci abinci?ubanki ne ya siya min,to kudina nasa na siya Dan gwal ne da sai a kwano me kyau zaici?, Mayar ki zubo Masa a wannan tsohuwar langar wacce ta kwankwatse idan ta Bace ma taje,amma kwano na me kyau sabo a bawa Mahaukaci abinci a ciki ai kinyi karya Yar Nan,Anty ta leko tace Wai ita iyayi ga Yar me kudi komai nata sai anyi karya Yar karya kawai shine harda daukan sabuwar silver.

Bance komai ba na canja kwanon lokacin Bature ya biyo Ni har kitchen Yana buya,Hajiyarmu ta rike haba tana  Salati tace wannan yaron mashahurin Dan iska ne,Dan ubanki wlh ki kiyayeshi,Anty ta karbe da Allah ya kiyaye Kar ya dirka Miki ciki kafin ta rufe Baki Abbu yace da

kuwa na kasheta da Hannuna.

Bance musu komai ba nayi hanyar waje ai kuwa da sauri ya biyo Ni mun wuce Abbu kenan ya Sa Muficin da yake fifita dashi ya kwalawa Bature a kafafu Amma kamar dutse ya daka,Abbu ya sake rade Masa kafafu sosai da zafin gaske,Bai ko kalli Abbu ba yabi bayana muka bar gidan.

Can nesa da gidanmu saman wani dakali na zauna shima ya zauna a gefena,tuwon naci gaba da bashi ya ci da yawa kuwa nasan Yana bukatar ruwa haka na tafi shago Yana Bina a baya kamar jela na siyo pure water biyu na bashi daya da kaina wannan time din Bai nuna ruwan roba ba.

Saman dakali muka zauna na dinga Masa magana Amma Bai ce kala ba,nace Dan Allah ya sunanka? Yayi Shuru ba magana,ko Kai kurma ne? Nan ma Shuru, maganata naci gaba da fada Dan Allah ka daina zuwa gidanmu wajena Abbu na zai Duke Ni,Amma ban San Ina zaka kwana ba,ga hadari a gari tabbas ruwa zai zaneka wayyo ya zanyi na taimake ka ni. Haka dai na karaci surutuna na mike zan tafi gida ganin dare yayi da yawa,na gargadeshi Kar ya biyo Ni.

Nayi Nisa da tafiya kawai na hango shi Yana Bina a baya Nan na kwashe da gudu na fada gidanmu sannan na kulle kofar har Hawaye nayi na tausayin bawan Allah yau nasan idan anyi ruwa ba shakka zai zaneshi.

Shi kuwa Yana karatowa yaji gidan Gam a kulle sai ya zauna a bakin kofar gidan namu ya fara gyangyadi bacci ya kwasheshi.
Misalin Sha biyun dare na kasa bacci tunanin Dan Bature nakeyi gashi tuni an fara ruwa nasan ruwa Yana dukansa yanzu hawayen tausayi ya zubo min,a hankali na tashi na fito a dakina na lallaba naje na bude kofar gidanmu a hankali, Aiko na ganshi a zaune Ana tsinka ruwan sama kamar da bakin kwarya shi kuma Yana zaune ya dunkule waje daya ruwa na labtarsa Yana ta karkarwa.

Salman ne ya fito yaji kamar an bude gida tunaninsa barayi ne sai ya ganni Ina leke,yace Sister Ify?, Nace leko ka gani,ya leka yaga Bature shi kanshi ba karamin tausayinsa yaji ba,yace taimaka Masa ya kwana ko a zaure ne Amma Da Asuba ki zo ki fitar dashi kafin Abbu ya tarfa ki.

Dadi naji sosai shi Kuma Salman ya juya ya koma dakinsu,Da gudu na fito na Karasa inda Bature yake na Dan bugi bayansa da Hannuna ga ruwa ya Kara tsugewa, da sauri ya juyo ai kuwa ya ganni ba shiri ya mike tsaye duk da duhu Amma ya gane nice,karo na farko da naga Dan Murmushinsa kadan,ban jira ba kawai na figi hannunsa me Masifar laushi muka Shiga gidanmu, Salman ne ya kawo min wani kayansa Shadda Riga da wando Tasha guga yace gashi ki bashi ya canja Kar sanyi ya Masa Illa,sannan ya dakko min wani bargo guda biyu,ungo ki Masa Shimfidar da daya ki lulluba Masa,na fara Masa Godiya Ina murna yace ke dai kiyi sauri karfa a Kama mu ya juya dakinsu.

Bature na kalla Ina Murmushi nace cire Kaya n ka canja,kafada ya make alamar yaki, nace sanyi zai maka illa Ashe kana Jin magana,rigarsa na daga zan cire Masa ya zuba min uban yakushi saida ya dauke min fata, haushi naji sosai na bude kofar nace to fitar Mana a gida,kawai sai Naga ya fita kuwa yayi tafiyarsa cikin ruwan Nan ga duhu ya dauki hanya sosai.

Gidan na rufe na maidawa Ya Salman kayansa na koma na kwanta da kyar bacci ya daukeni Ina tunanin Bature yanzu Yana can ruwa Yana zaneshi. da Asuba na tashi nayi Alwala da sallah sannan na fara tasbihi da sauran azkhar har Rana ta fito gashi dama Abbu ya hanani zuwa makaranta talla kawai nake fita sabo da na duba Bature ko ya kwana lfy? Da wuri na Taya Hajiyarmu girki shayi muke Sha lafiyayye da kosai sai bread,sannan ga Koko da dumamen tuwo,Bayan na sake yin brush nayi wanka na fes na sa doguwar rigar atamfa ta me kyau nayi acuci da gashina tare da yafa Dan gyale na,sabo da kallo a waya yanzu mutan kauye ma sun waye ba a wuce su a iya wanka da kwalliya sabo da kallace kallace a waya, Kuma da yawa Yan makaranta basu fiye kauyanci da yawa ba, suna wayewa bare gidanmu da muke da Dan rufin asiri daga mazan har ni daban muke ga kyau.

Hajiyarmu ce ta kalleni ta tabe Baki ga kyau har kyau ba miji,yau Kuma tallan goron da wuri za a tafi haka? Anya ba akwai wata tsiyar da Zaki shuka ba nasan halinki Fadila, Murmushi nayi nace nafi so na siyar da wuri kafin mazan su tafi gona kin San tsofaffi da gona, Hmm to ya Naga kina wani nishadi ke da kullum fuska ba rahma Kuma sai wani zumudi kike Bayan tallan idan Zaki je kamar Zaki mareni Haka kike tafiya.

Shuru nayi Mata ta Kara tabe Baki tace dauki ki tafi tuku tuku mugun ice a Haka kamar saliha,Ni dai Shuru nayi na dauki talla na na fita Bayan na Shiga dakin Abbu na gaishe shi Yana muzurai Ni dai na fice abina,ko wajen tsofaffin banje ba,na fara duba gari ko zanga Bature Amma ban ganshi ba,hankalina ya tashi sosai na Shiga zagaye kauyen nan, har kusa da wani Rafi da mutane ke wanki ga bishiyoyi da ciyayi Kore Shar ga sanyin Niima a wajen,na duba ko Ina Banga kowa ba na juya hankali na tashe na fara tafiya naji an ja min gyalena kadan,a tsorace na juyo sai nayi tozali da Bature,kasa kallonsa nayi sabo da tsananin baiwarsa da kwarjini ga wani kyau me tafiya da imanin Dan Adam.

Ajiyar zuciya na sauke a hankali wani farin ciki ya cika ni, nishadi ya kamani gashi lfy Lau,juyawa yayi ya fara atishawar mura sosai,kayan jikinsa Sunyi dirty,hannunsa naji me matukar laushi cikin nawa ya rike Ni wani zirrrrr naji jini na ya amsa,Har gindin bishiya ya Jani sannan ya zauna Nima ya min nuni da na zauna,Zama nayi nace Ina kwana Bature? Bai ce komai ba ko kallona baiyi ba,na durkusa nace Ina kwana? Ya ka tashi? Ice ko dai lfy kake? Ya ruwa jiya Kuma sai kasha dukan ruwa gashi mura ta cafkeka Bature Kai dama ba kwari ba kamar fiigaggiyar kazar turawa kake.

Kallona yayi kawai ya hade fuska,nace Allah baka hakuri me yayi zafi Ni Fadila,da gani Amma Kai Masifaffe ne ko irin Hajiyarmu,wlh ka kiyayi kanka mutan gari zasu tsaneka tam ga Hajiyarmu abinda ya jawo Mata baking jini kenan har mu yaranta aka tsanemi.
Ido kawai ya zuba min Yana kallona nace ae ka kalleni da kyau Kai ba a Isa a Gaya ma

gaskiya ba sai kana fushi Haka ake rayuwar duniya fisabilillah kace baza a fada ma gaskiya ba to ya kake so ayi maka Kai kaki magana kamar jariri.

Yanzu kaci abinci ko da yunwa ka zauna? Shuru ba magana,Maganar kurame nayi Masa kaci abinci? Kai ya girgiza min Alamar baici komai ba,nace to na ganoka kurma ne kai Ashe? Bari na Nemo ma abinci karka biyo Ni ka jirani a Nan.

Zama yayi kuwa Bai bini ba na ajiye farantin goro na a gabansa Ina cewa ga ajiyata Nan ka jire min Kar ka Bari wani ya dauka, nayi tafiyata abina.
Da sauri naje na damu Mahmood da Ya Salman sai sun bani dari biyar zan siya wani Abu,Ya Salman yace me Zaki siya? Nace sirri ne idan zaku bani ku bani,Mahmood ne ya zaro dari biyar ya bani Ina Godiya na fyalla da gudu,na koma gida ba tare da kowa ya ganni ba na dauki cup me murfi,na Shiga dakin Salman na dauki kayan sawar da ya bani jiya na sawa Bature,da gudu na arce muka ci karo da Abbu Dan karma ya min magana na Kara karfin gudu na a tamanin fiiiiit na wuce shi, Ina jinsa yace Zaki dawo ne.

Table din  me shayi na na tsaya nace ayi min hadin kauri na dari,Bread na Hamsim,naje na siyo pure water biyu,na siyo tooth paste da brush sababbi na dawo inda na barshi me zan gani Yara sun taru a gabansa suna ta kallonsa suna tsokanarsa ga goro na Sunyi kaca kaca dashi a wajen suna iba suna watsawa kogin, ragowar Kuma suka gatsa su Yanda bazai siyu ba.

Da masifa na koresu,suna tafiya cikin sanyi na nace yanzu kana gani suka lalata min Kaya Haka? yau duka Hajiyarmu zata min,Bai kulani ba, haka na bude brush na matsa toothpaste ina Masa Zancen kurame ya taso kusa da rafin, na gwada Masa yanda zaiyi abin mamaki sai ya make kafada ya ballo abin bishiya yayi Masa kamar aswaki ya fara goge Bakinsa dashi, Haba shi yasa naga hakoransa neat kullum Ashe aswaki yake yi,a gabana ya goge ko Ina har halshensa can ciki, fushi nayi yaki karbar nawa yayi brush,kamar ya sani sai ya jefar da Aswakin ya Miko min hannu na bashi Brush din yayi abinsa kuwa,sannan na bashi pure water daya ya kuskure bakinsa, brush din na wanke na maida su leda, Ina Murmushi na sake Mika Masa kayan Ya Salman nayi Masa alamar ya sa harda Boxers, da kyar na rokeshi ya karba ya zaga Bayan bishiya ya saka kuwa Normal sun Masa kyau da yake yafi Ya Salman Dan kauri sai ya cika kayan tab yayi Masifar kyau kamar wanka yayi abinka da farar fata.

Kayan daya cire harda singlet da boxers nasa designers na kwashe na linkesu na zuba a Leda,agogon dake daure a hannunsa nake kallo na Diamond me kyau da tsadar gaske da wata azurfa zobe me kyau.

Tea din na bude nasan ba iya Sha zaiyi da kansa ba Haka na zage da kaina na dinga bashi da bread ya shanye tas,ya fisge ruwan dake Hannuna pure water saida ya ji min ciwo kadan a fatar Hannuna ya karce ni,  shanye abinsa yayi sannan na mike na tafi gida, shi Kuma a Nan gindin bishiyar yayi kwanciyarsa bacci me karfi ya kwashe shi.

Munafukai yaran Kawu Salisu Dana Usman har sun ganni duk abinda nakeyi suna sa min

Ido,tuni suka dinga yada Ni a gari har Zancen ya koma kunnen Abbu da Yan gidanmu,Bulala Abbu ya tanada Yana jira na dawo,mutanen gari Ana ta surutu Ina iskanci da Mahaukaci Dan na ganshi Kyakyawa iskanci na harda mahaukata nakeyi.

Babu Wanda ya nuna min a fuska har na Shiga gida,Ina tunanin me Hajiyarmu zata yi min ba goro Babu kudin goro,ina rabe rabe na Shiga gida,Hajiyarmu tace au Ashe ma kin siyar har nace Zaki gane kurenki nawa kika siyar kawo a irga kudin Lallai kina so nayi Miki kayan kitchen me kyau idan auren yazo inye watarana kirkinki yawa ne dashi.

Ina Ina na fara nace Uhm...wlh ba laifina bane Dan Bature na bawa jira ya bar Yara suka kwashe,Dan meeeeee kikace? Hajiyarmu ta tambaya tana turo min kunnenta daya tare da karkace wuyanta, Bature na Bata amsa kafin na rufe Baki ta gasa min mari, ta hada kaina da bango ta gwara min guf tuni na kwalla ihu ina neman agaji,Abbu ne ya shigo da Bulala ya kulle dakin ya Shiga tafkata Yana dama taraki nakeyi abin kunyar da kike jawo min ya isheni gwara na hallaka ki da Hannuna, bulalansa sai da suka karairaye a jikina yayi min jina jina,fuskata da jikina sun kumbura Sunyi shatin bulala, Hajiyarmu tana Kara Mata Malam.
Anty ta sheke da dariya tace yarinya anga me kyau Oh duniya yanzu ba a soyayya Dan Allah.

Haka mazan gidan harda Mahmood suka ce Suma sun daina kulani tunda bana Jin magana Ina Bata musu Sunan family bana jin magana,Ya Salman yace kin San Halin Abbu da Hajiyarmu idan kinwa kanki gata to ki daina kula wannan Mahaukacin wlh matukar Baki daina ba Babu mu ba Ke,a hankali nace ai kuwa wlh sai dai a kasheni Kuma kowa ma ya daina kula Ni din Amma bazan fasa taimakonsa ba.
Haka kika ce? Cewar Ya Salman nace ae sai dai kuyi hakuri,Baki bude yace to muma ba ruwanmu dake,nace ae kowa yayi harkarsa, Hajiyarmu ce ta Kara kwarfeni da Mari ta harbo Ni tsakar gida Ina kuka .

Sai Dana kwashe kwana uku Ina jinya ko fita banayi,Amma duk da Haka tunanin Bature nake ko Yana Raina so nake kawai na warke na Nemo shi.

Abbu Kuma sunyi meeting da Yan uwansa za ayi min aure Nan da sati Uku da Wani dan uwanmu Dattijo ne ma Talle, Talle yace Yana so na a bashi ai kuwa Abbu yace an Gama ayi shiri Amma Kar a Bari na sani sai dai naji kawai an daura,Akan Haka Ya Salman yace gaskiya baza ayi min Haka ba,Amma Abbu ya zazzageshi Dole ya kyalesu.

Bayan naji sauki na kwaso shardarsa tare da Singlet da boxers Dana kwaso na bashi na Ya Salman ya Sa,Sabulun wanki da Omo na dauka a tsakar gidan na zage na fara wankewa,gashi yamma tayi kowa Yana gida Musa da Salman tare da su Hajiyarmu mamaki ya kamasu, yanda na zage nake dirzar kayan Mahaukaci,Su Salman da Anty suka Shiga sheka min Dariya irin Nima na haukace,Abbu ne ya shigo yaga na wanke farar shadda fari tas Malam tana daukan Ido, faraarsa ta fadada yace ah Lallai yau Ashe Ladan mahaifi ake nema harda yi min wankin Kaya,Ya Musa suka kwashe da dariya tare da cewa Abbu kayan saurayinta ne Mahaukaci take

wankewa ta bashi kayan Ya Salman ya canja take wanke nasa,kalli Singlet din da Boxers kalarsu daban,Amma duk inda wannan guy din ya fito masu hannu da shuni ne.

Nan take Abbu ya Bata fuska yace Allah wadaran naka ya lalace ya mace daya tal ta buwayi mutane,Sha shashar banza, na kusa maganinki ya shige daki Yana fada ba ji ba gani,Ni kuwa naci gaba da wankina har Waka nake rerawa.

Bayan kayan sun bushe daf da Magrib na goge su tas,Kuma kamshin turarensa suna jiki Bai fita ba duk sun bulle gidanmu da kamshi, da dare na saci jiki na Kai rigar shagon tela inda kamar kusa ta yaga na bada hamsin aka dinke Dan wurin sannan na gyara ninkin na saka kayan a akwatuna.

Washe gari wajen Ya Musa naje nace ya ranta min dari biyar, da kyar ya bani,na fita na siyi sabulun wanka Giv da soson wanka sabo na saci jiki da kayansa a Leda har brush da komai,Ina fita waje ikon Allah na hangoshi a kofar gidan mu nesa kadan ya zauna a jikin bishiya abin tausayi sai kallonsa akeyi kamar watan Ramadan, Yana ganina ya saki wani Murmushi Wanda bani kadai ba har mazan ya sumar dasu dimple dinsa ya loba kyawawan hakoransa suka bayyana,cike da takunsa na gadara ya nufo inda nake Nima Murmushi na Shiga yi ba tare da na sani ba,kamar me hankali ya karbi ledar Hannuna ya bude ya duba sai Naga ya hade Rai tare da turo Dan lips dinsa, Yunwa kake ji? Na tambaya Kai ya daga min Alamar yaji me nace,Hannuna zai rike na boye hannun nace ba kyau zo mu tafi na Masa da Maganar kurame,Muka jera gwanin birgewa sai labari nake Masa Amma kamar da dutse nakeyi.

Ban tsaya ko Ina ba sai bakin titi shagon aski muka je dashi,da kyar na lallaba ya Shiga Haka Zama a kujerar ma Nasha fama dashi,nace me aski na Yan gayu Zaka Masa Dan kadan zaka rage Masa sumar ka Masa gyaran fuska sosai haka kuwa akayi sai gashi ya Kara wani mugun kyau, nace nawa?  Me aski yace kyauta nayi Masa sabo da taimako ne tunda bashi da hankali kuje kawai.

Cike da masifa nace Kai kiyayi kanka Kar ka Kara cewa bashi da hankali wannan da kake gani ya fika hankali da baiwa,yanzu idan da Kaine a matsayinsa ai dukan mutane zakayi Dan kayi Masa aski kyauta shine zaka zage shi ga hamsin Dinka Nan bama son kyautar.

Me aski ya taso da masifa kamar zai mareni Yana kamar ba Ke ba Fadila,kin canja ke da kike me hakuri da kunya ga kawaici Amma akan Mahaukaci kin lalata rayuwarki,idan Baki sani ba ki sani kaf garin Nan ba a kallonki da mutunci zaginki akeyi, tsakiya Bature ya Shiga ya kareni wani kallo ya watsawa me aski sai gashi yayi mukus.

Gidan wasu samari na tsaya nace Dan Asabe Dan Allah ku bashi aron bayinku zaiyi wanka Baki bude suke kallona,Rabiu yace Fadila ko dai kema kin zare ne Taya Mahaukaci zaiyi wanka?,a wajen nace idan zaku bashi ku bashi, daya cikinsu yace wlh kika sake sai na fadawa Abbunki kin San dai halinsa,Nan tsoro ya kamani na tuna dukan Dana ci nace Allah baku hakuri naja Bature muka tafi Rafi da ruwa ke zuwa garai garai.

Da kaina na gwada Masa yanda ake wanka Amma yaki yarda sai na bashi sabulun da soso nayi kamar na tafi na labe a Bayan bishiya,ya Dade Yana tunani sai Naga ya cire kayansa kaf daga shi sai Boxers ya Dan Shiga gefen kogin abin mamaki yayi wankansa tas yanda kowa keyi har ta cikin boxers din Bayan ya Gama ya fito kawai sai na rufe idona Allah yasa wajen ba mutane ya buya Bayan bishiya ya Sa boxers dinsa Dana wanke da singlet,sannan yasa shardarsa Tasha wanki da guga.

Ina kallo yayi aswakinsa tas,sai da ya Gama na dawo, na kwashe kayan daya cire na zuba a ledar.sai Hamma yake da alama yunwa yakeji.

Haka na siyo Masa soyayyar doya da kwai da ruwa na dawo na kawo Masa,hayam hayam ya cinye ya shanye ruwan da gani ya Dade rabonsa da abinci tausayinsa ya kamani,na koma na Kara siyo Masa shinkafa da Miya da wake Nan ma ya cinye tas ya watsar da sauran ya Sha ruwa, sannan nace taso muje yawo kaga gona alama na Masa da hannu ya biyo Ni.

Yana Bina muna tafiya Ina ta Masa labari iri Wanda Bai ko kulani ba.

AsmaBaffa

[8/15, 11:43 AM] +234 813 228 4370: 🏕HADIN KAI🏕

Official

AsmaBaffa

Gajiya nayi da Shuru din nace Wai ya Sunan babarka ne? your Mum, Mama, Ummanka,kallona yake ta faman yi da kyar yace uhm? Nace Mamanka Wacce ta Haifeka,tunani Naga ya tafi me zurfi ya dafe kansa maana Yana tuna abu, da karfi yace Mum...What? Mum alamar ya tuna,zumbur ya mike Yana Kiran Mum, Palon ya Shiga bi da kallo daya Bayan daya Yana lekawa tare da Kiran Mum,kansa ya sake dafewa sai Hawaye zarr suke keto Masa Wanda ya bani matukar tausayi ban San sanda Nima na fara nawa kukan ba,Jin sheshekar kukana ya dawo da hankalinsa wajena ya zauna da sauri kusa Dani

Yanda yaga Ina goge hawayena Haka ya Shiga goge min da kansa,ji nayi Ina wani Masifar kaunarsa kamar Dan uwana, Shuru nayi naci gaba da bashi abincin Amma kadan yake karba yanzu tunani kawai yakeyi.

Bayan mun Gama muka sake yin brush Wanda dama shi ya iya Brush baya gudunsa, nazo zan canja Masa kayan bacci Wanda Mahmood ne ya siyo Masa har kala biyu ganin ango ne.

Da kyar ya yarda na sa Masa, bed din na nuna Masa ya kwanta fafur yaki,yin duniya yakiya sai ma kasan ledar tsakar daki ya kwanta,Ganin da sanyi gashi sabon gini ne sai na dauko bedsheet na shimfida Masa nasa Masa pillow nace ya koma ya kwanta kai Amma yaki sam.

shi kasa zai kwana Dole na kyaleshi na haye bed dina na kwanta bacci ya kwashe Ni,tsakar

dare misalin 2am ya farka naji Yana ta kici kicin bude kofa,Ina kallonsa ya fita na bi bayansa a hankali ba tare da ya ganni ba,sai Naga ya nufi kofar waje zai bude ya fita, da sauri nayi gyaran murya tare da kamo hannunsa,Ganin haka sai ya saki Murmushin Jin dadi ya ganni don ya manta ma tare muke 1room baida tunanin da zai gane,sai ko ya biyo Ni da sauri ya rikeni kamar za a kwace Masa Ni,muka koma Bedroom,ganin idan har na koma bed nayi bacci zai fita sai na dawo kasa Nima kusa dashi na kwanta, Hannuna na sarke da nasa bacci ya kwashe Ni sannan shima yayi bacci again nasan shi mayen bacci ne.

Bamu farka ba sai da asuba na tashi nayi Alwala da sallah shi bacci yake Amma na tasheshi nayi nayi yayi sallah yaki yi sai hakura nayi dashi, baccinsa yake har 10am lokacin na Gama gyara gida neat ko Ina Yana kamshin turaren wuta, wanka nayi nasa sabuwar atamfa ta Yar dubu uku Tasha dinkin Yan burni Riga da skert sunmin daf daf sabo da aikin su ya Salman ne Yan gayu sune suka kaimin dinkin cikin birnin Gombe.

Ban iya dauri ba kawai nayi irin ture kaga tsiya powder kawai na shafa sai maroon jambaki, da kwalli abinka da fara sai nayi kyau sosai,gidan naji an kwankwasa na bude tare da lekawa sai Naga Ya Salman da kansa dauke da food flask kala biyu da na ruwan zafi, farin ciki ya kamani nace Ya Ina kwana, dariya ya Salman yayi ganin Ina tare da Mahaukaci Amma har wani cakarewa nakeyi haka Ina nishadi na ko a jikina,Lallai mace indai tace tana son Abu a kyaleta kawai.

Shugo Mana Yaya Hajiyarmu ce ta Aiko ka? Kin San Abbu yace baza a Baki ko ruwan tea ba a gidanmu Ni na siyo muku  a bakin titi ga tea Nan wannan kuma doya da kwai ne, Zan na kawo Miki har na kwana uku, Kai Amma na gode ubangiji Allah ya Kara budi gaskiya bani da kamarka Kana ji Dani fa,Har Palo ya shugo ya zauna muna hira,yace Ina angon naki Wai? Nace sa Ido kazo kawai? muna dariya nace bacci yakeyi,Kai ya jinjina sannan yace an gaisheki masoyiya yanzu Wai Allah kika iya kwana dashi Fadila?

Dariya nayi nace kune fa kuke tsoronsa Amma wlh ba wani Mahaukaci bane,Hmm Haka dai kikace Amma mutumin da ya kusa halakamu kiyi dai a hankali,muna Haka sai ga Dan Bature ya fito ya tashi daga bacci kenan, Baki bude Ya Salman ke kallonsa yanda yayi uban kyau haskensa ya Kara fitowa, cike da mamaki yace Wai duk jiya kika canja shi Haka? Lallai Sister Kya so abinki Dole kema ki haukace wannan ko dai balarabene ko Bature a farar fata ma samun irinsa sai an tona.

Wani farin ciki ya kamani an yabi Dan Bature,ji yanda kike murna,sunansa Aliyu ko yace? Da sauri nace ae Mana Ina wani fari da Ido ,dariya Ya Salman yayi sannan yace Allah ya shiryeki wlh Baki da kunya yanzu Fadila a gabana.

Nace uhm Bari nazo ka Dan jirani,Dan Bature Yana tsaye  jirana yakeyi naje,Yau ma Haka yayi Brush da kansa,na rufe idona na Masa wanka sosai ya Kara wani fresh,Ya Salman Yana jinmu a bayi muna ta gwagwa gwa Ina ta lallabashi ya tsaya.

Bayan mun fito muka wuce bedroom a gurguje na shiryashi na canja Masa shadda Milk color yayi mugun kyau,gashinsa na taje masa,flower dake gaban rigata ce ta tafi Masa da hankali ya

fara Wasa da ita Ina taje Masa Suma naji hannunsa saman kirjina yaji laushi sai ya janye hannunsa da sauri.

Dariya ma ya bani yanda ya tsorata, Yana kamshi muka fito Palo wajen Ya Salman Wanda mamakina ya cika shi,ga bawan Allah ya dawo mutum jiya daya Nan gaba ya za a ganshi kenan?,kusa Dani Dan Bature ya zauna.

Yana nuna min flask na bashi abinci, Ya Salman ya min Sallama ya tafi abinsa Yana mamaki yaje gida da wurin Frnds ya dinga Basu labarin yanda Dan Bature ya koma.

Haka Hajiyarmu ta dinga mamaki Abbu kuwa Baki ya tabe tare da barin wajen.

Ni kuwa tea lafiyayye yasha Hadi na zuba Mana a cup daya idan na kurba na bashi ya kurba ga bread ga doya da kwai , Yayi Shuru abinsa Ina ta Masa surutu nace Kana da Yan uwa kuwa? Kallona yayi ya turo min lips gaba Sigar Shagwaba,Murmushi nayi tare da ja Masa hanci kadan Kara daure fuska yayi,Bayan mun koshi naje Ina wanke wanke ya bude kofa ya fice abinsa. Kyaleshi nayi ya fita kowa kallonsa yake a garin Ana mamakin kyau da canjawarsa kamar a sace shi,matasa har tsokanarsa sukeyi da Ango Ana mamaki wasu na dariya.

Shuru Shuru Bai dawo ba har magriba tayi Ina jiransa ban ganshi ba,gidanmu daya sani tun farko yaje kofar gidan ya zauna Yana jirana,ya manta gidan da nake yanzu,su Ya Musa Sunyi iya kokarinsu na ganin sun ganar dashi gidan da nake a matsayin Amaryarsa Amma yaki ma saurararsu,Amma da ance Fadila sai yayi ta kallon mutum Yana Murmushi, Ya Musa har gida yazo min yace to Amarya aiki ya ganki Ango ya Gaza gane gidansa munyi munyi ya gane ya kasa kizo ki tafi da abinki aiki ya ganki ai.

Hijab na sa muka fito da Musa Ana ta kallon Amaryar jiya a waje Ana gulma naje har inda Dan Bature yake Yana ganina ya mike zumbur Yana Dan Murmushinsa ya kankame Hannuna nace Ina ta nemanka muje gida,hannunsa cikin nawa muka Kama hanyar gidanmu Ina fada masa kaga dai gidanmu can ka gane ko,kicibus mukayi da Abbu zai je masallaci,har kasa nace Abbu Ina kwana Baki ya tabe yace shashashar banza Kinga da me hankali kika aura me zaisa a ga Amaryar da aka Kai jiya ta fito garari a titi, Baki na turo gaba, naja Hannun Dan Bature muka tafi gidanmu,Abbu ya wuce cike da takaicina Amma fa yayi mamaki gani Angon Haka ya wani mugun haduwa.

Bayan nayi sallar Magrib Yana kallona shima ya fara kwaikwayo na Wai Yana sallah Ina Kara gyara Masa Yana faman gwadawa,sai ya tafi tunani sai ya kasa tunawa,yau ma Haka Ya Salman ya kawo min kaza Gasashiya da yogurt sai gurasa taji Hadi su Muka ci da dare, Bayan munyi wanka munyi Shirin bacci na zauna da fitila a gabana na lallabashi na yanke Masa faratansa tas na kankare, yauma a kasa muka kwanta Ina gefensa Hannuna cikin nasa sabo da Kar ya tashi cikin dare yace zai fita.

Cikin dare aka fara ruwan sama me karfi munyi bacci window a bude sanyi ya ratsa dakinmu sosai, Jin sanyi Yana bacci Bai San ya matso kusa Dani bama hannunsa ya daura saman cikina yaji dumi dumi ya juyo tare da shigewa jikina sosai ya kwakwumeni ya Gama kanannadeni a jikinsa,Nima Jin dumi yasa na kara lafewa muna baccinmu a nutse cikin nutsuwa fuskarsa yake

goga min a wuyana bamu farka ba yau sai da Rana ta fito munji dadin bacci.
a hankali na tashi,Ina zare jikina a nasa shima ya farka tar ya bude idonsa a kaina,sanye nake cikin kayan bacci Yar riga da wando shara shara,Surata ya Shiga karewa kallo kunya ce ta rufeni da sauri na dakko Hijab Dina na sa a jikina, Baki ya turo min ya jawo Hijab Dina yana kokarin dage min Hijab nufinsa na cire Baya sonsa, fuskewa nayi kawai na ja hannunsa Yana daga zaune, Mikewa yayi ya bini zuwa toilet gashi ban Isa yayi ko fitsari a gabana ba,sai ya turoni waje ya kulle kofarsa kamar me hankali abin Nan Yana daure min Kai.

Yau ma Haka yayi wanka da Brush da kansa yayi sosai,sai da ya fito ya kalleni fuskarsa ba rahma dake dama da wahala kaga dariyarsa sai Dole,Kirjinsa da surarsa tare da skin dinsa me sheki na tsaya kallo wani azababben kyau da yake karawa ga surarsa dirinsa hadden gaske ne ta ko Ina ya haru,Namiji ne na gaske.

Toilet na Shiga da ruwana cikin botikin karfe na wanka,ya bini da kallo Ina Shiga toilet ya biyo Ni ,sai da na tube na ganshi a ciki,Kara na saki kafin na dauko towel ya dauki soso na da sabulu Wai zai min wanka shima,towel na dauka Zan fita da gudu taku daya ya damko Ni tare da dawo Dani toilet din da karfi,Ina a tsaye ya kwace towel din a tsaye yake min wankan Ina zillewa, tsabar mugunta Haka ya dinga gurje min jiki da soso zafi sosai nake ji, har gashina ya wanke min Kuma ya iya Yana yi Yana tafiya tunaninsa daya saba,idan ya tuna sai yaci gaba,sai da ya Gama Dole sannan yayi waje abinsa ya koma Palo ya daklo Mai yanda na Masa jiya haka yayi ma kansa ya bude akwatinsa yayi Baja baja da kayan a tsakar daki ya zari farin yadi yasa abinsa,gashinsa ne kawai ya kasa tuna yanda na Masa jiya,sai da nayi brush da Alwala nazo na Karasa gyarashi, gabansa na tsaya wata Yar tsugul Dani Ina kulle Masa botin na riga,ba zato naji hannunsa a wuyana Yana taba kashin wuyana, wani shock nake ji a jikina wani dadi dadi, towel din ya sauke kasa ya daura hannunsa saman dukiyar fulanina, kunya ta kamani na jawo towel Dina a kasalance sabo da abinda yake min jikina ya mutu gashi abinda nake ji bama na so ya daina abinda yake min Amma Haka nayi karfin Hali na maida towel Dina, na juya Masa baya, ya fara kici kicin kwace Towel din nawa, ya Kara janyeshi ya jefar Yana min wani kallo kamar me hankali idonsa ya canja zuwa red kadan, abin ya daure min Kai,Haka ya fara latsasu kamar Yana Jin tsoro Ni Kam na Gama tafiya bazan iya hanashi ba,kafafuna sun Gaza daukana sai saman bed na fada,shi Kuma bazai hau bed ba,sai ya rike Hannuna ya jawoni na mike tsaye,da sauri na fada Kirjinsa na rungumeshi Ina sauke numfashi.

So yake Dole Wai sai na tsaya sosai ya taba kirjina Ni Kuma naki yarda na kankameshi,so yake Kuma ya yakice Ni daga jikinsa naki yarda,kokawa muka fara na bi na makalkaleshi, tun Yana Murmushi ya koma dariya yanda na fara Masa cakulkuli,yanda yaga Ina Masa shima ya fara ramawa Ina dariya ta Dole na bar jikinsa tare da fadawa saman bed nasan bazai hau bed ba baya sonsa.

Kallona yakeyi sosai Yana Murmushin dake narkar min da zuciya,yau ma material nasa sabo dal doguwar Riga,ba karamin kyau nayi ba Yana tsaye na Gama shiri na, ganin dazu na rungumeshi Ashe ya koya ta baya naji ya rungumeni sosai a jikinsa wani irin Abu nake ji Yana min yawo a jini na idan ya tabani shock na tashin hankali ke damuna.

Yau ma Ya Salman ne ya Aiko yaro da abinci ya kawo min tun daga na safe har Rana,misalin 5pm Bayan min sake wanka mun shirya Angona Naga zai fita,nasan ban Isa na hanashi fita ba,mayafina na yafa kawai na bishi ya rike min hannu muka fito gari,Haka ake ta kallonmu muna yawo binsa kawai nake har ya gaji nace to mu koma gida Magrib tayi,Yana ganewa yanzu idan nayi magana ko na koya Masa Abu to ya koya kenan.

Sati biyu tsakani lokacin Ya Salman yace naci gaba da girki ya Gama siya Mana abinci,Sosai nake zagewa Ina gyara Dan Bature yanzu in ka ganshi kamar wani wankin engine Babu Wanda ya Isa yace Yana da tabin hankali,gashi wani gentle wani kyau yake karawa,Nima har kiba nayi da haske,Sallah ma yanzu Ina koya Masa Kuma Alhmdllh duk ya iya,watarana ma idan na fada Masa sai ya Lula tunani sannan zanga ya tuno yayi dai dai,da yawa yan tuna Abubuwa da dama.

Da dare Kuma kullum a kasa muke kwana tunda baya son Bed,ya rigada ya iya shirya kansa wanka da komai, mun Kara Zama so close dashi mun wani irin Shakuwa ta daban,yanzu mun Saba idan ma zamu kwanta Ina saman Kirjinsa ya rungumeni haka muke bacci ko ya shige jikina abin shaawa.

Yawo ma da yake fita ya daina kullum muna tare kafata kafarsa,komai na aikin gida ganin Ina yi shima ya koya tare mukeyi, har karatun addini Ina koya Masa gashi da Brain tana ja,duk Wanda yazo gidanmu a dangi ko mutan gari sai mun birge mutum yanda muke muamula,Haka watarana idan Ina so mu shaki fresh air zamu ci wankanmu dai dai talaka Mai rufin asiri mu fita tare.yanzu kawai baya son mutane ko fita baya son yi.

Yau ma muna zaune a Palo saman 3seater  na gaji na zame nayi matashi da cinyarsa, Fa.dila..naji ya Kira sunana karo na farko cikin wata muryarsa ta musamman yayi mugun iya fadan sunan sai da tsigar jikina ta tashi yarrr.

Naam na amsa tare da kallonsa Ina daga kwance,mene kake so? Kirji na ya shafo a hankali yace wannan ya sunansa ma kika ce? Oh...na tuna Boobs ko? Kai kawai na daga Masa cike da kunya, muryarsa me dadi naji yace Ina so ne, me zaka yi dashi?Bai bani amsa ba da Alama ko sanda Yana da Ify magana wahala take Masa.

Ba tare da na bashi izni ba ya Shiga shafa su Yana laguda su,hankalina ya tashi sai Kara kankameshi da na yi, tunawa nayi da American film din da muke gani a dakin Ya Salman Ana kiss nace Bari na gwada.

Lips Dina na daura saman nasa a hankali na Shiga kissing dinsa yanda Naga dama ban ma San Ina wani abun ba hankali na ya gushe da abubuwan da yake min, mun Dade muna tabe tabe Wanda shi ya manta sauran ba wani zafafawa yayi ba,Ni Kuma ban iya ba sannan ga kunyarsa na kasa sakin jiki, sai da ya gaji Dan kansa ya hakura.

5pm Hajiyarmu ta Aiko min matar kaninta ta haihu tunda Ina fita naje suna gidan,tare da Mijin nawa muka shirya na rufe gidan muka fito tare muna tafiya a nutse duk munyi kiba da kyau,

muna tafiya Ana kallonmu masu gulma Ana fama, a kofar gidan da ake Sunan nace ya jirani na fito da kyar ya yarda sai tsoron mutane yake ji,Dama a garin ma sun Saba duk inda suka ga Dan Bature to Ina Nan a kusa.

Masu tururuwar zuwa suna suna ta kallon me kyau Mijina,ganin na Dade ban fito ba ya ya matsu na dawo sabo da Dani ya Saba kawai ya shige gidan sunan abinsa,Wanda mutane ke tsakar gida a zaune sai ganin Bature sukayi ya shigo abinsa Yana duba Ni ko ina Mata ne Amma ba ruwansa dubani yakeyi cikin Mata,wasu suna dariya wasu Kuma kyansa tsoratasu yayi ma, wasu matan suka Shiga kwala min Kira Fadila fito ga jelarki yazo,masu Jin haushina suna yi, ko a jikina na fito daga dakin me jego ai Yana ganina ya tako cikin takunsa na gadara da birgewa fuska ba Rahma ya ja Hannuna a gaban mutane ya rungume Ni ,Mata suka kaure da Salati, wata cikinsu tace Shege mahaukaci Ashe shima yasan harka.
Harara na watsa musu tare da Jan hannunsa muka yi tafiyarmu gida.

Wasa Wasa sai gashi mun kwashe kusan wata biyu tare da Dan Baturena sosai yanzu yake addini ya iya komai tare da sauran abubuwan rayuwa ya koya,kasancewar ba inda yake zuwa Nima Haka muna zaune abinmu muci mu koshi sannan muyi romancing dinmu duk da ba wani kwarewa mukayi ba Haka Muke jagwalgwale junanmu muji dadinmu mun Gama sabawa da juna ga shakuwar da mukayi,kusan yanzu idan muna making love kasa control din kansa yakeyi da Alama xxx yake bukata,sannan mararsa na mugun Masa ciwo.
Gidan wata kawata naje wacce ta Dade da yin aure na sameta na fada Mata matsalar Mijina tace sex yake so ki daure ki bashi hakkinsa ne ke Zaki nuna Masa hanya tunda kwakwalwarsa baza ta iya tunanowa ba,nace ance da zafi fa? Ta zauna ta zugani sosai tace ba zafi sai ma dadi.

Ya Salman ya sake biya min kudin jarabawar waec da Neco zanyi November December a garin Gombe cikin birni, kullum idan zanje exam din Ya Mahmood ko ya Salman ke bani kudin tafiya dake ba wani Nisa bane tare nake tafiya da Dan Bature ya jirani a waje idan mun Gama mu dawo gida tare, kullum haka har muka Gama Zana waec muka fara Neco itama na Gama,lokacin munfi wata uku tare da Dan Bature,abinci ma ko yaushe duk da Bai Kare ba Ya Salman tunda suka samu aikin Teaching Yana siyo Mana kayan abinci iri iri,Dan kudin kashewa Ya Musa Yana bani bamu da matsala shi yasa kullum kyau muke karawa.

Yau kwanan mu biyu da Gama Neco Dan Bature ba Ify Yana ta ciwon Mara na Sha'awa kamar zai mutu,Munje chemist an bada Magunguna Amma a banza Haka na dauki shawarar kawata yau da dare munyi Shirin bacci da kyar ya lallaba na Masa wanka na shiryashi  Zan sa Masa Riga yace baya so na barshi da Boxers dinsa kawai.

Hajiya Babba taki kwanciya kwana da kwanaki a Haka take a mike,tausayi yake bani Haka na daure na cije na yakice kunya ta na fara romancing dinsa Haka dai ba wani kwarewa nayi ba Amma ya haukace min Baki daya ya Gaza hakura da kansa ya rabani da suturar jikina.

AsmaBaffa
[8/15, 11:43 AM] +234 813 228 4370: 🏕HADIN KAI🏕

3

Official

By
AsmaBaffa

MARCYCOOL, FLOWER,AUTA,ASYCOOL and JANNAT TA SALIM page dinku ne fa.ku kwashe min da tafi😆.

Muna tafiya dashi wani munafukin ya ganmu da sauri ya Kira Abbu a waya ya sanar Masa ga Fadila can sun tafi yawo cikin daji da Mahaukaci,ba tare da na sani ba sai ga Ya Musa tare da Ya Salman a fusace, ya Salman bai jira komai ba ya kifa min Mari har biyu,Dan Bature a hasale ya shaki wuyan ya Salman tare da yarfa Masa Mari sai da jini ya fito ta Hancin Ya Salman,Kuka na fara ya Musa da Ya Salman suka hada karfi da karfe suka fara dukan Dan Bature sosai,Gefen kansa ya fashe jini ya fara tsartuwa,Ni Kuma Ina kuka na Kare Dan Bature Ya Musa ya kawo Naushi ya sameni a Hanci Nan take Hanci na ya fashe jini na fita,Dan Bature Yana ganin haka ya Kara haukacewa ya mike ya Shaki Ya Musa da Salman ya gwara kansu,wani Naushi da yayiwa Ya Musa sai da ya zube har kasa,mutane dake kusa suka fara kawo dauki sabo da Dan Bature yayiwa Ya Salman jina jina Haka ya Musa ma tuni yaci dukan kawo wuka,Mutane da yawa suka taru tare da rirrike Dan Bature dake Huci kamar Zaki,Wata girgiza yayi gaba daya ya watsar da mutanen da suka rikeshi sannan ya Fadi a kasa shi kadai ya fara jijjiga kamar me fyarfyadiya sai dai wannan har wani gurnani ya yakeyi ya dafe kansa,Gigicewa nayi Ina uban kuka Ni Sam Bata su Ya Salman nakeyi ba hankalina Yana wajen Dan Bature,Addua na Shiga tofa Masa tun Yana yi da karfi har ya dawo yi a hankali sannan jikinsa ya saki yayi luf a kasa kwance Nan da Nan bacci ya kwashe shi, lokacin na cire gyalena na daure Masa kansa da Gyalena inda jini ke zuba.

A matukar fusace Salman da Ya Musa suka mike jikinsu duk jini suka fara cin ubana,Bulala suka Sa suka zaneni tas sannan Musa ya sabani a kafada suka tafi Dani giga,Ni Kuma kuka kawai nake Ina kallon Dan Bature cikin jini ya Dan bude idonsa da kyar Jin muryata Ina kuka Ina kiransa Dan Bature Ina Miko Masa hannu,Ya Salman ya lankwashe Hannun da na Mika sai da yayi Kara,na tsandara ihu,Dan Bature Yana yashe a kasa abin tausayi ya bude idonsa Yana

kallona bazai iya tashi ba,shima daga kwance ya Miko min hannu,karfin kukana na Kara.

Muna zuwa gida Abbu yau Bai dakeni ba, meeting din gaggawa ya hada tare da iyayensa,Iyayen Hajiyarmu da kannensa sai Kuma Yan gidan namu kaf yaro da Babba, a tsakiya suka sani Ina Hawaye.

Abbu cikin sanyin murya yace Fadila nace Naam Ina kuka,yace na biki ta lallami na biki ta lumana,na fada Miki a tsaye na fada Miki a zaune,sannan jikinki ya Gaya miki, yanzu gashi Ina fada Miki da sanyi karki kuskura na fada Miki da zafi wannan bazai Miki kyau ba,me na rage ki dashi? Kinki aure yanzu Kuma kina bin Mahaukaci,Yar iska kike nema ki dawo? Kai na girgiza alamar A'a, yace to bakya kaunarmu mu iyayenki da Yan uwanki kike aikata haka Dan ki zubar Mana da mutunci? Kai na girgiza, yace dubi Yan uwanki na jini yanda Dan iskan Mahaukacin da kike bi ya aikata musu yanzu dadi kike ji kenan? A hankali nace a'a Amma ai su suka jama kansu tunda sune suka tsokaneshi,Duka Hajiyarmu ta kai min Ana magana bakya ji ko, Abbu yace ai ke ta gado halinki tayo Hadiza munafukar banza ai ke kike zugata,Wai an tabo Fada Nan Hajiyarmu tace yanzu dai da tayi abin Tsiya sai ace iyaye Mata ke zuga yaro,Amma sanda yaro yayi abin kirki baza a taba godewa uwa ba ace anyi tarbiya me kyau sai marar kyau sannan miji zai dinga ganin laifin mace, Yafendo tace ke rufe mana Baki yo ke har wani halin kirki ne da ke,Anty da ke gefe tace badan Allah yasa an aure Ni ba ai da abinda yaran Hadiza zasu yi sai yafi Haka,nice nake sasu a hanyar kirki.

Abbu yace na sani Sarai Allah Miki Albarka Antyn Yara,Hajiyarmu zatayi magana Ya Salman ya Mata alama da ta kyalesu,Yafendo ce tace to Fadila tunda tsiya kike ji muma mun shiryeki aurenki saura sati biyu da Talle Mai lemo,Abbu yace Kuma wlh kika gudu daga garin Nan ban yafe Miki ba na cireki a yarana.
Ihu na Shiga tsalawa Yafendo tace kyayi Kya Gama Nan kowa dake wajen suka rufeni da fada kowa Yana tofa albarkacin Bakinsa, sai da suka Gama nace Wlh na daina hakuri daga yau na Zama marar hakuri da mutunci,tunda Haka ne tantiriya zan koma,Kuma matukar aka bani Talle sai na zuba Masa shinkafar bera.
Baki Kawu Salisu ya tabe yace munga irinku kun fi Dubu sai anyi aure ajiku luf.
Mikewa nayi na fita abina ba tare da an bani izinin tafiya ba.

Yau kwana nayi Ina kuka karshe dabara ta Fado min,na koma wajen Abbu Bayan na gaisheshi nace Abbu Dan Allah to Ni dai daka aura min Talle gwara ka aura min Dan Bature ko a daji zamu na kwana zan zauna,Salati Abbu ya saki kana ya fashe da kuka,Ya Salman suka afka dakin Abbu da gudu sun zata wani gagari min abune ya faru da har Abbu ya fashe da kuka Haka har tsakar gida Ana jinsa.

Musa yace Abbu Ify?, Abbu ya Kara fashewa da Kuka Yana nuna Ni da yatsa kamar yaron yaye ban San sanda na kwashe da dariya ba nace Wai Dan nace ya aura min Dan Bature Abbu Ashe Saurin kuka ne da Kai? Ya Salman ne ya Kore Ni shima Yana kunshe dariyarsa.

Gaba daya na canja halina na hakuri da kawaici tunda aka ce zan auri Talle me lemo,yau

shiryawa nayi fes nayiwa Hajiyarmu sallama nayi karya nace zanje gaida dangi, harda murna tana sa min albarka, ban tsaya ko Ina ba sai rumfar Talle me lemo,ga lemo ya kasa harda kankana,Talle tunda ya ganni yake faman washe jajayan hakoransa, Ina zuwa da gadara cike da Isa nace Dattijo fere ka yankamin na dari biyar,Talle ya washe Baki yace ai Amarya kyauta za a baki, jiki na rawa yace wannan kwalliyar tawa ce? Kaina na dauke nace ta hadadden saurayina ce,Kai nifa dana maka kwalliya gwara nayiwa Mahaukacin Kare,Baki bude Talle ya kalleni kawai sannan ya yanka min lemo da yawa,nace kankanar fa ko a banza zaka aureni,Nan ma na zabi katuwa nace yanka ta,yamin yanda nake so Yana wani washe Baki na dauki ledojin nayi tafiyata.

Na Shiga gida kowa Yana sa rai zasu Sha lemo da kankana sai suka ga na wuce na dauko Sallayata katuwa Ina budawa da gadara tunda yanzu na canja halina tunda akace za ayi min auren Dole,ficewa nayi daga gidan da kayana,inda nasan zanga Dan Bature naje,Allah sarki na ganshi futu futu duk yayi dirty ya rame sabo da yunwa yau kwana hudu kenan bamu hadu ba,ji nake kamar na Shekara wani dadi nake ji Dana ganshi,tunda ya Hangoni ya mike tsaye da sauri Yana Murmushi Wanda shima na farin ciki ne, wani azabar kyau yayi ga kwarjini.

Duk da Dirty da yayi bana kyankyaminsa na Shimfida Mana Sallaya tare na zauna sannan na nuna Masa shima ya zauna tun kafin na bude ledar ya fisge ya bude,Amma bazai iya Sha da kansa ba sai dai ya dinga damalmalawa ta baci,da kaina na Shiga bashi Yana Shan kankanar, har Hannuna yake rikewa ya zuke har cizona yakeyi sabo da sauri, idan muka hada Ido Ina ta murna Ina Murmushi burina ya cika Yana cin abin da na kawo,idan muka hada Ido indai yaga Ina dariya sai shima yayi Murmushi Yana min wani kallo me zautar da hankalin duk Wanda ya kalla,ga wani kwarjini,kyau,sura da cikar zati.

Yasha fruits din da yawan gaske musamman kankanar na zuba Masa ruwa ya wanke hannunsa Amma ya kasa wanke hannayen Haka na kwara musu ruwa ya janye hannayensa da sauri ya boye abinsa,faratansa nagani Sunyi zako zako,wani yaron Almajiri dake kiwon shanu a Bayan gari na aika shago nace sauri ka siyo min Reza, Bai dauki lokaci ba ya kawo min Reza, hannu na Mika zan jawo hannunsa Amma yaki yarda sai ma bar min wajen da yayi tare da shigewa cikin Dajin abinsa.

Gida na tafi Ina sauri sabo da na Dade.

Ina sauri sabo da gaskiya na Dade,ina komawa gida Hajiyarmu tasa Salman da Musa suka zaneni Nasha kuka Amma kamar me kunnen Kashi washe gari ma saida na saci jiki naje wajen Dan Bature.

Ranar Kuma Abbu yace ya haramta min fita ko kofar gida,Amma kwana uku na karya dokar sabo da yanda tunanin Dan Bature ya addabeni bani da sukuni Sam tunanina tausayinsa nake ji kawai.

Abbu tunda ya samu labarin yau na karya dokar na fita ya samu Yara majiya karfi mahaukatan fulanin daji suka kamo Dan Bature har kofar gidanmu na fito Ina kuka Ina bada hakuri me ya Muku Dan Allah kuyi hakuri karku taba lafiyarsa,Abbu indai zuwa wajensa ne wlh na hakura bazan sake ba Dan Allah karku yi Masa komai zaku dauki zunubi,a gabana Abbu

yasa kartan Nan suka fara jibgar Dan Bature da makami,suka Masa jina jina sannan suka jashi can gefen titi suka yasar dashi Ina ta uban kuka na fito da gudu zan bishi Abbu yasa Musa suka rikeni suka maidani gida,yau nayi kukan da ban taba yi ba a duniya duk me Imani sai ya tausayawa bawan Allah Nan.

Abbu yasa na daina fita ta Dole Haka Dan Bature ya karaci jinyarsa ya warke duk ya Kara lalacewa ya rame,ga dirty Yana cikinsa farcen Nan zako zako Suma ta Kara taruwa.
Yau ya rage saura kwana daya a daura min Aure da Talle,kasa jure bacin Raina nayi na saci jiki na tafi Office din Yan Hisba dake kauyen na Kai Karar Abbu za ayi min auren Dole.

Nan danan Yan Hisba suka min Nasiha sannan suka je har wajen Abbu suka kwatar min yanci na,suka yiwa Abbu nasiha sosai,Abbu yace naji na hakura Amma bazan daga ranar daurin aure ba ta kawo min Wanda take so yau.
Ba tare da tunanin komai ba nace na Amince, da yamma na fito neman Dan Bature can kusa da wata bola na hangoshi Yana kwance a tsakiyar Rana,sai karkarwar sanyi yake yi da Alama zazzabi ne ya kamashi,tausayinsa ya kamani jikinsa duk raunikan da Su Ya Musa suka dake shi.

Chemist naje na taho da me chemist din ya ganshi ya bani Magunguna yace a bashi,nace nawa? Me Chemist yace kyauta na bashi idan Bai warke ba ki dawo a canja wasu.

Da kyar a cokali na jika maganin ya narke Ishu me chemist ya tallafa min na bashi maganin da kyar ya Sha.
Haka Ishu ya Kira min wasu maza suka dauki Dan Bature aka kaishi inuwa Nan bacci ya kwashe shi,a wajen na yini Nima sai da yaci baccinsa ya koshi sannan ya farka da sauki Don maganin yayi Masa aiki,Abinci na naje gida na dakko taliya da miyar kifi na siyo ruwa na zauna na bashi da kaina Yara an taru Ana ta kallonmu, saida na tabbatar ya koshi sannan na sake bashi maganinsa lokacin Ishu me chemist yazo duba shi, na mike zan tafi gida naji ya rike min hannu, juyowa nayi Ina kallonsa nace me zanyi maka? Ina Masa Maganar kurame, Hawaye ne Naga ya zubo Masa sharrr....Ishu yace subhanallah wannan wlh duk yanda akayi haukar tasa me Tsafta ce,ba shahararriya bace Amma Mahaukaci shahararre ba Haka yake ba Sam, Allah Baki ladanki Fadila tabbas kina kokari Kuma sai Allah ya Baki Lada.

Komawa nayi na zauna kusa dashi na Shiga lallashinsa cikin sanyin muryata nace kayi hakuri anjima zan dawo kaga Abbu na zai dukeni, ya sunanka? Kallona yayi baice komai ba,nace ur name pls, kansa ya dafe ya Lula tunani da sauri ya zabura ya tuna kenan yace Aliyu Hydar,Murmushi na saki nace nice name, na Dade ina lallabashi sannan na mike na tafi ba tare da ya rikeni ba sai Murmushi da yayi min kadan.

Misalin Karfe 10 na dare Hadari ne ya Hado sosai,ba abinda ya dameni irin tunanin Dan Bature gashi bashi da Ify idan ruwa ya zaneshi shike nan Kuma.
Zumbur na mike na lallaba ba tare da kowa ya sani ba na bude gidanmu na fita da gudu naje inda na Saba ganinsa, hannunsa na jawo da sauri muka tafi gidanmu dashi,ina ta jansa,tsorona

idan na barshi a zaure za a ganshi ayi Masa wani abun kawai na kaishi dakina na nuna Masa bed dina nace kwanta yaki kwanciya,nayi nayi Amma yaki kwanciya sai ya koma kasan ledar dakina ya kwanta,Bargo na lulluba Masa ya cire tare da jefarwa Yana Bata fuska.

Kofar na kulle Masa sannan na koma dakin Hajiyarmu nace Tsoron tsawa da walkiya nakeyi yau a Nan zan kwana,Hajiyarmu tace Kya karaci gulmarki gulmawuya.

da Sassafe na farka kafin nayi sallah na budewa Dan Bature kofa Wanda dama ya gaji da Zama a dakin Ina budewa ya fice daga gidanmu da sauri,Abbu Yana kofar gida lokacin sai ganin Dan Bature yayi ya fito daga gidansa.

Abbu yace Kai Kai.....Amma ko kallonsa baiyi ba yayi gaba abinsa, da sauri Abbu ya dawo gida kafin nayi magana ya rufeni da duka tako ina,.

Yau zan daura Miki aure Dan ubanki tunda Baki da mutunci Haka ya fice a fusace ya sanarwa Talle da danginsa,nan danan aka taru a kofar gidanmu,gashi yace idan na bar gari Bai yafe ba bare na gudu.

Office din Yan Hisba na koma Ina kuka nace Abbu baiji nasiharku ba,Haka muka taho da Yan Hisba filin daurin aure an cika makil.

Dan Hisba ya fara waazi da Nasiha,Abbu yace nace yanzu ta kawo Wanda take so idan Bata kawo ba to wlh na daura da Talle,Talle ya washe Baki yace Bata da wani sai Ni a daura kawai, Ina Hawaye nace Ni Dan Bature nake so.

Abbu yace to kunji Mahaukaci take so,Dan Hisba yace a kawo Mana shi muji idan yasan sunansa sai a daura dashi tunda tace ita so take ta taimaka Masa ta ceto shi daga halin da yake ciki,,Nan mutane suka tafi neman Dan Bature suka ganshi a zaune kamar me hankali, mutanen kauyen har Yan hisban ba wani ilmin addini garesu ba, sukayi juyin duniya ya tashi bare ya bisu sai da nazo wajen da kaina sannan ya bini,nace ka fada min sunanka Dan Allah kayi magana sunanka za a daura Mana aure yanda zan kula dakai daga halin da kake ciki,wannan itace damar da zan iya yi maka komai,zan aureka ba Wai Dan Ina sonka ba,don kawai na taimaka maka,ka duba irin wahalar Dana ke Sha a kanka.

Sai da na Dade ina Masa maganganu nayi Masa Zancen kurame ya fada min sunansa,da kyar kamar me koyon magana yace Aliyu Hydar.

Mutane suna kallon ikon Allah Dan na birge mutane da dama,su Ya Salman duk suna wajen,Mahmood yaji tausayin bawan Allah yace na biya Masa sadaki,aka dauki kabbara Banda Abbu da Yan gidanmu babu Wanda yake murna,Hajiyarmu kuwa tana can tana ta kukan bakin ciki, Me gari yace Nima na bashi karamin Gidana na kusa da bakin titi Dana Gina kwana Nan, Allah yasa ban zuba Yan haya ba,na Basu aro su zauna har lokacin da Allah zaiyi ikonsa ya warke.nan ma aka Kara kabbara,Wani Alhaji me kudi shima yace zan Mata kayan daki,Abbu ya tabe Baki.

Kawu Salisu da Kawu Usman suka ce a matsayin mu na iyayen Amarya zamuyi Mata lefe,sannan zamu dinkawa mahaukacin nata Kaya kala goma da takalma kala uku.

Wani cikin dattijai yace zan zuba Musu kayan abinci dai dai gwargwado.
Farin ciki ya kamani Lallai Dan Bature Yana da kashin arziki.

Nan take aka Kara tambayar Dan Bature Sunan mahaifinsa yaki yin magana Dole aka Kara Nemo ni da kyar ya Kara lulawa tunani yace Sulaiman Saleh,nace Aliyu Sulaiman? Yayi banza Dani ya koma can jikin bishiya yayi kwanciyarsa bacci ya kwasheshi,Nan Kuma na fada musu me yace Nan take aka daura min Aure Aliyu Sulaiman da Fadila Tahir kan sadaki Dubu ashirin Mahmood ya biya cash, Ana daura aure Ina dakina Ina kuka yanda duk Yan uwana da iyayena suka tsaneni.

Hajiyarmu da Yan uwanta tare da Kakanninmu sai fada suke min Ina ta kuka,Anty ma tazo ta dinga habaici,Ya Musa zagi ba Wanda ban Sha ba,Ya Salman da Mahmood ne kadai suka dinga min Nasiha tare da lallashina,Abbu kuwa yace duk abinda ya faru ko ya biyo baya Kar na sake na doso gidansa,bazai min Baki ba Amma ko me ya sameni nayi kuka da kaina.
Hajiyarmu tana Hawaye tace yanzu Fadila kin zabi Zama da Mahaukaci? Yanzu kika yarda aka daura muku aure? Idan ya warke yaki kulaki fa? Idan ya warke kika ji ba sunansa Aliyu ba fa? Baki sani ba ko Arne ne kawai ki Kai mahaifinki Kara har wajen yan Hisba akan Namiji Mahaukaci da ba a San asalinsa ba.

Ni kaina sai da na tabbatar da Hajiyarmu gaskiya ta fada nace ba komai Allah na Bayan me gaskiya Hajiya kuyi min addua Ni Dan na taimaka Masa na aureshi,Bayan Haka ma ai kun tsaneni kowa ya tsaneni akan Allah Bai bani Mijin aure ba,gashi na Samu ai sai kuyi murna.

Fadila Babu iyayen da zasu tsani dansu sanin darajar aure yasa muka matsu kiyi cewar Hajiyarmu,nace yanzu ba da kuka ga na auri Mahaukaci Amma da wacce tsana ce ba a nuna min,mene ba ayi mini ba sai yanzu Dana auri Mahaukaci koma mene kune kuka ja min kowa Yana zagina Taya bazan auri ko waye ba na Kara rushewa da kuka me tsuma zuciya.

Haka muka yini Ana ta gulmata a garinmu,Anty ganin ba mutumin kirki na aura ba Mahaukaci ne yasa ta zage da ita aka yi min jeren kayan daki a sabon gidan da aka bamu na wucin gadi,2 bedroom sai Palo da bayi,ko Ina shafe sumul da siminti ginin bulon siminti,gidan Dan dagwas dashi harda fentinsa Shar milk color,mutumin da yayi alkawari shi ya min kayan daki sosai Palo sunsha kujeru da labule sai Gado a bedroom biyu sai mirror da Sip dai dai rufin asiri,kayan kitchen Yan kadan akayi min da resho na,Kawu Usman ya Kai kerosine paster guda,aka zuba min kayan abinci sosai a matsayin garata,da Kuma na ddattijon da ya bamu sadaka, Bayan sati biyu kamar yanda Kawu Salisu yace an min lefe katuwar akwati daya kayan duk birni aka kaimin dinkin,Takalma kala uku da jaka kala biyu Sai kayan kwalliya,da slifas na tsakar gida,shima ango sun dauki size nasa an gwadashi sun Masa dinki kala goma da takalma kala biyu Sai slifas.

Ranar Saturday Abbu ya Tara kowa a dakinsa yace yau za a Kai Fadila dakin mijinta ta zauna da mahaukacinta,Kuma bazan taba ci da su ba idan abincinsu ya kare,Mahaukaci ya Nemo Mata,sannan duk abinda ya faru Kar na ganki a kofar Gidana sai da zuwa gaisar da

dangi.
Alhmdllh mun fita hakkinki mun Miki komai Wanda ya cancanta iyaye suyiwa yarsu sai kuje ku karata aci soyayya Ify.

Kuka nakeyi sosai Ina Dan Allah Abbu kayi hakuri wlh Nima bada so na na bijire muku ba, Allah ne ya kaddara,Ya Salman yace karki damu Fadila kawai muyi Addua Allah ya bashi Ify,Allah yasa idan ya warke ya tuna dake kema ya Miki halacci.

Ina kuka haka naci wanka da kwalliya sosai tare da kawayena Yan uwana Kuma sai Anty da kakannina da Matan su Kawu aka tafi rakani dakin Mijina Ana guda Ana ayyiri da gayya suke yi suna dariya Ana gulmata,kicibus sai ga Dan Bature dukun dukun dashi yasha dirty, Bai San me akeyi ba tunaninsa ma yawo muka fito,duk da kaina a lillube yake sai da ya ganeni kawai ya shige cikin ayarin Yan Kai Amarya aka jera tare dashi gashi yamma ce lis maza duk sun fito Majalisa duk inda muka wuce Ana ta sheka uban dariya.

Suma masu Kai Amaryar Haka kamar ciki zai ciwo,ganin Haka sai ya firgita yayi sauri ya dawo kusa Dani tare da rike min hannu,kunya ta kamani Ana ta dariya da ihu,Haka aka Kai Amarya duk inda nasa kafata shima Haka zai sa, Ana kaini Yan Kai Amarya suka watse kowa yayi gida ana uban sheka dariya.

Ganin ba kowa na mike naje na rufe gidan,abin farin ciki harda rijiya a gidan,ba Bata lokaci na fara kokarin cire Masa Riga zan fara duty na gyarashi dama sabo da Haka na aureshi,kokawa muka farayi dashi ina dariya sai na cire shi Kuma ya hade Rai,da kyar na cire masa,ya cire wandonsa daga shi sai Boxers kunya ta rufeni a tsorace na jashi zuwa toilet dama duk na siyo su shaver ta,dama Kuma Ya Salman ya kaishi wajen aski anyi masa gyaran fuska an rage Masa gashin kansa.

Hannayensa na dage da kyar ya tsaya na asked Masa armft dinsa tas, shaver din Hannuna ya karba sai Naga ya tsaya ya Lula tunani sosai tare da dafe kansa, sai naji yace ah oh...sai ya fara kokarin cire boxers dinsa da sauri na bar Masa toilet din,Ashe tunawa yayi yanda ake askin sai ya aske gabansa tas,sannan da kansa yayi wanka,yanda Haukar tasa ke da Tsafta duk ya iya har su tsarki haukar tasa ba me yawa bace.

Bayan ya fito na leko sai na ganshi tsirara ya fito,tsoro ya kamani na fito ba tare Dana kalleshi ba na daura Masa towel Dina fari Wanda shima Ya Musa ne ya siyo min a Kano.

Bedroom na jashi na zaunar dashi, sai Naga kamar Bai fita ba,ruwa na Kara jawowa a rijiyar na haska Torchlight na Kara wanke toilet din fes sannan na zuba wani na sa masa wani karamin boxers da aka kawo dasu cikin kayansa,na jashi toilet na dinga darzar jikinsa da sabulu me kamshi sai gashi yayi wani kyau da haske, wandon ya cire da kansa Wai na wanke Nan ma, Haka Ni dai na rufe idona tunawa da nayi Mijina ne yanzu na wanke lungu da sako fes sannan na daura Masa towel muka koma daki.
Na shafeshi da Mai Vaseline sannan na sa Masa wani yard marar nauyi na zaunar dashi na

fesa Masa turar.

A dakin na barshi na tafi Nima nayi wankana na dawo na shirya Ina Jin kunyarsa,sai kallona yakeyi duk abinda nayi sai ya tafi tunani me zurfi sai ya jinjina Kai.
budurwar ya Musa ta soya min kaji biyu daban tayi min Miya lafiyayya, Anty Kuma ta dafa min shinkafa ta yanka salat a Daren da za a kawo Amarya aka kawo dasu Wai naci da dare kafin gobe harda pure water Leda biyar Hajiyarmu ta Aiko dashi aka ajiye a kitchen.

Abincin na zuba Mana da ruwa a gefe ban ce ya sakko ba Yana ganin abinci ya sakko ya zauna yana kallona maana na bashi yaci yunwa yake ji,Ina ci Ina bashi a Baki Yana ci,sai yayi Shuru dashi abin tausayi bawa ya koma kamar jariri

AsmaBaffa
Love u fans.
[8/15, 11:44 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

5-10

Official

By
AsmaBaffa

JINDADI SABO FANS THS PAGE IS FOR U FANS.

Daurewa nayi da kaina na nuna Masa hanyar na sashi a hanya wani dogon tunani ya tafi Yana tunawa ba a hankali ba kawai ya shigeni, azaba har kwakwalwata haka naji,na kwala kuka Ina ihu na rushe da kuka Amma kawai harkarsa yakeyi Yana wasu kalar kukan dadi na daban, sai da ya Dade Yana abinda yaga dama Dani har ya samu nutsuwa yayi matukar gamsuwa,wata lafiya ta shigeshi da farin ciki, nasan Bai da hankali n da zai lallasheni Bayan ya zare jikinsa daga jikina,duk wannan abin da muke a kasa muke ba a saman bed ba har yau baya Hawa bed Nima ya koya min nafi so na kwanta a kasa yanzu. Tun Ina kuka har na gaji

nayi Shuru na mike da kyar,shi Kuma Yana kwance Yana huce gajiya, kallo na yayi kamar daga sama naji yace ya Naga kina tafiya haka?, Me ya sameki?takaici ya rufeni ko kulashi banyi ba naje na kunna resho na daura katuwar tukunya na tafasa ruwan zafi nasa gishiri na hada abina sabo da duk kawata ta fada min yanda zanyi.

Sai da na Shiga ruwan zafi yafi sau uku a katon bahona na roba,sai da naji salama wajen ya daina min zafi da radadi sai kadan sannan nayi wanka na tsarkake jikina nayi Alwala na dawo daki Ina tafiya kamar wata kaguwa.

Na hada maka ruwan zafin, wankan tsarki zakayi Wanda mukeyi din Nan kullum ka tuna? Na tambayeshi,Kai kawai ya daga min ya mike tare da daura towel yaje yayi wanka da sabulu sannan yayi na tsarki ya fito.

Lokacin na gyara dakin neat na fesa turaren kamshi wani yard ruwan Milo ya dauko ya Sa abinsa kamar zaije wani waje sai nishadi yakeyi ya koma kasa ya kwanta Nima na kwanta gefensa ya Kara rungumeni sai bacci ya kwashe mu.

Ranar bakin ciki a wajena,ranar da bazan manta da ita ba a rayuwata bamu farka ba sai da Rana ta fito ya fara farkawa a matukar gigice ganin mace kusa dashi a kwance,dakin da yake ciki ya kalla yace what....da karfi Wanda yayi sanadiyar farkawata a bacci,nace Ify Dan Baturena? Dake Haka nake ce Masa,wani yare naji Yana yi Wanda ban San wanne yare bane sai Kuma naji ya koma turanci, Who are u? Who the Hell are u?, ya shako wuyana ya fesa min mari,ga dakin mun kulle ko Ina duhu, sai Kuma naji yayi Hausa uban waye ke, wacce kazama ce ke da Zaki kwanta a jikina? Mum? Mum, where am i? Ya Kara shako Ni ya jijjigani da karfi a Ina nake Nan dakikiya?  wani tsoronsa ya kamani da Alama ya warke nace a Dingawa kake kauyen Gombe state Nigeria, Kuma Ni matarkace kafin na rufe Baki ya zuba min Mari matata kazamarki nonsense kin San ko Ni waye? Karuwan banza Ni Aliyu Hydar oh..God fuck u ya kalli kayan jikinsa ya kalli dakin baya ganewa sabo da duhu,,nace ciwon hauka kayi na aureka Dan na taimaka maka wlh Ina sonka,karka min Haka karka gujeni,ka tsaya na baka labari a Mahaukaci kazo garin Nan,da farko ba sonka nakeyi ba tausayinka Dan na taimakeka yasa na aure ka,Babu wahalar da ban Sha ba akanka har sonka ya kamani hannunsa na ruko....

Maruka ya Kara zuba min har uku ya Sa kafa yayi ball Dani na nayi taka taka na bigi jikin bed ji kake gwaf,kaina ya fashe ,jini ya zubo ta hancina gashi mun rufe ko Ina duhu kamar dare bana ganinsa baya ganin fuskata ko kadan ya bude kofa kamar zai jijjigeta ya fice da sauri Yana kiran Dad da Mum tare da wasu mutanensa Kuma sai wani yare yakeyi Wanda ban San na wanne kasa bane.

Koda ya fita ba Ba mutane a garin kasancewar yanzu gari ya waye wani me machine ya tambaya ya kaishi cikin garin Gombe city,ya kaishi kuwa Yana sauka ya tare wani a hanya tare da tambayarsa Dan Allah ya ara Masa waya ya bashi ya Kira Mum dinsa Yana wani irin yare Wanda kamar na kasar waje ne, Nan take 30mnt sai ga Motocin sojoji sun zo Dalla Dalla guda biyu da gudu suka bude Masa mota ya Shiga tare da kamewa a Bayan mota Nan ya mikawa

me machine dubu goma cash, me machine ya dinga ihu da tsalle abinda naira hamsin suke Kai mutane yau gashi da 10k, wannan motoci Basu tsaya ko Ina wani katafaren Hotel Yana ta masifa da turanci da Hausa ko yarensa,a hotel ya dinga wanka Yana darje jikinsa da Bakinsa yafi awa a toilet Yana kakale kakalensa dinsa ga masifa Yana ta yi da yarensa da Kuma turanci watarana Kuma yayi Hausa,Kaya na Alfarma kana Nan Kaya ya saka sun hadu kamar yanzu ya sauka daga London abin kallo ne ga waya har an siyo Masa iPhone tafkekiyar da sai wane da wane, takalminsa wow sai Wanda ya gani idan ba saninsa kayi ba baza ka gane Dan Bature ba sabo da ya gaji da haduwa, sai Airport ya shige jirgi sannan ya Kira Dad dinsa yace Dad London Zan wuce a duba Ify ta na huta sai na dawo Nigeria pls Dad,wata aljana ce ta sace ni can wani daji I'm 100% sured Aljanna ce Dad,Bayan sun Gama waya jirgi ya Lula sararin samaniya abinka da masu hannu da shuni kudi Kare magana idan da kudi yanzu zakayi komai a wuce wajen.

Fuskata ta kumbura sumtum,ga Baki ya fashe,ga hanci jini da kyar na lallaba na mike nayi wanka na Dan gyara kaina,Ina rusa kuka Hawaye ya gagara tsayawa,takaicina ba dukan ba kawai sonsa da ya rigada ya dagargaza min zuciya,bazan iya rayuwa Babu Dan Bature ba,gashi abin haushin sanda yake da hankalin Bai ga kalata ba Bai San fuskata ba bare ya ganeni watarana, sallah kawai nayi na kaiwa Allah kukana tare da karatun Qurani, Yini nayi Ina kuka a daki nayi tunanin komawa gida na tuna furuncin Abbu Kar na soma zuwa inda yake da matsala akan aurena.

Me machine kuwa tunda ya dawo ya baza labarin a kauye Yana fada Dan Bature ya warke ya bar garin Nan Ashe Hamshakin me kudine zance har yaje gidanmu,Ya Salman yazo ya buga min kofa.

Idona a kumbure jajir nazo na bude kofa da sauri tunanina Mijina na ne da sauri na bude cike da farin ciki baya laifi a wajena,Ni Akan Ya warke ya rabu Dani gwara ya zauna da cutar haukarsa mu dawwama tare ,Ina ganin Ya Salman ne na rushe da kuka tare da fadawa jikinsa, tausayina ya rufe shi tabbas abinda yaji a gari gaskiya ne, Kuma abinda ake gudu shi ya faru,cikin gidan ya Jani tare da zaunar Dani gefensa, ya rasa ma ta Ina zai fara,ina kuka na bashi labarin abinda ya faru kaf ya tausaya min,Ya Salman yace hope dai kwanciyar aure Bata hadaku ba, Ina Hawaye nace sau daya ne Yaya Kuma jiya ne a Daren da yayi bacci ya warke ya dawo hankalinsa.

Yaya Wlh Ina sonsa na Shiga uku ya zanyi da rayuwata wlh Ina sonsa Don Allah Yaya nasan kana Sona ka Nemo min shi idan ban ganshi ba mutuwa zanyi, kafafun Ya Salman na rike na dira gwiwoyina a kasa Ina gunjin kuka Ina rokonsa,Nasiha ya Shiga yi min Amma Sam bana jinta burina kawai Naga Danbature na ya dawo gareni,kafin kace me zance ya baza gari mutane suka dinga turuwar zuwa gidan da nake Ana min jaje wasu suna Allah ya Kara dama ai an fada Mata taki ji, wasu Kuma sun tausaya min ganin halin da nake ciki kamar mahaukaciya na koma.Anty Amarya da tazo shewa tayi tare da shekewa da dariya tace Rana dubu ta barawo Rana daya Tak tame Kaya,yarinyar har Kara kika Kai ubanki mahaifinki wajen Yan Hisba Akan ya zaba Miki miji ke so ya rufe Miki Ido,  yau wa gari ya waya? Shuru nayi ta Gama ta tafi tana dariya.

Hajiyarmu itama kuka take na tausayin yarta ga Abbu ya tabbatar Kar na doso gidansa shima yaji labari,Anty Amarya sai Murna take tana Kara yayatawa a gari, Haka Matan su Kawu Salisu da yaransu Mata Banda Mahmood sai gulmata sukeyi Ana Allah ya Kara.

Talle me lemo labarin na zuwa Masa ya raba lemonsa kaf kyauta sabo da murna Yana Allah Kara yanzu sai kuma Nan gaba a hakura a dawo a aureni Dole uwar naki.

Bayan kwana biyu Ni kadai nake kwana a gidan Ina Addua da kuka Ya Salman,Musa da Mahmood kullum a gidana suke yini anan muke cin abinci tare suna debe min kewa suna min Nasiha da tayani Addua,duk na rame nayi duhu kamar ba Ni ba.

Bani da aiki sai tunanin Mijina Wanda kullum kayan sawarsa da ya Bari nake Shimfidawa Ina kwanciya a Kai,Haka kuma na dinga gasa kaina har na warke sumul, Ya Salman da Whot card suke zuwa mu yini muna buga game suna ebe min kewa.

Yauma muna yin game din ban San sanda na koma tunanin Baturena ba yanda mukayi rayuwa tare nake matukar kaunarsa kuka na fara Wanda ban San na fara ba sai sheshekar kukana suka ji Wanda sun rigada sun Saba da hakan, Ya Mahmood yace Sister mene haka Kuma again? Katin Yana Hannuna na jikesu da Hawaye na daga kaina sama Ina kuka nace Ina sonsa ya zanyi Ina kaunarsa na Kara rushewa da kuka duk suka tsaya suna saurarena cike da tausayi sukayi jumgum jumgum.

Ya Mahmood ne ya katse shurun yace ya kamata kawai muje mu roki Abbu ta koma gaban Hajiyarmu sabo da zatafi samun nutsuwa,sannan tunda result dinta ya fito Kuma sunyi kyau sai mu kaita ko college ne tayi karatu ko ta rage tension.

A hankali Ina share hawayena nace bazan iya karatu ba a halin da nake ciki bazan iya komai ba face sallah da Addua Allah ya hadani da Mijina karku Bata kudinku.

To Amma ai Zaki koma gida kici gaba da Zama ko? Ae idan Abbu ya yarda ba.

Bayan kwana biyu Suka roki Abbu da kyar ya hakura na dawo gida shima saida manyan gari da su Kawu suka Sa Baki sannan ya yarda na tattaro kayana na kulle gidan mukaje har gidan me gari na bashi key mukayi Masa godiyar aron gida da ya bamu kyauta.

Bayan na dawo Gaban iyayena Babu abinda suka sassauta a gareni yanda suke min da Haka ma yanzu,ga tunanin Mijina,na rame na fige nayi duhu kamar ba Ni ba, Bayan na kwashe wata uku a gida jahilcin mutan kauye suka fara maganganu ya kamata na manta da auren dake kaina nayi aure Nan gaba dama ba a sani ba ko ba sunansa Aliyu ba kawai aka daura akayi Masa waliyai.

Bana fita ko Ina kullum Ina gida Ina kiyaye igiyoyin aurena na tabbatar sunansa Aliyu kenan tunda naji ya fada da kansa Bayan ya dawo hayyacinsa,kullum burina na zauna ko na kwanta nayi ta tunano rayuwata tare da mijina watarana nayi dariya watarana kuka, nayi tunanin

saduwata dashi daya Zan samu cikinsa da nayi murna Amma Ya Salman ya kaini har asibiti Babu ciki a tare dani banji dadi ba naso zanga Dana jinin abin kaunata Danbature.

Me machine da ya Kai Dan Bature Gombe city na Nemo na tambayeshi labarin abinda ya gani Aiko ya bani labari karshe yace naji da turaci ya ambaci a kaishi airport Kuma da Alama ba Dan kasar Nan bane Don yaren da yeke Babu shi a kasar Nan kalar fatarsa ma ta nuna, Hawaye ya ziraro min nasan ma har abada bazan sake ganinsa ba ya kamata na hakura Amma zuciyata ta kasa hakan kawai naci gaba da kaiwa rabbil kuwwati Wal jabarut kukana,na Kara kwashe a kalla 5mnths Amma na kasa hakura anyi fadan anyi nasihar an gaji an kyaleni Haka. Inda Allah ya taimakeni ya bar agogonsa na diamond me tsadar gaske da kyau,ga zoben azurfarsa me kyau,chain din sarka na Samu na zura ta cikin zoben ya Zama kamar sarka me zobe nasa a wuyana da ita nake kwana Ina tashi,Haka agogonsa duk da yayi min yawa Haka na daurashi a Hannuna ya zauna dadas yayi min Masifar kyau kowa sai ya kalli Hannuna.

Attine yar Uwar Hajiyarmu wacce ke Zama a kudu can bangaren Iyamurai itace tazo gida tare da yarta budurwa Safarau,sunzo gidanmu taga halin da nake ciki tace Hadiza me zai Hana na tafi da Fadila can kudu ta samu salama sannan zata samu aiki tana kula da kanta,yanzu Kinga Safarau a Company na arna take aiki tana goge goge da shara da kin bar Fadila sai na kaita aiki ko wani Company ko gida ko office din wasu tana Dan aiki suna biya da tsada musamman idan mutum ya iya aikin ga Tsafta.

Baki na tabe nace me zanyi a kudu Ina da aurena,Hajiyarmu tace to da surutun da mutanen garin Nan sukeyi ai gwara ki koma can ko banza ma huta da munafunci, Hajiyarmu ta shawarci Abbu,shi Kuma yace a dawo Ify Ni da zagin da take jawo min ai gwara ta tafi can tazo Mana da yawo,Anty ma tace da mun huta wlh.

Ya Salman na kaiwa Kara Amma Nasiha ya min gwara na tafi Amma na rike mutuncina da igiyar da take kaina,ya dinga min Nasiha Kar na bijirewa Hajiyarmu again kaucewa Umarnin iyaye Yana kawo matsala,ba a son Raina ba ranar da Attine zata tafi tare da yarta Safarau na shirya da akwatita katuwa na bisu munyi sallama da iyaye Yan uwa da abokan azirki,Ya Salman ba,Musa,Mahmood har Tasha suka rakamu tare da bani dubu ashirin cash,ba tare da na San wannan state zamuje a Nigeria ba.

Gani nake kamar Watarana Dan Bature zaizo nemana kauye har sallahu na Bari idan ya dawo Zan siyi waya acan Zan na Kiran gida mu gaisa idan ya dawo a sanar min.

Ban San birni ba sai da yawo a Shiga a fita bare kudu,Haka muka je Tasha naji tace Lagos Baki na hangame nace Lagos kuma Hawaye ya zubo min shike Nan Dan Bature bazai ganni ba har abada Ina zai ganni Ina gari kamar Lagos,Attine kuwa haushi nake bata sai masifa take min muka Shiga mota katuwa doguwa, ita ta biya kudin da komai muna tsakiyar arna karfe 4 na yamma motar mu ta hau titi.

Tafiya muke ba ji ba gani Safarau sai dariya take min yanda nake ta sheka bacci,ita Kuma wayarta tecno take dannawa tana chart,tasa earpiece a kunnenta kujerarmu kusa muke a jere Attine Kuma tana gabanmu tana sheka bacci,Safarau tace Fadila ungo sa kunne daya na sa

daya muyi kallon Nigerian film a wayata,kafada na make nace A'a ke nifa da nayi komai arayuwata Wanda ba addini ba gwara nayi tunanin Mijina yafiye min komai nishadi.

Attine ce ta zuba min rankwashi shashasha kina wahalar da kanki akan mutumin da ya rigada ya manta dake Bai sanki ba marar zuciya, Jin tace Danbature ya manta Dani wani kukan rashinsa ya taso min na fashe da kuka, Baki Safarau ta rike tace ke kuwa Fadila wanne balain kaddara ce ta afka Miki ta soyayya? Allah ya yaye Miki,kukana nakeyi har bacci ya sake kwasheni ban farka ba sai da mota ta tsaya za ayi sallah masu fitsari da siyen abinci ma suyi,sallah mukayi Attine ta siya Mana kaza da yogurt har gurasa,mota taci gaba da tafiya muna cin abincinmu har muka Gama.

Sai da gari ya waye 11am muka Isa Lagos lokacin Ana shara ruwan sama Amma Haka mutane ke harkokinsu abin ya bani mamaki sabanin mu Arewa idan Ana ruwa to ba me fitowa, Attine ba ruwanta ta tare Mana taxi Muka Shiga sai Unguwarsu ta talakawa Wanda Hausawa Yan ci rani da talakawan Hausawa da Kuma arna talakawa Yan bariki etc Nan muka nufa,wani gida me bene sama da kasa duk da cewa tsoho ne ya kwararrabe Amma dai Yan haya ne sama wasu yare ne Yoruba kasan Kuma na Attine ne ta kama haya.amma ciki yasha gyara.

Palo ne sai daki biyu da toilet sai kitchen ba laifi akwai rufin asiri na talaka, gidan muka gyara fes sannan Attine ta dafa Mana jallof din taliya da kifi muka koshi sannan muka kwanta baccin gajiya.

Sai yamma lis muka tashi wanka mukayi da sallah sannan muka daura abincin dare Ni da Safarau tuwon shinkafa miyar alaiyahu mukayi me dadin gaske ko Attine ta jinjina mana, Attine tana da kirki ba laifi ga son Dan uwa Bata so taga Dan uwanta cikin damuwa, Haka take koya min aiki da kayan Yan gayu sabo da Kar naje aiki gidan masu kudi na kasa komai,har girke girke na Yan gayu take koya min,waya tecno Yar dubu ashirin da biyar ta siya min Nan Safarau ta dage wurin koya min yanda ake Amfani da har browsing yanda ko girki Zan iya koyar Abubuwa ta YouTube etc, tace Bari na bude Miki Facebook da WhatsApp Kya dinga rage tunanin da kike na masifa,Baki na tabe nace tunda dai kin koya min Google da YouTube ya Isa bana fatan muamula da kowa idan ba Mijina Zan gani ba,Dariya Safarau tayi tace to Allah ya shiryeki nace Ameen.

Satina uku a Lagos nayi kyau da kiba hasken fatata ya dawo har nafi sanda nake kauye haduwa lokacin da Dan Bature Yana Nan,Attine sai Jin dadi takeyi tana fadawa Hajiyarmu kasancewar kusan kullum Attine sai ta Sa min katin waya nayi waya da Yan gidanmu.

Ni kaina Ina Jin dadin zama.watana daya Safarau ta koma can Company inda take aiki a wani reception Ana biyanta.

Attine kuwa Yar kasuwa ce tana Saro irin su Maggi,Omo,katin waya etc tana siyarwa sannan itama tana aikin kula da wata dattijuwa Igbo wacce danta Hamshakin me kudi Ne,kullum Ni kadai ce a gida,yan kudu ba Zama Mata da maza neman kudi,Ni nake aikin gida sannan na dafa abinda nake so,Lallai cimar mu danan da kudu ba daya ba,su Dole sai anci dadi iya talaucin mutum sai yaci Mai kyau Lallai Dole sufi mu girma da komai.

Attine ce ta dawo nayi Mata sannu da zuwa,da Murmushi ta amsa min tace kina Nan ke daya ko sai tunani,a hankali nace ai na rage Auntynmu,da dai yafi sauki ki taimakawa kanki,me kika dafa Mana? Pounded yam with egusi soup,to Bari naci na huta sai mu fita yawon zaga gari kema kina ganin duniya,dake Attine kyakyawace itama Yar gayu ta waye sosai,dama na fada duk danginmu kyawawane masu hasken fata.

Hmm da kin bar fitar Nan Antynmu komai baya gaba na Ni dama Danbature na Zan gani,fada Attine ta fara min ke Baki da hankali Naga Alama so kike ki kashe kanki akan wani banza Wanda Bai sanki bama yanzu, Idan Attine tace Danbature ya manta Ni Bai sanni ba shine ke matukar daga min hankali kamar Ana zuba min garwashi a zuciyata,kukan tausayin kaina na shigayi sosai har sai da ta tausaya min ta lallasheni,tace Fadila kiyi hakuri kamar yanda kike da addini ga sallah da yawan adduoi ina so ki fawwalawa Allah lamarin kici gaba da Addua sai kiga Allah ya kawo Miki canjinsa ko ya hada ki dashi again ba abinda yafi karfin Allah.

Sai kikaga ya dawo ya daukeki,inye ya kaga Fadila ga Dan baturenta ku santalo yaranku kyawawa,ban sanda na fashe da dariya ba tare da share hawayena na Kara gyara zama, nace Auntynmu sai fa kiga ya dawo ko watarana? Attine a ranta tana mamakina tace kwarai ma kuwa,nace Alhmdllh Antynmu ya kamata ki Nemo min wurin aiki na fara zuwa sabo da nayi sauri na Tara kudin da Zan gyara kaina sannan da yanda Zan kashewa kaina kudi kafin Danbature na ya dawo Kar ya dawo ya iske banci gaba ba banyi kyau ba,Dariya Attine tayi tana ganin shirmena zalla.

A fili tace inshallah kin kusa tafiya aiki kema sai dai kizo wajena da yawo Kinga Safarau a Company nasu har Wurin kwanan aiki ne dasu 24hrs ba hutu Amma akwai samun kudi kema Nemo Miki inda Zaki samu kudi nakeyi inda baza ki Sha wahala ba.
Murmushi nayi nace Allah yasa.

Bayan sati biyu zazzabi me zafi ya kamani Attine ta kaini asibiti hankali tashe,Bayan gwaje gwajensu ya nuna Hawan jini ne kadan,jini na ya hau kadan,Doctor yace ya kamata idan akwai abinda ke damuna na rage na daina damuwa sannan ya rubuta Mana Magunguna Attine ta siyo min,Bayan na warke Ras,yanda na Kara dagewa da Addua naji sauki a Raina yanzu gani da damuwa Amma Bata damuna sosai sabo da Qurani Dana rike ya Zama abokina dare da Rana,Kar nazo Danbature ya dawo ya iske bani da Ify ai abin baiyi ba Sam shi yasa na dage na rage sabo da Danbature ya sameni Ify Ify muci soyayyarmu.
Tunanina Kullum yanda muke romancing juna,muci abinci tare, wanki tare,unguwa tare,ko Ina muna tare.

Yau kwana biyar kenan kullum sai Attine ta fita Dani yawon zaga gari gaskiya Lagos ta hadu domin wani yankin ko a Abuja baza a Sami wuri me kyau Haka ba,sai ko turai shima ba ko Ina ba.

AsmaBaffa

AsmaBaffa
[8/15, 11:44 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

11-15

Official

By
AsmaBaffa

Hajara Atiku sallama (laver),
Zahrau Abubakar Dambuwa
Sadiya Abubakar Dambuwa.
Ina kaunarku wajen Sharhi ga page dinku fans na kwarai.

Na kwashe wata daya da kwanaki a Lagos muna yawan Fita da Anty Attine tana aikena yanzu na fara sanin gari sosai,kasuwanni super market etc,Yau da Wuri Attine ta dawo tace maza shirya kije ki siyo kayan kwalliya ke ko kwalliya kin daina sai dai kiyi wanka kawai kisa Kaya ba kwalliya kamar ba mace ba.

Murmushi nayi kawai nace wa Zan yiwa kwalliya? Wanda Zan Masa kwalliyar yayi min Nisa sai sharrrrr....Hawaye suka tsiyayo min masu dumi,Attine jikinta yayi sanyi tace Dole ki tafi aikin Nan ko aikin ya Isa ya hanaki tunani, saman kujera na zauna dama hijab ne jikina kaina na rufe gaba daya Cikin hijab Ina ta kirsar kuka me sa Wanda ya saurara tausayi,Attine tayi Shuruuuuuu tana ji har na Gama Bata ce komai ba tace zo muje yawo kiga gari,haka muka fita Ina ajiyar zuciya,wani eatery muka je ta siya mana snacks da Ice cream sai wata burmukekiyar cinyoyin kaji.

Sosai na Samu nishadi sai na tafi tunanin inama da Danbature nazo wannan wajen ba da Attine ba, washe gari da yamma likis Attine tace na shirya yau Zan tafi gidan aiki,Attine tace sai

dai kiyi hakuri ba a samu Company ba sai Gidan wata Igbo Ijeoma girki kawai Zaki dinga tayata a kitchen,mijinta baya cin abincin Yan aiki so Bata son wahala da yawa girma ya kamata kuma,wata zata dinga biyanki dubu ashirin ya kamata ki bude accnt sai ki dinga Tara kudin, farin ciki ya kamani har dubu ashirin nace Antyna ai Ina da accnt a gtbank ya Salman yaje Dani na bude ina da komai a kaina,good cewar Attine Dan Allah ki tsare mutuncinki da addininki,Kinga gidan arna Zaki je ki kula ki Zama wise, nace inshallah wacce unguwa ce Anty? Tace Island unguwar masu kudin gaske ce sai wane da wane, idan kika Shiga Zaki ce a kasar waje kike aljannar duniya ba hayaniya Shuru,gidaje na alfarma.

Matar tayi senator sau uku sannan tayi Yar majalisar tarayya sau biyu,ta rike ambasador a kasar India yanzu Kuma Minister ce har sau uku Ana Bata mukamin minister ta Tara kudi,mijinta Steven Defence permanent secretary ne a Nan Lagos ki kula gidane gari guda dauke da securities ko Ina ga Yan aiki iri iri, yaransu biyu kacal Emanuella da Amaka dukkansu matane Yan Shekara 36 da 33yrs a turai suke rayuwarsu Amma tace yanzu sunzo Nigeria kafin su koma.

Hmm to Anty nifa bana wani Jin turanci da yawa,Haka Zaki ta jagalgalawa har ki kware Nima ai a Haka na koya,Murmushi nayi sannan na hada komai nawa na bukata muka Shiga taxi sai unguwar.

Unguwar ma ba a barmu mun Shiga ba saida Attine ta Kira Babban yaron Ijeoma sannan aka barmu muka Shiga da taxi har kofar gidan,gaba daya na rude sai kalle kalle nakeyi sabo da tsaruwar unguwar, gidan Ijeoma yafi karfin a kwatanta shi karshen haduwa ne gari guda part part Babu Bata lokaci Yaron Ijeoma Dennis ya Mana iso ko Ina matakan tsaro ne da Maaikata suna zirga zirga, ganin Palon da muka Shiga sai na susuce ban San Dame Zan kwatanta muku ba,ga wani sanyi da kamshi ta ko Ina,mun Dade a zaune Ina ta kalle kalle.

Daga baya muka ji wani kamshi na daban ya gauraye Palon tare da kwas kwas na takalmi,wata dattijuwace Fara irin na Igbo Sai hancin Nan kamar carpenter yasa guduma ya dakeshi, ga Baki chokoko lebe shaftarere,sai kiba dum gashinta wani kwaikwaye kamar birbiri ya yada zango a kanta,sai dai gashin yasha gyara Yana kyalli da sheki,Riga ce ta material me hannun bra har kasa ta sata ga wata sarka ja me kululai kafta kafta,abin hannunta sai Kara suke da gani arniya ce ta gaske,anci haram an koshi,Zama tayi da kyar tana yanga yanga,kafin tayi magana sai da ta dauki dogon lokaci mun gaji da jira sannan, Attine ta gaisheta tace Good Evening ma,Hope u r fine ma? Da kyar tace im fine thank u, Nima da guntun turancina na gaisheta ta amsa.

Da harshen turanci tace itace me Taya Ni girki? Attine tace itace,hope she's clean? Yes Ma so very clean cewar Attine, Ijeoma ta danyi Murmushi kadan sannan ta zaro kudi a Jakarta dubu ashirin ta mikawa Attine tace na Bata Number accnt dina ita a accnt take biyan maaikanta salary,Nan take ba kuskure na bata, Attine sallama tayi min zata tafi, hawaye na fara ta dinga lallashina tace ke da zaka nemi kudi kizo ki gyara kanki kafin Dan Bature ya dawo kwana Nan,wani sanyi naji sannan nayi Murmushi na nace Haka ne Anty sai nazo weakend munyi sallama ta tafi,Ijeoma tasa wata Charity ta kaini part din Yan aiki.

Ijeoma tace idan har taga kyan aikina sannan kuma tana jin dadin Zama Dani to part zata canja min na dawo part dinta muna ci gaba da yiwa me gidanta abinci tare, ko part din Yan aiki ya Hadu kamar bana Yan aiki ba,daki kowa Mata biyu Amma Ni tace a bani daki guda sabo da kwar jini irin na addinin musulunci,Haka Yan aiki duk nayi musu kwar jini sai Nan Nan akeyi Dani sabo da musulunci da yawan addinina.

Yau da dare misalin 8pm Bayan nayi sallar Isha Ma ta Aiko nazo zamu Shiga kitchen mijinta ya kusa dawowa,dama nayi wanka na na canja Kaya naje palonta Wanda ya gaji da haduwa kallo ta Kare min ta ganni fresh neat tsaf Dani Murmushi tayi hankalinta ya kwanta Dani tace let's go na bita a baya har hadadden kitchen dinta,muka fara aikin dake kalar abincinsu daban Dana Hausawa sai tace na dinga dauko Mata Abu Wanda ya kama a yanka tasa na yanka Mata,Wanda za a wanke na wanke,Wanda za a markada nayi ban samu matsala ba ko kadan tana nuna min Ina kallon yanda suke kalar abincinsu tana yi tana koya min Nima,muna Yar Hira sama sama tana tambayata kalar namu girkin Ina Bata labari da guntun turancina tana ganewa Kuma ba wulakanci ba komai muka Gama na shirya Dining na gyara kitchen sannan tace na ebi nawa naje part dinmu naci, na eba duk abinda Naga Zan iya ci sannan na Mata sallama, wanka nayi naci abincina na kwanta bacci da wayata wacce nake bincike a ciki.

Washe gari ma Haka muka shirya break lafiyayye tana jin dadin aiki Dani ga Tsafta ta,yaranta Yan Mata Amaka da Emmanuella Wanda suka dawo daga turai ne suka sakko Amaka Tasha wando short da Yar Riga taci kwalliya Wai Shirin fita tayi Nan ga wani gashin doki brown tayi kyau sai dai fuskar Nan kamar an taka Kashi sai farin kawai shima da Karin Mai,Haka Emmanuella ita Kuma bakin gashi dogo tasa tana sanye cikin wata Yar Gown da kadan ta wuce duwawunta itama ta cakare da makeken glass a Fuskarta Baki ga takalmi me tsini sunsha da jaka masu tsada sai uban farce da suka Sa yasha paint zako zako kamar na horro.

Mum dinsu suka rungume suna gaisheta ita Kuma mundukar arniya tana manna musu kiss, Wani kato,murjeje,wani dunkulelen gardi Dattijo ne ya sakko Baki wuluk dashi ga sandar girma ta kudi ya rike a hannunsa wuyansa yasha murjani,wani Zanin atamfa ya daura ga wata rigar yard me Masifar tsada da kyau 3qtr ce, kamshi kawai suke bulbulawa tare da warinsu na arna, saman Dining gaba daya suka zauna,Ma da kanta tayi serving nasu,duk abinda suke Ina labe cikin kitchen Ina gani, naji Ma ta kwalla min Kira Fadila kamar ita ta Rada min Sunan, yes Ma nace daga kitchen,Mijinta David yace who is she? She is my new House made, the name saund like Hausa, Ma tace Yeah ofcourse she's beautiful Hausa Girl, very Beautiful girl and clean,that girl she's different Imfact I like the girl so cool,friendly and Nice.

David yace da turanci ai dama a Hausawa akwai mutanen kirki sosai wasu kuwa Sam Basu da amana sannan gasu da kyawawa.

Baki Amaka ta tabe tace those criminal Hausa people Mum kika dauko Mana Yar aiki sai ta harbe mu ko ta saka Mana Bum a gida mun Kone gaba daya,Dirty people begas, Dariya Emmanuella tayi tace nawawo Aboki hmm ahhh fear them wooo,Zaki gansu so silent kamar baza su aikata tsiya ba, Baki Amaka ta tabe tana wani shanye hannu tace Almajiri people.

David Dad yace be quite let them be pls Akan ko wacce alumma Ana samun na kirki Dana banza,Ma sai lokacin tace Ina ruwansu ma suna maganarsu da turanci Ina ji,a tsorace na fito kusa da Ma na tsaya nace Good morning Dad, da Faraa yace morning, Suma Yan Matan na gaida su sai lokacin suka kalleni, Amaka ta zabura tace Chineke God Beautiful girl like u as House made ahhhh.

Emmanuella sai kallona takeyi kamar zata Hadiye Ni,kyau na ya gigita su,yanda suka yi zaton ganina ba Haka suka gani ba.

Ma dariya tayi musu sannan tace naje Driver zai kaini kasuwa na siyo abinda Babu ta bani kudi masu yawa tare da jotter inda ta rubuta komai.

Bayan na tafi suka dinga gulmar Wai bana Jin turanci sosai ai Hausawa Basu damu da ilmi sosai ba Kuma gaskiya suka fada.

Ban Saba zuwa kasuwa ba Amma Haka na zage na siyo komai, sannan muka Shiga store Nan ma na jido kayan girki muka dawo na shirya komai inda ya Dace sannan na kaiwa Ma canjinta tace na rike ta bar min na dinga murna naje Driver ya kaini banki na saka dubu Bakwai dina a accnt.

Yau da dare Amaka ta kirani Wai na hada Mata fresh Juice na Apple nayi Mata yayi Masifar dadi Ma ce ta fada musu yanda na kware wajen hada juice, ta harde a kujera tana karanta jarida na zuba Mata a cup na Mika Mata kenan ta kula da agogon Hannuna,mamaki ya kamata taga agogo na diamond me tsadar gaske da kyau,kirji na ta kalla taga sarkar Dana sa zoben azurfar Dan bature.

Tace wannan agogon a Ina na sameshi dake su babu boye boye nace na Mijina ne,tace zoben fa?nace shima Haka,tace Jesus yanzu kamata Haka Ina da aure?nace ae amma Mijin bama tare,tayi tunanin sakina yayi tace eyya sorry eh? Nace thank u.

Ta fadawa Dad da Mum tare da Emmanuela suka min jaje,tun daga lokacin suke Jin tausayina, suka ce a schl Ina na tsaya? Na nuna musu takardu na na ssce ,Ma tace zata sani a University makarantar kudi, na dinga murna na bugawa Attine waya na fada Mata taji dadi,Haka Yan gidanmu Ya Salman yafi kowa Murna.

Bayan na kwashe wata guda gidan Ma mun Saba dasu sosai,turanci na ya karu na fara kwarewa,ga albashina farko da aka min transfer naje na cire dake duk sati daya ko biyu Ina zuwa gidan Attine,Haka na Kai Mata albashina nace na Bata 20k na dauki dubu goma,da kyar ta karba sai da taga Raina ya baci ta karba.

Safarau ma Ina Kai Mata ziyara itama tazo min gidan Ma sau biyu,Bayan sati daya Ma ta kawo min Admission da komai anyi min registration a Health education zanyi Degree na Shekara uku,na fara zuwa schl ba,driver ke kaini ya dakko Ni, Emmanuela da Amaka suka ce ya kamata na waye na dinga matsewa cikin kana Nan Kaya,nace mu addininmu sai Miji ake sawa ko a gida,Haka suka suyo min Kaya kana na iri iri Amma bana sawa ganin Haka sai suka dinka min su atamfa da materials laces,shadda Riga da skert da dogayen riguna tare da mayafai na sirara masu kyau,takalma da jaka iri iri, idan kun ganni kamar bani ba,tsofaffin Kaya

na Attine na kaiwa ta San yanda zata yi dasu.

Karatu da aikina nakeyi Ify Ify ya rage min tunani da yawa sosai na Kara girma,kiba skin Dina tayi fresh sai sheki nakeyi kullum kamar wata Amarya haka nake, ga Saloon Ina yawan zuwa Ana wanke min gashi na,lokacin dasu Amaka suka ga gashina haukacewa sukayi, Ma ta dinga mamaki kamar gashin Baturiya.

Yanzu tuni na dawo saman Benen Ma a Nan ta bani daki kusa Dana yaranta komai akwai kayan kwalliya iri iri,gashi Hawa biyu ne,Ma da mijinta a saman karshe yaranta a hawan farko.

Mun Gama girki munci mun Sha nayi Shirin kwanciya Bayan na Gama karatuna na mike jikin window na dake kallon gidajen waje kullum sai na leka na kalli unguwar da tsaruwarta.

Yau ma labile na zuge Ina tsaye da tea cup a Hannuna Ina kurba wani gida nake ta kallo nesa da mu sosai kaf unguwar Babu kamarsa a kyau duk da kyan na Ma ba komai bane Akan wancen gidan,wani daki na gani an kunna Kwan lantarki taram ya gauraye da haske,wata Yar aiki ce Naga ta wuce da plate, ta sake dawowa ta wuce tare da wata mace dattijuwa fara kamar Baturiya ban fiye gani tar tar ba Tunda da Nisa,Yar aikin ta sake ficewa Matar na gani ta saka jajayen kaya wani yadi kamar dodon tsafi Haka ta dawo Fuskarta ta rufe tana motsa bakinta da Alama magana takeyi,sai Naga ta Zama kamar horro ta Bace bat,tsoro ya kamani Bayan 30mnt sai na ganta wukil ta dawo inda take da wata tukunyar shirka a hannunta,ta ajiye tare da cire Kaya ta canja nata na farko ta kashe wuta duf sannan ta bar dakin,steal Ina tsaye bul Naga a dakin an Kara kunna light wannan namijine fari tar shima kamar Bature Amma Banga fuskarsa ba ya juya baya rigarsa ya cire gabana ya Fadi exertly jikin Danbaturena sai dai wannan yafi fari da mirjewar skin kamar ka tabashi jini ya fito,ko Dan Danbature a kauye muke ne ga Ciwon hauka shi yasa,ga wani uban gashi a kansa Wanda yasha askin irin shegun turawan Nan mawaka ko Yan film kyau iya kyau,gashin Nan Baki,shi ba gajere ba, ba Kuma dogo can ba,ba rammame ba ba siriri ba, so nake kawai ya juyo Naga fuskarsa, na bude kofata ta baya dama akwai corido Dan nafi kallonsa sosai na tsaya a Nan,barin wajen yayi ba tare da ya juyo fuskarsa ba ko yasan da wata tana kallonsa ba, ya Dade Nima Mayyar naki tafiya,sai gashi ya dawo sanye da rigar wanka fara Kal da Alama wanka yayi,jikin window dinsa ya tsaya shima dake facing nawa Amma Sam kasa yake kallo Bai kallo saitin gidanmu ba,

Gani nayi kamar Danbature ne ke min gizo nace Kai wannan idan ma ban samu Danbature ya dawo ba to Naga Mijin aure,Dole ne ma ya aureni tunda suna Kama, Dole na San yanda zanyi na Kulla alaka dashi, Kuma sai Naga Danbature na kamar yafi wannan kyau da komai,sannan ya fishi kira da cikar zati har ma kwarjini da komaima.

Da karfi na kwalla tare da Mika Hannuna Ina tsalle nace Danbature......Baturena .....kaiiiiii.....Dan fari ....juyo.....Nan...gani .....kalleni......Kai......Malam.....nice Fadila......dolene ka aureni......gaba daya dake dare ne duk kusan layin wasu da dama sunji Ni, amma ba wasu Hausawa Basu san me nake cewa ba,shi kanshi Wanda nakeyi dominsa Bai ji ba gani nayi ma an kawo Masa lemo Yana kurba Yana shafa sumarsa, dagowa yayi kadan sai da na firgita da kyansa, wannan ai Danbature yafi shi, Amma suna mugun Kama, wata budurwa na gani itama zukekiyar gaske fara tas tazo ta rungumeshi ta baya.

A fili nace na Shiga uku kaga tsinanniya Karuwa,Anya wannan ko dai Matarsa ce wash na

dafe kirjina, kishinta naji na Kara kwallawa da karfi Ina nunata da yatsa kee....Mayya....matsa daga jikinsa....Mijina..nane....Arniya.....Arniya....Allah ya tsine Miki na Kara tsalle kamar zararriya na Dane karfen jikin corridor din nace Mayya....ke...uwarki Ina Mata dakuwa kuwa Allah yasa karaf ta hango,ban hakura ba nace karbi Nan ungo na Kara Mata zagi da tafin Hannuna Ambola dakuwa.

Kirjinta ta dafe kamar taga Aljana tayiwa Namijin nuni da ya kalli Aljanna a sama can gidan,ai kuwa ya kallo wajena gabana yayi mugun bugawa daram kamar Danbature,Amma Ina wannan ya take Danbaturena kyan fata sabo da hutu ya ratsashi,na tabbatar da Danbature ne ya samu hutu Haka to ya ninka wannan komai,to me ma zai kawo shi Lagos.

Haka na dake na nuna shi da yatsa sannan na sarke yatsuna kana Nan biyu maanar aure, Ido ya zaro,kiss nayi Masa ta iska sannan na hura Masa ta iska, dariya ta kamashi sai yayi Alama shima ya cafke ya lika a zuciyarsa dariya na kyalkyale da ita na tafa Masa sannan na daga Masa Babban yatsa  irin Good. Tunawa nayi Ina da aure fa sai na fara istigifari.

Budurwarce ta dinga kwasa dariya tana ganin haukata gani Yar yarinya tace kawai irin Yan iskan yaran Nan ne kawai yayan masu kudi fasikai,shima Haka yayi tunani sai Naga sun koma ciki matar ta fice shi Kuma ya gyara labilensa tare da kashe light alamar ya kwanta.

Ban taba samun jindadi irin wannan ba Tunda nake a duniya sai lokacin da muke tare da Danbature na,fes nayi bacci na tashi,inayin sallah da azkhar na Kara lekawa ta kofar dake dakina ta baya ko zanga me kama da Danbature Amma ban ganshi ba gani nayi ma an rufe window din ruf,jiki ba laka na wuce kitchen inda na iske Ma ta fara aikin,na gaisheta muka ci gaba da aikinmu Ina ta faman tunanin Danbature da mutumin jiya me kama dashi.

Bayan na Gama komai nayi Shirin schl na wuce,su Ma da yaranta duk sun wuce Office Suma ba zama.karatuna nakeyi sosai.

Yau ma dai dai lokacin jiya da dare Naga me kama da Mijina ya sake fitowa Yana Shan iska direct window na yake ta faman kallo,katsam na sake Nima fitowa, hannu na daga Masa shima ya dago min Yana Murmushi,Alama ya min wai na sakko na zagayo gidansu,kafada na makale nace sai dai shi yazo, katuwar paper ta Zane ya dakko ya min rubutu da Babban Baki Ur Name pls? Nima na rubuta na nuna Masa ya karanta Fadila.

Hausa girl ko? Ya sake nuna min,Nima nace ae Ashe kana Jin Hausa? Yace ae Babanmu bahaushe ne mun zauna a Kano,Adamawa, jigawa duk gidanmu kowa najin Hausa nace to yayi kyau.

A Haka muka dinga Hira sosai cike da nishadi Ina magana da me kama da Mijina.

Yau mun kwashe kusan sati Uku kullum sai munyi Hira da wannan mutumin Wanda yace min sunansa Doctor who ake ce Masa,kowa na tambaya Dr Who za a nuna min shi da gidansu.

Sosai muka Saba da juna, Amma dare daya ya nuna min manufarsa Yana so yayi xxx Dani shi manemin matane tun daga lokacin naji bana sonsa na tsaneshi, ba wani boye boye yazo wajena har gidan Ijeoma ya fada min halayensa da niyyarsa a kaina,zuwansa wajena biyar tunda Naga ba mutumin kirki bane na daina saurararsa Amma Kuma sai suna matukar Kama da Danbature.

Ijeoma tayi mamakin alakata da yaron masu kudi Haka Wanda Babu kamarsu a Lagos, ji akeyi dasu kowa yasan da zamansu.

Yau Sunday kowa Yana gida yau Amaka zata kawo Mana saurayinta Dan Rivers Wanda tare sukayi karatu a turai Kuma shi zata aura,sosai aka shirya Masa liyafa,matashin Igbo me kudi gurjeje dashi katon Arne, yazo Ni nayi serving Nasa abinci Wanda sai kallo na yakeyi kamar maye,Silvester sunansa Ma tabar Palon,Emmanuella Bata nan,Amaka ta mike tace Bari ta dakko wayarta zata Kira Emmanuella tazo taga mijinta,Yana ganin Haka ya matso kusa Dani Yana fada min wai yanzu Ni yake so nafi matar da zai Aura Amaka kyau,Amaka karaf a kunnenta da ihu ta karaso tare da rufe Ni da duka Evil hausa girl, Silvester da sauri ya bar gidanta, Amaka tace zamu hadu da Kai I will kill u.

Ma ta fito taji labari Haka ta dinga zagina tana Harara ta da kyar na Basu hakuri suka hakura Wai laifi nane.

Bayan sati biyu Emmanuella ta kawo nata Richard Wanda zata aura a gaban kowa ya dinga min signa,ranar kaca kaca suka Bata da saurayinta,Nima Ma tace you again ta fara min gorin abubuwan da suka min wai naci Amana suka kamani suka yi min dukan kawo wuka naji jiki duk sun kumbura min jiki, ranar Ma ta bani ragowar kudin aikina ta sallameni,duk abinda suka siya min na kayan sawa da kayan kwalliya sai da suke cika min akwati biyu da komai Basu kwace ba suka sani a taxi sukace na tafi gidan ubana bazan zauna musu a gida ba,schl Kuma Ina level 1second semester suka ce naje naci gaba da zuwa har na Gama level 1 na biyawa kaina sauran shekarun ko na tsaya iya nan na karbi transcript.

AsmaBaffa
[8/15, 11:45 AM] +234 813 228 4370: 🏕HADIN KAI🏕

16-20

Official

By
AsmaBaffa

Ina sonku fans a zubo min Sharhi naji dadi typing kunayi Ina Jin dadi💋😍😍

MAMAN ABBA,HABIBA,AICHA,AUNTY SUMEE,ZAINAB ATIKU SALAMA,MAMAN MEENAT, OUM page naku ne Yan gayu na.

Katsam Attine ta ganni da Kaya Niki Niki cike da bacin rai kamar zanyi kuka,Attine tace karki

yi kuka fada min me ne ya faru nasan Baki da laifi Fadila,abinda ya faru na kwashe na sanar Mata,tace to kyalesu idan sun gane gaskiya zasu nemiki na tabbatar Babu Wanda zai zauna dake Baki Shiga ransa ba Fadila.

Zamanmu Shar nida Attine muyi hirarmu.
Kwana uku tsakani Ma da yaranta su Amaka suka ga amfanina a gidan,suka gane gaskiya bani da laifi mazan ne masu laifi maciya Amana.
Wayar Attine ce tayi kara Ma ce da kanta ta nemeta tana dagawa ta Bata hakuri tace sun gane gaskiya da Allah a sani a taxi da kayana na koma,murna da farinci ya kamani sabo da naji dadin Zama dasu ga kyautata min da sukeyi inyi abinda nake so kamar Gidana,wanda musulmammu baza su zauna da Yar Haka ba bare har a wani sani a University, Kuma bana so na daina ganin Dr who me kama da Dan bature.

Inda yake birgeni yanda zaka San wayayye ne idan ya nemi kuyi fasikanci kika Ce no to bazai Miki Dole ba,Kuma bazai Kara miki Zancen xxx ba sannan bazai fasa muamula ta mutunci da ke ba,ta Nan zaka San Dr Who ya Gama wayewa baya Dole,sannan kyauta da mutuntawa zai Miki,sabanin wasu mazan Wanda idan ba wani Abu zasu samu wajen mace ba to fa ba ruwansu dake.

A ranar Attine ta kaini again gidan Ma da kayana,suka tarairayeni tare da bani hakuri Akan abinda ya faru,nace ba matsala,Attine Tasha kyautar Atamfa me tsada turmi guda da kudi masu kauri.
Dr who Bai San Ni Yar aiki bace Amma Yana mamakin musulma a gidan arna,sai daga baya yaji labari ba karamin mamaki yayi ba Jin Wai Ni me kyau Haka a matsayin yar aiki,Bayan masu kyau da dama gasu Nan Akan son Kudi sai karuwanci sukeyi suna Zama hamshakan masu kudi sai kaga mace tana Hawa dalleliyar mota Wanda gidansu Gawayin girki ake siyarwa,Makkah duk Shekara Ana daukan pics Ana sawa Dan kawai q burge mutane anje Makkah da kudin Haram anyi shawagi an dawo.Allah ya shirya.

Bayan na dawo da sati biyu Emmanuella da Amaka suka koma London abinsu,daga ni sai Ma muke rayuwa kowa Yana addininsa, ga schl dina Ina zuwa ina karatu na.
Daga makaranta na dawo a gajiye,Ma tana wajen aiki Bata dawo ba wanka nayi tare dasa gown marar nauyi iya gwiwa Zama da arna har na fara koya Nima kwanciya nayi na huta.

Wani Cikin Securities ne yazo yace Wai nazo inji Dr who,a wata arniyar mota yazo sanye cikin kayan likitoci nasa hijab naje, Bai fito daga mota ba ya sauke glass muka gaisa yace masu Hijab gashi ya Miko min wata Leda cike take da snacks sai Ice cream,Godiya nayi na karba Bai jira nace komai ba ya ja motarsa ya tafi na koma cikin gida Ina daukan abinda nake so Ina ci.

Satina Uku da dawowa Mijin Ijeoma ya fara shaawata a gidan yanda yaga Ina kwalliya da gyara kaina,kullum muka hadu sai ya faki idon Matarsa ya dinga min maganganun batsa, na Masa magana yaki ji ba yanda zanyi dashi,idan yaga Ijeoma Bata Nan sai ya dawo gida daga Office ya takurawa rayuwata,har schl Bina yakeyi,Ni Kuma Ina tsoro na kasa sanarwa Ma yace

idan na fada zai batar Dani.

Gajiya nayi sabo da ina kitchen ya shigo ya fara shafa min Mazaune Ina guduwa tuni na fara hawaye Ina fada Masa Ina da aure Amma yaki ji kicif sai ga Ma ta Fado kitchen Ina kuka nake fada Mata ba laifi na bane wlh gwara ma ta sallameni tunda matsala nake zamar Mata a gida,karshe Nace na tsani gidan Baki daya sabo da cin mutuncin aure na da yayi bazan yafe Masa ba.

Ma tasan bani da laifi kawai Haka ta sallameni again salin alin tayi min kyauta me yawa,sannan tace naci gaba da karatuna zata dinga biya min nayi ta Godiya na tafi gidan Attine na sanar Mata komai taji dadi sannan tace inshallah zata Nemo min gidan musulmai.

Hankalina kwance nake zuwa makarantata sannan muna zaman mu Ify da Attine, na Kara wani wayewa ga kyau na ya ninka nada,na Kara girma da tsayi shape dina ya fito sosai Duk Wanda ya ganni sai ya Kara son sake ganina.ina da kawayena na schl Amina da Rahina yaran mutunci.

Safarau ma ta samu hutu yau tazo zata yi weekend a gida,tace mutuniyar wannan kyau Haka da Alama an daina tunanin Dan Bature,dariya nayi nace Anty Attine kinji ta ko?ai Yana Raina har abada yarinya, hmm kin fara chart? Cewar Safarau nace Allah kiyaye, wayata ta karba ta tura min Hausa novels iri iri ta koya min yanda Zan bude na fara karatu,ai kuwa tunda naji dadi love iya love ga koyon abubuwan rayuwa yanda zaka kula da Mai gida,na tuna idan Danbature ya dawo haka Zan dinga nuna Masa love kawai sai na dage da karatu ba dare ba Rana,watarana Har masifa Attine ke min.
Na waye sosai na Karu ta hanyar karatun Novels Ina yin na schl abina ras.

Bayan sati hudu lokacin mun Gama second semester Ma tayi min registration da komai na level two muna hutu bamu koma ba,Attine ta rafka sallama ta dawo daga unguwa, sannu da Zuwa Anty ya hanya, Alhmdllh tace sannan tace kafin na zauna Bari na Miki albishir na samo Miki gidan aiki gidan musulmai hamshakan masu kudi Ne duk fadin kasar Nan an San da zamansu,aiki ma idan kika samu a gidan to fa kakarki ta yanke saka, Hajiya Asiya daya daya cikin matam mutumin ce take neman yarinya nutsatsiya da zata dinga Mata girki wacce ta iya girki da tsafa girki ne kawai aikinki.

Alhmdllh na huta zaman banza, Attine tace gobe a kaiki sai ki shirya naki ya naki,Family house ne sai kinyi taka Tsantsan kin nutsu,Bari na Baki tarihinsu kadan yanda naji kafin idan kinje gidan ki gani da idonki.

Alhaji Sulaiman Araba Lagos shine cikakken Sunan me gidan idan kina Jin radio ko News Zaki jishi sabo da kudinsa, Dukiyarsa tun ta gado ce shi kadai iyayensa suka Haifa, Babansa da sauran kannena mahaifansa ko yayye duk basa Raye sai yaransu,Kanwarsa ce daya da yaranta mijinta ya rasu tana gidan da yaranta part dinsu daban,yaran yayye da kannensa duk shi yake rikesu suna gidan ko wannensu da part dinsu,Dattijone na kwarai me kirki da son dangi

ga kyauta,bashi da ilmin boko sai business na alatsine uwar me karya kasa kasa bashi da lokacin kansa.

Babansa ya rasu sai babarsa tsohuwa da ta rage tsohuwa ce wacce take tarwatsa kan dangi,Bata kaunar zaman Ify,kullum a gulma take tana hada dangi fada ba hadin Kai ko kadan, Haka kawai zata hada gaba da fitina tsakanin jikokinta da Matan danta.
Hajiya Khadija suna kiranta da Nana tsohuwar banza ce magulmaciya,shi yasa jikokinta ba wani mutuncinta suke gani ba.

Alhj Sulaiman Araba Lagos Dan Asalin katsina state ne,bafillace ne usul Kyakyawa fari dashi.Araba Lagos matansa uku Matarsa ta farko sunanta Karimatu Yar garin Adamawa ce, Karimatu akwai rashin Imani,son Kudi ga Hassada,Dole Mijinta ya Mata Abu ko baya so sabo da Yana tsoron masifarta.
Tana da Yara biyar Habib shine Babba da Matarsa Farida Yana Zama a Abuja,sai Saudat tayi aure a lagos,sai saddiq Wanda shekararsa 26 ya kusa Gama degree a UK,Ammar 19yrs yanzu Yana Ukraine,khairat auta 16yrs tana Ss1.

Sai ta biyu Asiya Mai hakuri,nutsuwa saliha ga hankali ba ruwanta.Araba Lagos Bai damu da ita ba Bora ce a gidan,kowa taka ta yake, yaranta shida,khausar tayi aure itama a Abuja, Yousuf 26yrs shima a Paris ya Gama degree ya dawo gida,saif 23yrs Yana level 2 a China,Khadija 20yrs tana level 1 a India, Kabir 17yrs Yana ss2, Ahmad auta 11 yrs Yana jss1 Nan Nigeria.
Yara ne masu tarbiya ba ruwansu.Asiya Yar zamfara State ce.

Sai mowa Amarya wacce tafi kowa fada Babu wacce ta Isa ta kama kafarta wajen me gida, sai abinda tace Aunty Amarya Maryam kenan Kyakyawar baturiyace ta gaske dattijuwa me kyau gata itama iyayayenta Yan Paris ne masu kudin gaske ne,Bata auri Araba Lagos ba sai da ta tabbatar yafi su kudi,kudi ta gani ta aureshi,musulman kasar France ne Amma lalatacciya ce ta gaske Bata bin addinin nata,iyayen Sunyi Mata fada har sun gaji, itace Shan giya,Shan wiwi,Bata son talakawa,Bata da mutunci ko kadan,tunda tazo Nigeria take Hulda da Yan kudu ta koyi tsafe tsafe iri iri wajen arna.

Gata tana neman mazan waje Yara matasa tana Basu kudi,shi yasa taki yarda ta haihu da yawa Yara uku kacal ta Haifa, mazanta biyu mace daya, Namiji na farko 30yrs yake suna Ce Masa Ice ance wannan sai kinyi taka Tsantsan baya ragawa Wanda ya Shiga gonarsa,Bai son kazanta,baya Shiga harkar kowa gashi da zuciya,cikkaken Masifaffe ne,kaf gidan tsoronsa akeji,sannan Bai son kallo sabo da Yana da kyau ance kamar aljan sabo da kyau ki kiyaye wlh. Nace to Attine shi ba musulmi bane naji ance wani Ice, hmm yafi kowa addini a gidan musulmi ne,gidan suna da nickname kowa dashi ake kiransa, Basu da aure ne?sabo da masifarsa suke Ce Masa Ice, baya ko dariya.

Ae duk Namijin da kika gani a wannan gidan to baida aure,na biyun Kuma Who nickname nasa shi ance yafi kowa saukin kai,sai dai Yana Shan giya watarana Kuma Yana neman Mata Amma ance duk yafi kowa kirki,shima kyakyawane.

Sai Autarsu Meenal suna son kanwarsu akanta sai su koreki a aiki,ki kula tana da kala sharri iri iri mate dinki ce 18yrs.

Maryam Amarya
Ta Gama tsafe Alhji sai abinda tace,farko a jigawa suke zaune tace ya Mata kauye Kano take so sun kwashe shekaru ashirin a Kano tace Abuja ya maidasu can tace Rivers State Bayan Sunyi 3yrs tace a dawo Lagos yanzu shekarunsu takwas a Lagos tare da danginsa da Dangin matansa gidane na Alfarma na fada a jarida.

Sabo da Yana son zumunci yaki raba musu gida yafi so yaransa su shaku da juna su hada kansu,Kuma abin mamaki yaran Amaryar suna da nutsuwa ance Basu gaji halinta ba Amma Babban ya Dan dauko wulakanci da izza kadan Kuma baya ragawa duk Wanda ya Shiga gonarsa.

Matan dangi ma duk sun dawo Yan Mata da samarin cikin danginsu ko wacce an Basu part na Yan uwanta a Nan suke karatu da komai Mijin na daukan nauyinsa.

Yaran da ake rikewa kiyi hankali dasu sunfi Yan gida iya shege Kuma duk farko daga kauye aka kawosu suka yi clean.

Karimatu uwargida yaran Yan uwanta
Naja (cilla)
Fatiti
Zahrau Yar dagwas
Zulfau zuly kanwarta ce.
Sai maza
Saad Boy 40yrs ba aure.
Shehu Niga 35yrs

Yan uwan Asiya daga kauye
Sumayya(chakwas)
Kanwarta Rahina da kaninta Usaini Usy 27yrs
Sai na Amarya Yan kasar waje da kawarta
David Dan uwa Arne 30yrs
Michael Dan uwa arne 25yrs
Muhammad 26yrs
Irfan 17yrs.
Kawarta Sahr
Sai Linda itama Kawarta.

Shi Kuma kanshi me gidan Yana da yaran Yan uwa maza da Mata sun Kai su goma Sha ko wanne akwai part dinsu daban tsakanin part da part Nisa ne sosai kamar estate ba abinda Babu a gidan,masallaci da Islamiyya duk akwai,mota idan zasu Shiga sai driver ya kawota har kusan bakin kofa,basa muamula da talaka,mutane komai kudinka Basu damesu ba musamman turawa na Amarya Maryam rayuwarsu daban a gidan.

Fadila Zaki Sha kallo a gidan,Zaki fafata sai dai ki Zama wise karki sake a takaki Kuma karki Shiga sabgar kowa Amma fa Zaki Sha kudi ki samu iyayenki da Yan uwa suyi Alfahari dake. So nake ki Dan Tara da yawa Abbu sai yasha mamaki Ina Miki tanadi.

Ki Zama me juriya kawai,Murmushi nayi nace Inshallah ko Dan Na kularwa da Danbature na jikinsa ai nayi,dariya Anty tayi tace iyye marar kunya,da gudu na kule cikin bedroom na fada saman bed tare da lulawa tunanin Mijina abin kaunata.

Washe gari da yamma karfe 5 muna taxi Ni da Anty Attine da akwatunan guda biyu manya shake da hadaddun kayana Wanda Ma ta siya min da komai na bukata ta kun San yanzu fa na fara wayewa,unguwar su Ma ta masu kudi Naga mun nufa Attine tace kin San masu kudi Ne fa Dole kiga unguwar su Ijeoma,abin mamaki sai Naga katafaren gidan su Dr who me kama da Danbature Ashe gidan yafi ma yanda nake zato.

Attine tace wannan gidan Babu kamarsa kaf unguwar Nan bama layin Nan ba,alatu ma sai mun Shiga karki tsorata Zaki ga ko Ina sojoji da masu aiki iri iri, tun daga bakin gate na Raina kaina na ganni wata kucaka Dani, ban Gama mamaki ba saida Attine ta Kira Yaron Asiya a waya ya sanar Mata ta bada Umarnin bakinta ne a barmu mu Shiga gate aka bude kofa karama cewar baza mu Shiga da kazamar taxi ba gidan, idan ba Motocin gidan ba Babu Wanda ya Isa ko parking yayi da motarsa yanzu sojoji zasu saki harbi,rawa jikina ya fara yi Kar karkar, gidan duk inda kuke zatonsa ya wuce Nan,kafin na Shiga da akwatina na sai da sojoji suka duba ciki suka tabbatar ba abin cutarwa sannan suka Bari muka Shiga ciki tare da Driver na Asiya Yana Mana jagora,Attine ta kalleni yanda taga na hada uban Gumi jikina na rawa, Murmushi tayi tace ki kwantar da hankali kamar Kinga wani malaika Fadila,jikina Yana rawa kamar tsohuwar Shekara dari nace to..to Anty.

Gidane ko Ina tiles da tiles ga flowers swimming pool iri iri har kala nawa,motoci kuwa a parking space kamar wajen saida su,masu tsada Babu ta kasa da million goma, Ni ban San yanda Zan kwatanta maku gidan ba,duk wani Abu da ake yayi a kasar Nan Babu shi a gidan nasu kalar latest ne sai sun Gama yayin Abu da shekaru sannan ake Fara kawo abin kasar nan. Komai nasu baza ka ganshi a wajen mutane ba tsada ma baza ta Bari a iya siya ba.

Wani Palo muka Shiga gari guda kujeru na Alfarma set kala sun Kai biyar a ciki,sanyi da kamshi ta ko Ina labile ma Dana ganshi tsab zance wani material ne na dinka naje gidan ratsatsan biki dashi, wasu abun ado kamar Gold a palon, Kai abin yayi yawa jikina na ya Kara daukan rawa ganin wata zukekiyar Yar budurwa ta gilma ta wuce ko kallon inda muke Bata yi ba,cikin kana Nan Kaya take hadaddun gaske masu tsada,wani yawu na Hadiye makwat,Driver yace Hajiya kalle kallen naku yayi haka muje Mana,wani Palon muka wuce Nan yafi na baya haduwa,muka Shiga na uku yafi ko wanne haduwa,a Nan yace mu zauna zata fito,ita kanta Attine ta rasa bakin magana.

Mun Dade a zaune har na fara gyangyadi sai mukaji Karar takalmi kwas kwas wata dattijuwa take sakkowa daga saman bene chocolate color ce sanye cikin shadda dakakkiya dinkin Senegal,Tasha aiki Purpple color, hannayenta da wuyanta duk Gold ne,kamshi ya bulle mu,jikina na rawa har yau, ta zauna tare da daura kafa daya kan daya,Attine tace Ina yini ba

laifi ta saki fuska tace Ify Alhmdllh kune bakuwar? wace cikinku me aikin? Attine ta nuna Ni,Nan murya na rawa na gaisheta ta amsa tare da bin akwatina da kallo,tace Amma bada kauye kike ba ko? Kai na iya dagawa tace Good, waya ta dauka tare da Danna Kira ta Kara a kunne chakwas kawo min Handbag dina.

2mt sai ga wata budurwa zata Kai 20yrs ta sakko cikin matsatsun kana Nan Kaya kanta yasha gyara ba dankwali ba laifi tana da Dan kyau Jakar ta Mika Mata sister gashi,ba laifi tana da Dan kyau,a wulakance ta kallemu tace sister sabuwar Yar aikince Haka zukekiya da ita hala bada ga kauye ta dira ba?ta Dan goge a nan,? Ta furta tana Mana kallon raini,  Chakwas ban son iskanci da rashin tarbiya ki gaida su,Kuma na hanaki matsewa maza na sintiri Amma bakya ji jiba shiganki banza.

Bata gaishe mu ba ta juya tana Danna makekiyar wayarta tayi tafiyarta,Matar tace na gode Zaki dinga dafa min abinci shine aikinki abinda nace shi Zaki dafa karki sake wani ya saki aiki a gidan Nan kiyi sai kishiyoyina sai yaro na Dana ke kauna Zaki ji Ana kiransa Ice ba Dan Dana Haifa bane Amma Ina sonsa yafi Zama a part dina yafi cin abinci a Nan,satinsa biyu da dawowa daga British.

Ki kiyaye ban son rigima,ya sunanki? Nace Fadila tace nice name sunana Haj Asiya nice ta biyu a matar me gidan,Ana kirana da Nanee, tunda ke me girki ce bazan kaiki part din Maaikata ba Zaki zauna a Nan part dina Zan Baki daki can Palon farko,akwai maza da yawa a gidan Nan Marasa tarbiya ki kiyaye ki Kama kanki ki rike mutuncin ki, masu girkina dama duk fasikanci yasa na koresu Dan Allah muyi Zama na Amana abinda kike so ki sanar min,da kanta ta nuna min ko Ina na gidan da part dinta har sama sabo da Kar na bace a gidan, kitchen duk ta nuna min iri iri.ta kalleni tace kinyi karatu ne? Nace yanzu Ina level to a Niclos University Ina karantar Health education, wow wa yake biya miki?,, Murmushi nayi nace Wata Ijeoma minister dake makwaftanku nayi aiki a gidan na girki shine dadin Zama yasa take biya min, Asiya tace me yasa kika bar aiki wajenta? Mijinta ne fasiki Yana min Maganar batsa sannan ya dinga kokarin taba Ni,shine nace ta sallameni,tasan bani da laifi yasa taci gaba da biya min schl.

Hmm to yanzu Yar aikin girki na University ya za ayi da girkin Rana?ga Dana baya jure yunwa, 1pm ake Kai Masa abinci Office ko ya dawo gida yaci, ai ba damuwa ko me nakeyi a schl Zan dawo kafin 1 nayi ko lecture ba damuwa Dan na rasa wata kin San makarantun kudi Babu wata matsala wasu ma sai su kwashe watanni Basu je schl ba kuma kiga sunci exam sabo da kudin kawai suke so basa ka da kowa,Murmushi Asiya tayi tace wlh kin waye ba wani nuku nukun magana Haka nake son rayuwa da mutum, Dan Allah before 12pm ki dawo 1pm dot ki Gama shirya abinda nace ki dafa ko wanne time,nace Inshallah yanzu ma hutu muke saura sati biyu mu koma.good sannan tace gobe ki shirya Zan kaiki part part a gidan Nan sabo da kisan kowa kema a asanki,tare da uwar mijinmu. Nace to.

Attine tace to Ni Zan tafi Kudi ta Bata sun Kai dubu Hamsim ta siyi recharge card,Nima albashina har dubu Arbain tace zata iya Kara min fin Haka idan har na iya aikina Kuma ban jawo Mata magana ba.

Bayan Attine ta tafi ta bani dakina hadadden gaske a Palon farko sannan tasa aka kawo min abinci lafiyayye kala biyu,tace gobe da safe Zan fara aikina, a Raina nace Ina wa zai hada gidan Nan Dana Ma ko kusa ko Alama.

Da Asuba na shirya tsab bayan nayi sallah da azkhar na Shiga kitchen Bayan naje na gaisheta da ladabi ta fada min abinda take so da safe tace nayi daga ita sai danta Ice sauran Yara da Yan uwanta masu Dafa musu abinci daban,naji dadi bazan Sha wahala ba,

Girki ne na Yan gayu iri iri ta sani nayi wani abunma sai da na duba YouTube,gani dama na iya girki tuni part din ya dau kamshi ko Ina Wanda yayi sanadiyar jawo hankalin mutanen gidan kowa sai ya nemi a wanne part wannan kamshi ke tashi Haka?

Kafin kace me Sumayya Chakwas ta fasawa gidan labari Nanee ce tayi sabuwar Yar aiki Wai Fadila wata budurwa kamar balarabiya kyau iya kyau wata Yar gayu.

Mamaki munafuncin yakai kunnen kowa dake kowanne part, yau har kunne Kaka Babar Araba Lagos Hajjojo labari ya sameta,jira kowa yakeyi yaga wace ce Fadila me kamshin girki.

Bayan na Gama girki iri iri cikin kankanin lokaci na shirya Dining sannan na gyara kitchen na sanar da Nanee na Gama mamakin saurina ya kamata tace na gode da Alama za a je dake Murmushi nayi na fita abina,dakina na fada toilet na fesa wanka Naga gidan Nan sai da kwalliya in ba Haka ba rainaka Matan zasuyi, lotion Dina na shafa me kamshi na sa wata doguwar Riga ta Arabian dark brown sosai nasan tana min Masifar kyau Kuma Bata dameni ba powder na shafa da man lebe pink kadan na fesa Yan turarena sama sama,wata Yar aiki ce ta buga min kofa lokacin Ina gyara dakina tare da shirya komai nawa, Ina budewa ta harareni sabo da na fita komai tace kije inji Nanee ta juya abinta.

AsmaBaffa

[8/15, 11:45 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

21-25

Official

By
AsmaBaffa

Asycool, Fancy Honey, Oum Hanan,zulaihat,Queen kk,Jannat, Maman Abba,Maman Fahad.

Ga page dinku mutanena.

Fita nayi na sameta palonta a sama har kasa na Duka nace Nanee gani, tace Haka nake so Fadila Yar aiki tsab ta Zama kamar kowa ba Wai son Kai yasa kaga Yar aiki kamar an tonota daga Rami an maidata kamar dabba, akwai Islamiyya ta Yan aiki daban a gidan Nan,sannan akwai ta yaran masu gida daban,Dan Haka ki dinga zuwa Islamiyyar Yan aiki wacce akeyi da yamma duk ranar Saturday da Sunday,ta masu gida kuma Kullun kullum suke zuwa,murna nayi nace Inshallah Nanee na gode,tace tsaya muje ki gaida kowa Kar abin ya zame min bacin Rai a gidan nan,.

Tana gaba Ina binta a baya misalin 11am muna fita sai ga dalleliyar mota ta alfarma da gudu guard ya bude mata shiga tayi tace na shigo mamaki ya kamani a gidan Nan part ma za a je sai an wani Shiga mota,Haka na Shiga muka tafi,Nanee Tasha wanka cikin atamfa Super Holland, tafiya kadan a mota muka tsaya,na fita da sauri na zaga da gudu na budewa Nanee mota,ba karamin dadi taji ba Ina mutunta ta Haka, wani part muka Shiga wanda ya gaji da haduwa Yan aiki sai sintiri suke yasha gyara, Cikin wani katafaren Palo muka Shiga,wata dattijuwa tsohuwa ce fara yakunanniya Tasha Lace me tsada da Alama itace Babar me gidan,Nanee ta zube a kasa tare da sallama Nima nayi yanda tayi, Nanee sabo da biyayya kanta kasa ta gaisheta Nima Haka Amma da kyar ta amsa sau daya, tace Asiya uwar kinibibi komai ki nuna kinfi kowa ladabi Wai ke kissa ko to baza ki taba birgeni ba.

Mamaki ya kamani tace wannan Kuma kodaddiyar daga Ina?nasan danginku babu farere kyawawa haka,Asiya Bata damu ba tace Yar aiki nace me min girki tare da Ice, Baki Hajjo ta tabe tace Dalla gafara can wai me yiwa Ice girki Ice din danki ne? in ba shishigi ba,Kinga je ku karata can dallah ku barmin part dina ban son ganinku.

Ji nayi na tsani Hajjo tsohuwa haka muka tafi jiki ba kwari Asiya tana share hawaye, nace kiyi hakuri Nanee komai me wucewa ne nawa take duniyar,dadi taji a ranta tace na gode Fadila kina da hankali.

Part din gaba muka je Wanda ka rantse gidan wani sarki ne Nanee tace  Nan part din mijinmu ne Bai cika Zama a kasar ba Amma Ni baya bani kwana na yanzu Fadila,na yarda dake shi yasa na iya fada Miki ban San me nayi Masa ba yace bazai iya kwanciya ko daki daya Dani ba,yayi niyyar sakina Ice shine Wanda ya Hana hakan,Kinga Dole naso Dana Ice, tace Ina cikin wulakanta a gidan Nan,kiyi hakuri Nanee inshallah komai zai wuce mu dage da Addua tace na gode yanzu naji labari Mijin namu ya dawo shekaran jiya muje na gabatar dake.

Mun Shiga cikin part din Palo Palo kafin mu Isa inda yake,kishingide na hango farin Dattijo me Kamala da haiba,Wata dattijuwa Baturiya wato Amarya Maryam Maman su Ice tana gefensa tana bashi abinci Yana ci,itace take ciyar da shi kunya ta kamani Amma Naga su ba ruwansu, ganin Asiya sai ya hade Rai kadan yace Ify ya akayi? Muka zube a kasa tare da gaisheshi da sakin fuska ya amsa Mana,tace me min girkice Ni da Ice sunanta Fadila na kawo ta gaisheka, kallona yayi kadan yace na gode Allah ya taimaka kuje kawai, Amarya Maryam ta hade Rai ta

zuba min tsaki tana min mugun kallo da hausarta wacce Bata iya sosai ba tace Ana kwace min yaro na kamar uban wanine ya aifa Mani shi, wlh Ana ta kashe min yaro sai nayi daure ku gaba daya.

Mu dai Shuru mukayi dariya hausar Tata ta bani kawai muka wuce,sai part din Karimatu uwar gida Nan fa muka Sha matsiyacin kallo ita da yaranta ko kallo bamu ishesu ba muka tafi, part din Amarya tana wajen mijinta sai kawayenta da Yan uwanta muka gaisa sama sama suna dauke Kai muka fito sai part din yaran dangin Me gidan Nan fa Naja wacce ake kira da Cilla tace hmm Yar aiki da kwalliya ayiriri , sadiya misisi tace Ni Misisi Naga ta kaina Wai Nanee daga kauye take Haka? Ahayye dukkan Yan Matan suka saki shewa, Shehu Niga yace gaskiya Naga budurwa in da kasan kuluwa tsohuwar budurwata ta kauye, Nanee tace zaku ci ubanku wlh wannan tafi uwar kuluwa ma,Kuma Kar naji wlh kun sa Mata Sunan banza nasan halinku Yan iskan kauye da ance anyi sabon bako yanzu zaku kalleshi ku sa masa Sunan banza.
Dariya sukayi gaba daya.

Bayan mun fito Nanee tace yaran Nan Yan iska ne in kika zauna dasu cikinki zaiyi ciwo ranar Friday gaba daya Family suke Zama ayi Hira aci a Sha zamuje dake kici dariyar su Cilla, ko Ice da baya dariya watarana Dole suke bashi dariya.

Murmushi nayi nace wato su suke sawa mutum Sunan banza? Nanee tace duk sune suka radawa kowa suna har Dr Who.zai wahala kema Basu Sa Miki ba.
Murmushi nayi kawai Haka muka Gama zagawa gulmata ko Ina ya dauka a gidan,breakfast din Dana shirya Naga an cinye komai,nace Nanee waye ya cinye? Tace Ice ne kin San na ebi nawa na bar Masa nasa,nace to Ni me zanci banci komai ba,Wannan kinfi kowa Shirme kiyi girki da kanki ki kasa ci,Kitchen na koma na hada cornflakes da Madara Nasha abina a kitchen din masu wanke wanke da shara goge goge suka fara aikinsu.

Dakina na koma Nasha bacci na har 12:40pm Nanee ta turo me aiki ta tasoni na daura girkin Rana Ice ya fara Kiran waya,a firgice na mike Ina magagin bacci kaina na daurawa wani Dan gyale kawai nayi waje Ina tafiya Ido a rufe ji kake Kum munyi karo da wani,kamshi ya cika min hanci ban bude idona ba na kauce Zan sake hanya naji yace what...Fadila kece a gidanmu Oh My God,Muryar Dr who naji na bude Ido na kalleshi tar na saki Murmushi gani nayi kamarsu daya da Dan Bature na bangale Dan bakina na saki Ido Ina kallonsa nace Nanee yanzu nakewa aikin abinci na dawo Nan,oh dazu kece me kamshin girkin da muke ji? Munci abincin nida Ice wlh bamu taba cin girki me dadin naki ba bakiji yanda Ice ya dinga Santi ba.

Murmushi nayi Nanee tace ya kika tsaya kin sanshi? Kai na daga Mata tayi Murmushi sabo da kowa yasan idan Dr who yayi iskanci da mace to ita ta amince bayawa mutum Dole, yace Nanee ta window din gidan Ijeoma ta sanni wannan ta gari ce karki ji komai,dariya Nanee tayi tace see u na sani Malam, kan uba wani azababben kamshi muka ji na fitar hankali wajen dadin Shaka,ban San sanda na lumshe ido ba, wani ne kamar aljani sabo da haduwa sai da na kusa sumewa sabo da Jarabar haduwarsa, can Naga Yana sakkowa daga sama yasha kyau cikin wata shadda me tsananin kyau dinkin da kadan ya wuce gwiwa,wandon pencil na shaddar kun

san dai maza yanzu Suma fitted ake damesu, hannun links ya Hadu ya Hadu,sumarsa me yawa baka me santsi tana sheki yaci uwar wani askin Wanda ya take na Dr who haduwa.
Tafiya yake cikin wata Izza takama da gadara fuska ba Rahma,waya yake dannawa wata iri Ni ban taba sani da irinta a duniya ba, komai Fari har takalmi, Dr who naji yace Aljani na Nanee kaga Ice sabo da sanyin zuciya wannan uban kyau Ina zaka je Haka kamar yau za daura ma aure? Kansa Yana kasa Yana latsa waya na kafeshi da Ido,dariya Nanee tayi tace Dana kenan tamkar da dubu ga kyau ga iya wanka,gadanga kusan yaki,kainuwa dashen Allah duk Wanda yace bashi ba,Dr who Yana dariya ya Karasa min nace mishi shima ba shi ba Nanee.

Dago da kansa yayi ya kalli Nanee yayi Murmushi kadan yace da shagwaba Nanee pls Mana,ba shiri na kwala ihu nace Yeee wlh Allah Danbature nane,na rantse da Allah shine Mijina,na dira tsalle na dirga a gabansa na tareshi na tallafi kumatunsa da tafin Hannuna na saita fuska ta a tasa na tsura Masa Ido na sakeshi naja baya farin ciki ya mamayeni,nace Nanee wlh na San wannan Mijina ne Aliyu sunansa tun Yana mahaukacinsa,sanda yayi Ciwon hauka aka daura Mana aure a kauyenmu mun kwashe wata 9 muna tare Allah shine.

Nanee tace ke...ta daka min tsawa Ashe Baki da hankali?yaushe wannan ya taba Ciwon hauka wlh na rantse Miki Bai taba barin gida ba ta sanadiyyar hauka ba face kasar waje da yake Dan zuwa,tabbas sunansa Aliyu Hydar Amma bamu sanshi da Ciwon hauka ba,sai wani kika sani,wannan Bai taba aure ba.

Dr who yace na Dade Ina zargin ke mara hankali ce a cikin masu hankali wlh tun sanda kike min magana ta window yau na tabbatar Baki da hankali wannan Zaki ce ya aureki Dan son Abin duniya,ihun danayi yasa Yan Mata da samarin gidan dake kusa shigowa inda muke sai ji nayi hhhhh sun kece min da dariya sunce anga kyau da kudi za ace mijinki ne ta Ina? Lallai Yar Nan Makira ce,oh wato anga banza ko? Naja Cilla tace mun San mutan kauye da wayo muma daga can muke,dariya ake ta yi  min shi Kuma Wanda nace Danbature ya daskare a tsaye Rai bace ji yake kamar ya kashe Ni sabo da haushin na taba Masa fuska ya tsani mace ta rabe shi.
Idonsa yayi jajir Nan take ,Murmushin takaici yayi dimple dinsa ya lotsa nace Yeee...gashi ..gashi...billahillazi la ila ha Illa huwa Danbature nane,ka tuna ta kauyen Dingawa can Gombe wacce ka Mara lokacin hankalinka ya dawo jikinka kayi tafiyarka bayan ka min duka? Galala ya tsaya Yana kallona,na washe Baki nace pls ka tuna time din wani me machine ya kaika birnin Gombe motoci da sojoji suka daukeka?

Mamaki ya kamashi ya harde hannayensa a kirji Yana kallona shifa Bai San komai ba,nace akwai ma zobe da agogonka suna wajena Amma na barshi gidan Attine watarana Zan dakko na nuna ma wlh Allah kaine,Kuma wlh Ni matarka ce da igiyarka a kaina uku.
Kowa abin ya daure Masa kai.

Ni kuwa na dage nace gashi gashi komai na gane kaine,kune baku Sani ba Amma wlh yayi Ciwon hauka lokacin da ba Wanda zai iya rabarsa Ni na sanshi na soshi na aureshi na zauna dashi,Nasha wahala wajen iyayena akansa Amma na jure sabo da sonsa da nake wlh badan kudi na soshi ba,lokacin da na soshi ko mahaifiyarsa nasan baza ta rabeshi ba a lokacin Ni

kuwa na yarda na soshi....Gau......naji an zuba min mari Ni kike cewa Mahaukaci? Yaushe nayi Ciwon hauka Dan ubanki kika Kuma fada sai na yankaki,kinji na rantse Miki ba Ni bane yar iska ki nemi mijinki mahaukaci, banyi Shuru ba Ina kuka nace wlh kaine,Kuma da kasan ko Ni wace a wajenka wlh baza ka soma daga min ko yatsa ba bare ka mareni,Kuma Kaine Nan Mahaukaci da Aliyu Hydar Sulaiman da Kai aka daura min Aure,mamaki ya kashe su tunaninsu hada sunan kawai nayi sabo da naji sunansu yanzu Zan cucesu.

Dariya suka dinga sheka min Ana ganina mahaukaciya har Nanee,kitchen Danbature Wanda suke cewa Ice Naga ya Shiga ya dauko kwandon tace taliya yace ki tsaya yanzu zamu gane tana da hankali ko a'a?

Kwandon ya Mika min yace ungo na karba yace ebo min ruwa a ciki na gani Wai ta haka zai gane haukata Babba ce ko karama Murmushi sosai na kalleshi sonsa ya Kara ninka na baya nace lokacin da muke soyewa muna Shan love da Kai kana Mahaukaci ai Ni ban ma Haka ba,marina yayi sosai me zanci dake zakice munsha uban love Dan uwarki.

Murmushi nayi nace ku sani Yan gidan Nan wlh Ina da auren Aliyu Hydar Sulaiman Kuma har kwanciyar aure munyi sau daya Banda romancing din juna da muke tun Yana kazaminsa mahaukaci lokacin Bai iya komai na duniya ba.

Dariya aka Kara dauka harda ihu Ice duk tsanar Mata da yayi baya kula kowa yau gashi ance har kwanciyar aure yayi Wai da ita Yar aiki, idonsa jajur yace Ni Virgin ne Dan kan ubanki, nace wlh karya ne ba virgin bane Kai an taba yi ye wullu..plate din tangaran ya dauko zai kwada min, na sheka da gudu Bayan Nanee nace daga fadan gaskiya ta Bayan Nanee ya damko ni na bige plate din ya Fadi ya fashe Ina ihu nabi ta saman kujera ya biyo ni,sabo da tsokana nace Ina gudu da Haki,sau nawa Ina maka wanka tas, kullum sai na maka wanka kana cewa My love Nan Bai fita ba a wanke can,ihun dariya Yan dakin suka Sa,naja Cilla harda tsalle Dan dariya,Nanee tace tunda bakya ji ke dashi ta haura sama tana Naga abin naki tsokana ce.

Har ya kamo rigata na koma bayan Dr who Wanda ke dariya ganin ba Babba a Palon Ina haki nace kasan lokacin gajeren wando ma Ni nake sa maka,Mika daya ya damko Ni ba Wasa sai da na Sha Mari yafi biyar fuskata ta kumbura,ya sameni da wayar charger jikinsa na rawa babu Wanda ya ceceni ya Zane fes sai da ya farfasa min jiki, Ina ta kuka a hakan ma saida da Dr who ya karbeni da kyar.

Yace wlh in kina Wasa ki daina kaf gidan Nan tsoronsa akeyi baya Wasa da kowa zuciyace dashi zai iya halakaki ba ruwansa,yanzu da kike gani ba hucewa yayi ba ki kiyayi haduwarki dashi anjima ko gobe.

Nanee ce ta gasa min jiki tasa aka kaini asibiti duk inda Naga wani ko wata Yan gidan sai su kwashe min da dariya,tsoron Dan Bature ya kamani bama naso ko a hanya na ganshi Amma sabo da sonsa yasa nake labewa na dinga lekensa,abincina ma tunda yasan nice ya daina ci a part din Asiya Nanee,da kyar ta bashi hakuri ta lallabashi ya dawo Yana Dan karba yaci.

Nanee tace karki Kuma zuwa inda yake wlh dukan da zai Miki sai yafi na baya,Haka ban Kuma Bari mun hadu ba tsoronsa nake ji kamar malaikan daukan Rai.

Har na koma makaranta ban ganshi ba,yau Tuesday Bayan na Gama aikina na shirya cikin Riga da skert na lace takalmi da jakata iri daya da mayafin duka peach color lace din blue and peach nayi kyau Amma banyi wata kwalliyar kirki ba,Nanee na sanarwa tace naje driver ya kaini,ganin Yan gidan Basu da mutunci nace a taxi zanje,ta bani kudi tace kin huta jawo min magana,karki manta 12pm Dole kizo kiwa Dana abinci,nace ba damuwa na tafi.

Na makara 8am nake da lecture Amma Yanzu har 8 din tayi,da gudu gudu sauri sauri na fito Haka ta compound na fito, Ice ya fito cikin daukan wanka yayi kyau iya kyau sanye cikin kana Nan Kaya kyau dai ba a fada Yana kamshi,Ina ganinsa tsoro ya kamani na koma na labe Dan kar ya ganni Ashe ya ganni ya tsaya jikin wata dalleliyar motarsa yaki tafiya Nima na gaji gashi Zan makara,na fito Ina lallabawa Zan fice yacewa wani Soja ya dauko Masa Ni,sai ji nayi an sabani a kafada,kuka kawai na fashe dashi Raina ya baci da aurena Kato ya daukeni,nace wlh Ina da aure Bazan yafe ba cin zarafin aurena da akayi,a gabansa aka dire Ni na zube a kasa jikina sai rawa yake nace da aurena wlh kasa za a ci min zarafi,yace oh yanzu ma Zaki ce Ni mijinki ne? Da sauri tsoro yasa nace A'a karya nake Kai ba Mijina bane,kayi hakuri ka yafe min, fuska ba Rahma ya kalleni shekeke yace to a gaban kowa Zaki tonawa kanki asiri kamar yanda kika yi wancen lokacin,kaina a kasa hawayen so Yana zuba nace na yarda Amma don Allah ka Bari na dawo daga makaranta da yamma,mamaki yayi yasan babu Yar aikin dake zuwa makaranta sai yanzu yaji yasan Islamiyar Saturday Sunday ta gidan kawai sukeyi.

Kina Yar aiki har wani schl kike zuwa? Nace ae Mana University ma kuwa Yar jamia ce ni level 2 nake Health education, Minister Ijeoma na taba aiki a gidanta itace take biya min kudin Niclos University me tsada sabo da kyan halina take biya min,Kai ya jinjina naso na bashi dariya harda yabon kaina Wai sabo da kyan halinta ya furta a ransa,sai da ya Gama ji yace to ubanwa ya tambayeki Dalla bace min a gani kafin Raina ya baci na halakaki.

Jikina na rawa na mike da sauri na fice daga gidan Ina godewa Allah Bai min komai ba,da gudu gudu na nake tafiya ina so na Isa titi na hau mota,rantsatsiyar motarsa na gani tana slow a titi driver na jansa ya kame a baya Yana Danna waya,Driver dinsa ya ba Umarni yace tafi ka kwashe min yarinyar can da mota,Driver yayo kaina sosai da mota,na kauce ya bini again na kwashe da gudu ya biyo Ni zai takeni da mota Naga wata waya an zagaye wani garden da ita na Kama wayar na daka tsalle na haure na rufta ciki wayar ta yankeni a kafata sosai jini na fita,ban sani ba a ciki Ashe kusa da miciji Kato na fada ya kafta min Sara a hannuna.

Da gudu na Kara yo tsalle na fito waje ban tsaya ta wani yankan waya ba,ihu na saka kawai nabi titi Ina miciji ya cijeni a kaini asibiti,shi kuwa mugun yayi tafiyar sa,taxi na tare na fada da turanci na fada wa Driver me taxi miciji ya cijeni ya kaini asibiti kawai.

Nan take nacewa Driver sunana Fadila,a gidan Sulaiman Araba Lagos nake aiki,Ina da Aunty na Attine can Ojeota layin Babatunde 14no house, na rubuta Masa number ta Attine data Nanee nace ko da zan mutu ka Kira wannan Number.

Da gudun tsiya ya kaini wani katafaren Hospital yace miciji ya sareni Nan take aka bani

agajin gaggawa na treatment, suka bani gado sannan Driver Yoruba ya Kira Number ta Nanee ya sanar Mata,ya sanarwa Attine,sai ga Attine tana kuka tazo, lokacin Ina bacci sai ga Nanee da zugar motarta biyu itama Nan ta biya kudin magani da komai,sai dare na farka Naga Nanee da Attine Sunyi tagumi.

Attine tace garin Yaya Fadila na Basu labari harda kuka na,Nanee tace ai ke kika jama kanki na fada Miki kar ki kulashi, Attine tace Ice dinne Haka dama yake? Nanee tace ita ta tsokaneshi, kuka na fashe dashi nace Ni na fasa aikin wlh tafiya wajen Attine zanyi,Nanee tana dariya tace bazai sake faruwa ba kiyi hakuri,Attine tace saida na Baki Ibr ai halinki ya jawo,Bayan an sallameni Nabi Nanee muka koma gidan Bayan Attine ta ja min kunne sosai na fita hanyar kowa.

Washe gari Haka na fito zan tafi schl na Kara ganinsa yayi Shirin fita cikin wasu kana Nan Kaya Yan gaske kamar Bature, Ina so na kalleshi naji sanyi a Raina Amma na kasa sabo da tsoro nayi tafiyata sum sum na fice,da mota ya fito yau shike driving tun Bai kusantoni ba na fada can kofar gidan wasu na bashi hanyar Amma sai ya tsaya da mota ya cuno min wasu karnuka suka yo kaina kamar zasu ci babu, tsoro yasa na watsar da hand bag Dita na take da matsiyacin gudu na fige dankwalina na jefar karnuka biyu suka rufa min baya, Allah ne ya kawo Dr who ya Hangoni ya fito da mota Ina kukan masifa ko gama tsayawa baiyi ba na afka motar sa.

Da kyar ya rike dariyarsa yace sannu me aure Mijin nakine? Harararsa nayi nace malam jeka dauko min mayafina da dankwalina Ina matar wanka ka rainani,Yana dariya ya fita ya dauko min har jakata ya dawo har schl ya kaini.

AsmaBaffa
[8/15, 11:45 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

26-30

Official

By
AsmaBaffa

HADIZA MUKHTAR,MOM INTEESAR,STYLISH ANGEL,AUNTY SUMEE,FATEEMAH ZAHRA.
ga page naku 👍🏻😍

12PM na bar lecture na dawo gida, Nanee na tambaya me Zan dafa tace na Masa pounded yam da miyar kwai, sai farfesun Kaji,sannan na hada juice kala biyu,Ice baya son abinci barkatai yaci wannan yaci wancan,ban dau dogon lokaci ba na Gama tare da gyara kitchen,na fito Ina shirya Dinning Naga Ice da tafiyarsa ta Izza,tunaninsa Ina schl, ko kallo ban isheshi ba ya wuce, wani sonsa ya taso min na bishi da kallo tare da share guntun hawayena na tausayin kaina.

Wurin Nanee ya wuce Ni Kuma na koma room dina na fada saman bed sai da naci kuka na sannan nayi wanka na sake sabon shiri cikin doguwar rigar material,nayi rolling mayafina cikin mutunci da Kamala,na dauki hand Bag Dita tare da fesa turare kadan na fito zanyiwa Nanee sallama na gansu saman Dining ita da Ice suna ta kwasar girki na me dadin tsiya.
Cike da damuwa na duka kasa kusa da ita nace Nanee Zan koma schl, Murmushi tayi tace to kinci abinci dai ko,karya na Mata nace naci Amma damuwa baza ta Bari na ci ba.
Tace to a dawo lfy ta Miko min dubu biyu ki Kara kudin taxi nace A'a akwai canjin dazu sun isheni Har gobe Nanee,

Aransa Yana ji yace shi Kam tunda ga kan danginsa zuwa Yan aiki Bai taba ji a gidan an bawa mutum kudi yaki karba ba,har ma yace akwai ragowa sun Isa Haka, sai yau da yaji a bakin wannan baiwar Allah me kiransa da mijinta.

Ina ta kallonsa na shagala Ba tare da ya kalleni ba naji yace an dameni da kallo fa, Mikewa nayi kamar kwai ya fashe min a ciki na tafi schl.

Da dare Nanee ta sameni har dakina tace Fadila? Nace naam ki daina kallon Ice a mijinki,karki nuna ma kin San me kama dashi,wlh Baki San gidan Nanba sai Nan gaba,uwarsa Bata kaunar talaka,idan taji kina shige Masa ko wani Zancen mijinki duk da ba gaskiya bane,zata Sa a koreki a gidan Nan,ke zata iya salwantar da rayuwarki ki rike kome a ranki ba ruwanki,a gidan Nan Ni ba kowa bace kin ma gani da idonki,kudin kashewa,sutura da komai yanzu ba me gidan ke min ba Ice shine ke min kome nake so.

Ki San me kike ki dawo hayyacinki, Kaina kasa nace Inshallah Nanee bazai sake faruwa ba,tace Good kallo me tsayi karki Masa baya so Kuma uwarsa idan ta fara Jin jita jita ke zakiyi kuka da kanki.
Inshaallah na gode,ta fita na zube a kasa na rushe da kuka, ganin za a jini na wanke fuskata nasa Hijab nayi waje can Garden na Samu inda ba kowa na saki kuka na,idan na tuna Wai Dan Bature Bai sanni ba sai na Kara fashewa da Kuka me Sauti,na Kara barkewa da kuka,na kwanta a kan grass carpet na tuna  yanda nake matukar sonsa,Kara tsagewa nayi da kuka na dinga burburwa Ina birgimata da Shure Shure kamar Zan mutu.

Tsawa naji an buga min ba shiri Jin Muryar Dana sani Ice ne nayi duf lokaci daya,ban ko kalleshi ba na tsaida hawayena,na goge fuskata na juya na kifa cikina nayi kwanciyata, kafin

kace me bacci yayi awon gaba Dani a wajen.

Wajen Nanee ya wuce yace Yar aikinta mahaukaciya Nanee tace ban son sharri fa,yace yanzu na Gama tabbatarwa ya dinga Bata labarin yanda na dinga kuka da burbuwa,Nanee tace to meke damunta?Baki ya tabe yace harfa ihu da burbuwa takeyi aljanu ne da ita.
Nanee tace kyaleta na gaji da matsalarta.

Na tsawon kwashe 3wks a gidan na Dan Saba Amma bama muamula da kowa yau jumaa yaune Kuma ake hallara a wani Palo hadadden kamar wani hole yasha alatu Bayan an sakko daga masallaci kaf gidan manya da Yara zasu hadu a palo,ko wanne da Yar aikinsu daya me dafa musu abinci tana kawo musu abinda suke so,Nanee da Ice tare da Yan uwanta da yayanta nice me kawo musu ko me suke bukata, duk part me dafa abincinsu days zata zauna a Palon.
Nima na Gama dafa duk abinda Nanee tace Ina da lecture Amma ba yanda zanyi Dole tace na hakura ba a tsallake ranar jumaa.
Duk mukamunka sai ka zauna a gida a wannan Palo,Daddy ya koma kasar wajensa business,Hajjo kakarsu taci kwalliya tana Palo da masu Mata tausa da me girkinta,Haka Karimatu da Maryam Amarya ko wanne da iyalansa.
Ice ne kadai ke bangaren Asiya Wanda uwarsa sai haushi take ji an rabata da danta,Yan Matan dangi kaf da maza suna Nan an hallara,Naja Cilla tace yau akwai labari me zafi yau kuma zamu bawa Fadila suna Nickname, Ina gefen Nanee nayi Shuru, Ice Yana can baya kan lumtsumemiyar 3seater Yana latsa waya.
Ni tsoronsu ma nake ji duk sun Sa min Ido,wata Jamila Ana ce Mata jummala tace tunda tace Ya Ice ne mijinta Sunanta matar Ice ko ya kukace, Yar lalle tace Dalla matsa ai iyayi gareta Wai ita ta waye,Hajjo ta tabe Baki tace tana bangaren Asiya ai Dole ta gaji iyayi.
Shehu Niga yace Allah tana Kama da budurwata Kuluwa ta kauye na fada muku gani kuke karya nake,Ni dama zata aureni,sai tafi raf raf da dariya,Ina jinsu suna ci min mutunci.

Karimatu tace Kai kun cika Mana kunne kufa Yan iska ne,Salihu Boy kaninta yace Aunty masifa munyi Shuru Nan suka ce heee suna dariya,Nanee tace kawo Mana juice sharesu, na mike Wata a ciki Ana ce Mata Shekara tace Ashe akwai Dan shape inye Nan ma sai dariya,Raina yayi matukar baci na kasa hakuri nace ke dakata kucaka da igiya har uku a kaina ta aure,karki Kara kalamai irin wannan wani Ina da shape salon wannan kartan mazan su dinga kallon tsaraicina suna hadiyar yawu suna kissima Abu a ransu zuciyarsa na darsa musu bad Abu a kaina.

Chakwas tace iyye waye saanki a Nan wlh sai muyi Miki dukan tsiya,na kalleta naja tsaki nace Wanda Bai fasa ba Baya kaunar Allah,karku ga nazo aiki gidanku wlh na fiku gata da asali halak nake nema, Iyye cewar Karimatu da suke Ce Mata Umma ta fara zazzaga min masifa da cin mutunci,nace kija mutuncinki Umma Dan Nima na gaji Masifar Nan Dan uwata data haifeni ta fiki balai,muguwar Masifaffiya ce babata da anan gidan take da tuni ta Cinna muku wuta kun Kone kurmus, hhhhhh aka dauki dariya kowa Yana kyakyatawa har Nanee sabo da yarinta da kuruciya Dana nuna, Ice Yana ji Bai San sanda dariya ta kwace Masa ba,Dr who harda rike ciki yace in Banda kuruciyarki Fadila Kya Fadi mummunan halin ummanki,Kinga yanzu kowa yasan

Mum naki da halinta.

Tunani nayi Naga Haka ne ai nace to ai dai tana da kirkinta Kuma ma...ma ai Abbu dina baya so na har wajen Yan Hisba na Kai kararsa amma Hajiyarmu sabo da kyan halinta itace take so na,Nan ma sai dariya Chakwas tace Abu ya lalace babanki kika iya kaiwa kara,? Na Galla mata Harara to ai da dalili malama Dan kawai Ina bin Mahaukaci akace zai min ciki sai dariya kyalkyalkyal kowa dake Palon har Anty Amarya da Bata dariya yau tayi,Hajjo tace wannan yarinya kuce kawai masifa aka dauko Mana gida ba na gari bane.

da sauri nace A'a ai mahaukacin na aura na Kai Babanmu Kara Dole aka aura min mahaukacina aka bamu gida aro, Umma tace uhm Kuma ya kukayi rayuwa na zauna nace hmm ai Ina sonsa, nice Nan nake Masa wanka da komai na sa Masa Kaya,ke in kin ganmu abin Sha'awa, baya magana, Shehu Niga yace Dan Allah fa nace Allah da zaku ji labarin sai kun tausaya min kunyi kuka sabo da tausayi, Cilla tace mun shirya maza Gama aikinki ki bamu musha nace to.

Da gaske kowa ya matsu yaji labarin, na Gama aikin na dawo da yake gulma ce harda tarairayata,na zauna Hajjo tace matso kusa Dani nafi ji,shi kanshi Ice daina danna waya yayi ya zauna zaiji labari auren Mahaukaci.

Labari na fara Basu tun farkon ganina da mahaukaci, har wahalhalun Dana ci a kansa,har aure da rayuwarmu ta aure,har sanda ya Dan dawo hayyacinsa ya tafi Bayan naci duka.

Kafin na Gama na jike da Hawaye jagwab, su Cilla da Misisi har da kwalla,Hajjo kanta tayi kwalla,Nanee harda kuka wiwi,tace Dole maza su dinga Miki gizo kowa kika gani kice Danbature ne, Ice Kam yaji tausayina matuka Yana tsinewa Danbature a ransa yayi butulci.

Anty Amarya Baturiya sarakan love tace Mazaje gasu Nan everywhere ki canja shi ga masu kudi wa yake ta wani talaka me Mahaukaci.

Nanfa suka lakaba min  DanBature suna na, Karimatu kuwa marar Imani cewa tayi ke Dalla makaryaciya kawai ki shirya Mana film wannan ai film ne Ina Haka zai faru.

Shuru nayi musu kawai  nasan ba yarda zasuyi Dani ba,Dalilin da yasa na Basu labari ko Allah zai sa Danbature ya gane Ni ko Yan gidan su a samu a fayyace gaskiya Amma Shuru basu San ma ya taba wani Ciwon hauka ba,shi kanshi ai da zanga alamar ya gano gaskiya Amma ko Alama.

Bacin Rai yasa nace Nima yageshi zanyi a Raina kawai nayi rayuwata an daina auren ma.

Shekara tace Hajjo yaushe Daddy zai dawo next month birthday na,gwasaleta akayi tsohuwa dake 35yrs mun gaji da party sai na aurenki, Haka na kawo abinci iri iri masu arnen dadi,Yan aiki Suma Ana ta kawowa tunda suka ga kalar abincina sukace sai sunci, Nanee tace suzo su eba kafin kace me an cinye nawa ko Danbature Basu ragewa ba, nasan Kuma yunwa yake ji, Allah yasa na ebi nawa na ajiye iri iri nasan zai isheshi,masu gyara Palon sun kwashe komai sun gyara Ana ta santin girki na,Naja Cilla tace Dr who Kuna cin dadi Yar kauye da iya girki Haka Wai. Babu Wanda ya kulasu, Danbature yunwa tana ta kwakule Masa ciki ya tsaya yanga,komawa nayi na dauko Masa nawa na jera su a wani hadadden tire komai da nasa na

musamman ne abin kallo na kawo na ajiye a gabansa Yana kwance sai latsa waya yake, serving dinsa nayi sai kallona sukeyi wasu suna cewa iyayi wasu na tabe Baki.

Nanee kuwa taji dadi Ashe na ajiyewa danta nasa daban, sai gadara yake zubawa da kyar ya zauna, ya cinye shi tas kuwa, 5pm aka fara watsewa daga zaman Palon na zumunci.

Yau Saturday abin ya bani mamaki Islamiyyar yaran gida na gani har maza da Mata manya da Yara,kowa ya hallara Banda DanBature, Kuma duk cikinsu ba Wanda ya Gama izu goma a schl din kawai Danna waya sukeyi da laptop basa fahimta.

Yan aiki ma ga tamu kusa da tasu.

Ni na wuce Izu arbain Karina daban ne,littafan Addini da dama na iya,na tashi Ina rero qiria ta dukkan Yan Matan da mazan hankalinsu ya dawo wajena sabo da kwarewa ta da Kuma dadin muryata, Danbature na hango zai fice na tabe Baki shi yasa Bai iya addini ba lokacin da yake Mahaukaci Ashe Bai San komai ba, da Asuba ake tashin kowa a cika masallacin gidan sallar Asuba har Mata.

Yau da Asuba Ina magagin bacci na fito.

Komai duhu Dole na gane Danbature ya fito da jallabiya harda carbi a hannunsa,a Raina nace kamar gaske ba a San ko fatiha ba, a hankali na labe kusa dashi jikin masallacin a hankali na canja murya nace ba virgin bane, juye juye ya kama yi Yana neman Ina yaji ko kunnensane, na Kara cewa ba virgin bane,ya Kara waige waige Amma ba kowa,tsaki yaja yaci gaba da Jan carbinsa kafi a tayar da sallah, nace kauyen Dingawa Gombe state kana da Aure.

Tsoro abin ya bashi ya rasa waye da sauri na bar wajen na shige masallaci ta baya.

Bayan an idar da Sallah ya Gama laziminsa ya fito na Kara labewa a kofar part dinsa sabo da karfin Hali a hankali nace ba Virgin bane...da aurenka dube dube ya fara na tsorata Naga ya wuce sama,na fice da gudu na koma part dinmu.

Sabo da mugunta yasan Ina da lecture yau Monday sai yace Nanee ki tura Wannan Yar kauyen zata gyara min Office dina,wace Kuma Yar kauye? Nanee ta tambaya,mahaukaciya Mana cewarsa,Nanee ta kalleshi kawai tace ba ruwanka da ita, 1pm na Gama girki na na shirya komai Nanee ta fito cikin kwalliya tace shirya abinci a basket driver zai kaiki office din Ice Zaki gyara Masa me aikin ya koreta Wai kafin ya samu wata.

Ba yanda na iya na sa hijab Dina Kato na dauki basket muka tafi,na kwankwasa Masa Kofa ya Dade kafin yace come in,Ina Shiga wow sanyi da kamshi ya dakeni,katon Office ne ga table dinsa da kujera tana juyashi takardu a gabansa,gefe Kuma Palo ne na Alfarma yasha kujeru babu wani dirty, Ina yini na gaisheshi hannu kawai ya daga min .

Yana Shan tea Yana ta rubuce rubucensa na wuce na zauna a palon,inda aka tanadi kujeru lafiyayyu Yan gaske,kallon Office nayi tsab ya gaji da haduwa, wani maaikacin ne ya kwankwasa Izini ya bashi ya shugo wani saurayi matashi Kyakyawa shima Dan gayu, tafawa sukayi yace Kai Dan iska ka share mutane bikina fa saura 3wks Zan barka a gwauro, Aliyu ya kalleshi cikin nutsuwarsa  da Izza Bai ce komai ba yaci gaba da aikinsa, ban son rashin mutunci zanzo har Office naka kana min kallon da ka Saba, kayi wani Shuru dama ka Saba yi Mana haka,Me kake so nace maka Allah ya kaimu musha biki Omar.

Wata hirar suka sake,Ni kuwa Ina gefe Dadi nakeji gani kusa da Danbature shi yasa nayi zamana Ina satar kallonsa,zuciyata tana sanyi Ina Jin dadi.
Mikewa nayi nace na tafi sum sum Zan fita yace hey.. come back stupid girl,wa zaiyi serving na ko Nanee Bata fada Miki yanda nake ba, Omar abokinsa yace wanna me kyau Haka kanwarka ce,badan an Sa min Rana ba ai wlh canjawa zanyi na aureta, karaf nace malam Ina da aure,ke Dalla shut up wani kina da aure mahaukaciya Hospital Zan kaiki sai anyi Miki gwajin kwakwalwa cewar Masifaffe Dan Bature.

Omar yace to fa Kai matar wani kake wa tsawa? Na tabe Baki nace Kai ai shinefa...cike da balai yace shinefa ubanki wlh Zaki jawo na Miki mugun duka, kallon Omar yayi a hasale yace Malam tashi ka tafi gidanku zanzo da yamma,au korata kayi? Ae Jeka.
Yana fita manager dinsa ya shugo suna ta aikinsu,Yana fita Secretary itama tazo,Bayan ta fita wani yazo da kudade a shirye cikin kwali, ka rantse macaroni ne, waya ya daga ya Kira Daddy suka Gama maganganunsu a waya na wajen business, wani ya Kira a waya yace ya Kai kudin bank.

Mikewa yayi Yana mikar gajiya ya bude wani Room Wanda hadadden bedroom ne ciki toilet ya Shiga yayi Alwala ya fito a bedroom din yayi sallah,Ni kuwa yau bana sallah period nakeyi,na matsu ya barni na tafi sabo da rushing yake min Kar na baci Allah ma yasa na taho da pad a hand bag Dina.

Fitowa yayi Yana Izza  tsakiyar Centre carpet ya zauna yana latsa waya yace serve me,ban San me yake so ba na bude nace wanne ya nuna abinda yake so na zuba Masa komai a plate biyu sai juice Amma kadan Yana da Saurin cin abinci Amma baya ci da yawa,a Raina nace oh halayensa ne Zama a kasa tun Yana Mahaukaci ma.

Ya fara ci a ransa Yana Jin dadin girki kamar me Amma baya ko nunawa ma, Bayan ya Gama ya Kira maaikatansa masu aiki karkashinsa suka dauka abincin suka tafi ci sabo da tunda na fara girki suke maitar abincin sabo da dadin girki na.

A kasan carpet ya kwanta Bayan ya Dan jira abincin ya tsirga Masa,idonsa ya lumshe yace jeki fara aikinki ko ina ya Zama neat, ta bedroom na fara da toilet suna sheki da kamshi na fito nayi Wurin Table nasa da komai har na karaso inda yake kwance Yana bacci,tuna baya nayi baya so yana bacci a tasheshi a Raina nace wancan daban Danbature wannan daban Aliyu Ice,
Tashinsa nayi nace zanyi shara ka koma bedroom, ya mike kuwa ya koma bedroom ya kwanta yaci gaba da baccinsa har na Gama ko Ina Yana kyalli da kamshi,na zauna ina jiransa.
Ya Dade sai 4pm ya tashi yayi Alwala da sallah sannan ya fito, ganina a zaune yasha mamaki,Ni kuwa searching girki nakeyi Ina koya a YouTube yace ke Wai bakya sallah ne? Ae kawai nace yace kanki tashi ki barmin Office.

Har na bude kofa yace ke dawo na dawo na tsaya gabansa Ni haushinsa nake ji yaki so na ya mantani, yace bani Detail na Mijin da kika aura Mahaukaci ya gudu ya barki Naga kin

haukace kema so Zan taimaka nasa a bincikoshi duk inda yake a fadin duniya.

Dariya ya bani ga mutum Amma yace ba shi bane,a Nemo shi mu gani,a fili nace Sunansa Aliyu Hydar Sulaiman da Haka aka daura Mana aure,yasan sunana Fadila,sannan kirarsa da komai irinku daya, kauyen da kika zauna dashi?, Nan ma na sanar Masa,Ina Agogon nasa da Zobe da kika ce nasa ne kina dashi? Nace ae jiya naje gidan Attine nace ta bani na karbo gasu a jakata,Ina murna ai yanzu Danbature zai ganeni nice Matarsa,na kwaso jikina na rawa na Mika Masa su,Abin mamaki juyasu ya Shiga yi ya Kare musu kallo sai ya tabe Baki yace wannan ai trash ne kina wani kalli agogo tsoho dashi haka Danma na diamond ne ga wannan kazamin zobe, sa min su a Leda Kar na dauki cuta, Jin abinda yace ya tabbatar Bai gane komai ba.

Kuka me Sauti ya kwace min banyi shiri ba,Baki bude yace ke Wai wanne mahaukaciya ce ne,wannan shi ya manta da ke Bai sanki ba Amma sai cutar da kanki kikeyi kina Masa kuka,wanne so kike Masa Haka? I pity u wlh, soyayya irin Haka a Mahaukaci ke ko kema ya goga Miki cutarsa ne? daga na kushe agogonsa Zaki Fara kuka, to shike Nan me kyau ne agogon ga tsada sun hadu ba kazamai bane ok? Ya furta Yana dage min gira ban San sanda na Kama dariya ba yanda ya fara lallashina,da mamaki yace Allah ya shiryeki jibeki ko kunya daga yabon Abunsa sai dadi kike ji, Kai na Naga Baki na a washe nace ai Ina sonsa da yawa ne kasan dai labarin Dana baku wlh gaskiya ne ba karya,gashi irinku daya da Sigar rada na sunkuya da fuskata saitin tasa na sa yatsa nace da sumarsa na taba da yatsa nace irin taka, table ya buga da karfi Ni babu me kama Dani a duniya malama ki nemeshi can wlh kika takura min bazan Nemo Miki shi ba.

I'm sorry bazan sake ba ka Nemo min shi,za a taimakeki kina Iskancin banza fitar min a Office,ba shiri nayi waje, Nan take yayi gayyar sojoji ya Basu Agogo da Zobe na yace wani Mahaukaci ne a Gombe ya Basu labarin yace nasan haukar karya  yayi ya yaudari yarinyar tana cikin wani Hali,so nake kuyi searching Gombe city da kauyuka a Nan zai labe dole, karshe yace cikin kwana biyu naji labari me dadi, ya dankara musu kudi,Sojoji suka tafi duba,Bai hakura ba ya Kara Kiran Yan sanda sukace a Basu hotonsa, ya tambayeni baki da hotonsa nace ka Basu hotanka kawai irinku daya,masifa ya fara wanne iskanci ne wannan shi za a rainawa hankali aikin banza aikin wofi.

Ya fadawa Inspector abinda nace Sukace tunda ba hoto to zamuyi Amfani da me kama dakai idan mun samu za a kawoshi ta nuna shi da hannunta tunda tasan Mijin nata.
Shashanci roko gidan kurma Haka ya Basu kudi masu yawa,a sannan na tabbatar Bai sanni ba,da gaske be gane ba,to me ya faru ko lokacin dai Bai Gama dawowa hankalinsa ba ko Kuma brain dinsa har yanzu akwai matsala,Kai akwai abinda ke faruwa ta karkashin kasa ya kamata nasa Ido a kowanne part na gidan Nan ko Zan samu gaskiyar lamarin.

Bayan 3days babu labari daga Yan sanda har sojoji sunce Basu ga ko me kama dashi ba,sai wani kodadden matashi fari rammame kamar me kanjamau, a sirri yace Nanee tasa driver ya kaini Office dinsa Ina zuwa Naga wani kanjamammen yaro kansa duk jijiya,ga wuya kamar

sanda,Ina ganinsa na fashe da kuka a wajen,Ice harda murna yace Alhmdllh an Dace Ashe dama Akan wannan kika jefa kanki a masifa? Sautin kuka na ya karu nace an cuceni kamata a rasa Wanda za a Nemo sai wannan me HIV, matashi kanjamamme yace ke yar Nan da kike ganina Haka da auren wuri nayi da tuni na haifi kamarki,kyan jiki Allah ya bani bana tsufa tunda nake Haka nake Dan caras inci zamani na naci na wani,.

Dariya Aliyu yayi Yana saman sit Wai kyan jiki ne dashi,nace ba shi bane ko Kama,Kai Ya Aliyu ai me kama da Kai nace yanzu ka yarda wannan me suffer Yan ruwan kamarku daya?
Dadi yaji na kirashi da Ya Aliyu dama ya tsani Ice din da Yan iskan yaran gidansu suka lakaba Masa.

Kudi ya bawa kanjamamme sunkai 30k yace Kuma a mayar dashi inda aka daukoshi Kar a ci Masa ko kwandala ya dinga murna da Godiya yace Hajiya zagin da kika min alkhairi ne idan da hakane ki fasa neman wancan nazo ayi Dani,Aliyu ya dinga dariyar mugunta yace Zan baka ita, haushi naji na Kama fushi Bayan sun fita ya rage daga Ni sai shi ya kalleni ya sheke da dariya yace da kuwa kin more chest din Miji, nace Allah kiyaye kirji kamar na fara,shegen kansa kamar electricer ne yayi wiring da wire.
Ban taba ganin dariyarsa ba irin yau Dan ya hada min mugunta yace to sai watarana idan na Samu time Zan kaiki da kaina har Gombe ki nemeshi tunda ke kin sanshi Zan ganshi idan baiyi Kama Dani ba wlh sai kinyi kwanan sell,nace ae aje zaka gani  kuma ana zuwa kauyenmu zasu ce Kaine.
Murna nakeyi zamuje har garinmu a can zai gane gaskiya Zan kawo Masa shedu.

Yauma rashin zuciyata yasa na dinga tunanin Danbature irin rayuwarmu ta farko kuka ya zo min na koma garden Ina ta burburwata Ina Shure Shure,nayi kuka na goge hawayena, nayi ta gwada Maganar Danbature Yana Mahaukaci nayi dariya Ni kadai, Aliyu Ice Yana kallo na ta saman bene can part dina,yau yaga Lallai aljanu gareni,kawai ya shika kitchen yazo da katon kwandon karfe na tace taliya, kamshinsa naji kawai nasan shine, sanye yake da 3Qtr da t- shirt ya dauki kyau sai sheki yakeyi, kwandon ya ajiye min a gabana ke ebo min ruwa cikin Nan,hhh nayi dariya a Raina Wai Dan ya gwada Ina da hankali ko babu,
Kawai na karba naje famfon dake garden na ajiye na saki fanfo shaaaaaaaa kwando baya rike ruwa,da karfi nace Ya Aliyu bahon Ashe ya tsage ta kasa kaga yaki rike ruwan,na dauki kwandon na dinga ball dashi nace Dan ubansa ni zai rainawa hankali na dinga haukar karya.

Aliyu sai ya yarda tsab Wai Banda hankali da gaske yayi dariya,ya tako har wajen yace yau na tabbatar da zatona,bani kwandona,baki na turo ya zaka ce na baka kwando wannan kwando ne Malam botikin zaka cewa kwando,ke psycho wannan basket ne get that in to ur Empty head ok.

Nace Dan Allah a Nemo min Mijina kaji Yayan gidan Nan, Ido ya kafe Ni dashi Yana son tuna Abu sai ya kasa yace badan halinki ba zansa a Kuma zuwa a Nemo shi ko wani state din ne kamar state uku,kamar gaske nace na gode Allah ya biya nazo na gyara ma part dinka?

Baki ya tabe yace shagiri girbau irinki Zaki shigar min part me kika iya yayi wucewarsa.
Haka washe gari Aliyu yace aje gombe again,kano,katsina idan anga me kama dashi a kamoshi nazo na nuna Mijina da kaina,sannan yace har gidan mahaukata aje a dubo me kama dashi.
Yan sanda harda Kara daukan pics din Aliyu.
Ya cika musu Lalita da kudi.

Nanee taji labarin a wajena ta dinga dariya tace Lallai Aliyu shashasha ne Ina za samu Mahaukaci, ta kirashi tana Masa fada,yace Nanee abinda yasa Zan taimaka Mata tausayi ta bani kullum kuka Akan namiji, gashi tana Mana girki me dadi oh na manta me Dan dadi dadi, ai kin sanni Ni bana son mace na kuka Amma sabo da Mum na tsani mata.

Kwana uku tsakani Aliyu ya sanarwa Nanee ta Sa Driver ya kaini Office dinsa an kawo masu Kama dashi har mutum biyar Dole a cikinsu a kwai mijina.

AsmaBaffa
[8/15, 11:45 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

31-35

Official

By
AsmaBaffa

Fulani Gal,Fateema Ig,silent Queen,Maman Husna,Bee'at,Bilkin Jml Maman Ammar,Haleecyy Sanee.

Ina Godiya da Sharhi ga page dinku.

MamanSamha,
Hauwa j,Auta,
Nafeesah Rabiu Godiya dubu nake da Sharhi.

Nanee tana sanar min nayi dariya a Raina kawai na shirya sosai Nasha kyau cikin atamfa sky blue and black, dinkin Riga da skert duk Wanda ya ganni sai yaji kamar ya sace ni, Driver ya ajiyeni a hadadden building na Aliyu na Shiga Office da sallama,ba tare da nayi knocking ba,ko kallona baiyi ba yace koma ki kwankwasa first, lips Dina na turo gaba nayi waje na kwankwasa na Dade tsaye sannan yace In...na Shiga,yace koma kiyi sallama, kunkuni nayi mutum ba wani ilmin Islam sai sallama, komawa nayi nayi sallama na shigo.

Kamar bazai magana ba ya amsa min, waya Naga ya latsa yace kawo min su, 15mnt Ina zaune a kujera maza su biyar tare da Dan sanda daya suka shugo tare da jerewa kamar Yan amshin shata.
Wani zabiya kalar kyankami jikinsa duk Rana ta Masa illa yayi wani rodi rodi,kazami na kalleshi na kalli Aliyu Wanda ya zuba min Ido irin ya gane ko an Dace,sabo da Allah ya Aliyu wannan mutanen ne zasuyi Kama da Kai,kalli fa Kai zabiya ne? Farinka na zabiya ne? to ai Baki San arziki ba shi yasa Zaki ce Haka, Kuma ma ai kalarki ne su sune dai dai ke Yar aiki, takaici ya kamani na kalli wani fari kwal Amma sai katon Baki da hakora nace cikin shagwaba kalli fa kamar Kare Yana cin floggi wannan.
Wani shi Kuma kamar Dan Igbo Ido ka rantse kwakwulosu akayi waje gasu jajir Dan wiwi,sai wani dogo kamar fol zololo dashi,wani Kuma me Dan kyau da sarkoki a kafafunsa da hannayensa Wai daga gidan mahaukata aka daukoshi.

Fisabilillah Ya Aliyu jiba fa na fara dire diren kafafu Allah Ni cutata kayi, har cikin jininsa yaji yanda nayi shagwabar,kallo na yayi kadan a ransa yace ta danyi kyau a fili yace kina matar wani kike min haka, zunubi akanki ba ruwana wlh, dama Mata yanzu haka suke da yawa mace da aurenta a gaban Namiji wurin aiki ko kasuwa tana yiwa wasu mazan abinda ya Dace ace mijinta take yiwa,tunda ke ba a Miki gwaninta tafi gida, I'm sorry na gode Amma pls ka shirya muje Dani dakai indai har taimaka min kayi niyya idan kana kusa za mufi gano shi Mijin nawa, a Raina nace sai Munje kauye ko brain dinka zata dawo ka tunani sannan a mota zance muje dashi Ina kallonsa kusa Dani Ina Jin dadina. Sallamar mutanen yayi da kudade yace a maidasu Suma.

A fili nace pls Sir muje tare I'm sure idan Munje da Kai Zan gane shi Kuma za a fi Saurin samunsa,ka taimaka min pls na koma kalar tausayi harda sheshekar kuka,ya Dade Yana ta aiki a system Bai kulani ba,Ni Kinga ban taba zuwa kauye ba ko kwana daya taya Zan je, Kuma Ni bana driving me Nisa,sannan ke bana ma tafiya a mota har wani state jirgi nake bi.
A kaini kazamin gari na rasa me Zan ci.

Murmushi nayi nace a kwai hotel fa,yace a kauyen Dan karya,A'a I mean a birnin sai kana kwana a can idan zamuje nemansa sai mu Shiga Mota muna zagawa gari gari ko ya kace? Pls Ya Aliyu,kaifa me taimako ne pls for the sake of Allah, do me a favor kaji.
Baki ya tabe idan na Sha wahala u wl pay for it,ae na yarda,Bari sai nayi tunani. Ya Aliyu...Kai ya rike kin dameni da surutu kije gida ki Mana abinci Malama kin tsaya Nan sai yunwa ta min illa to 1pm, sabo da nasan zuciyarsa nace na tafi,ko kulani baiyi ba.na koma gida abina na Shiga kitchen.
Anjima Zan fara Shiga part part Ina gaisuwa sabo da na fara binciken gidan Nan meke a kasa ne.

Da yamma 5pm na Shiga part din Anty Amarya Baturiya, Linda Kawarta da ita kanta Mum Ice sigari suke busawa ga shisha tulu tulu a gefe,kwalaban giya iri iri,ga kida na tashi, Sahr Yar uwarta Kuma Kawarta itama tana zuwa ta karbi sigari Kara daya ta dodani wuta a wacce ke

bakin Linda ta zauna,gaba daya sun matse a Riga da wando.

Sallama nayi na Shiga Palon Wanda hayakin taba kawai ke tashi,da Ladabi na gaishesu suka amsa,na nemi kujera kusa da Anty na zauna, sigari ta Miko min Kara daya tace bismillah,Kai na girgiza nace bana sha, giya ta tsiyayo min a cup tace Sha wannan sabon shugowa ce akwai sweet, nace A'a na gode.

Linda Baki ta tabe tare da Dora kafa daya kan daya saman table tana bulbulo hayaki ta hanci ta Baki, wasu mazan a ciki suka shugo Suma suka Dan Kora giya suka yi waje.

Harshe suka canja suna faransanci da Russian language sai gulmata sukeyi da yare Ni ban sani ba nayi tunanin Hira suke ma, kamshin Ya Aliyu naji nasan ma shine, yayi mamakin ganina a part din Mum nasa sabo da kaf gidan ba a zuwa part dinta sabo da idan kaje sai ace Dan shaye shaye ne Kai da fasikanci.

Yasan Lallai ban San halin uwarsa ba shi yasa na rabeta.

Ko kulasu baiyi ba ya haura sama ya fito da wani file zaiyi waje Mum dinsa ta Sha gabansa where do you think u r going? Gefe ya matsa fuska ba Rahma zaiyi waje tace You are working out of me How dear u Hydar, I'm ur mother not your age mate, zaka je wurin wancan foolish woman Asiya ko, don't try me I can kill u, u already knew me. Saida ya Gama jinta kawai ya bude kofa ya fita a fusace.

Ina kallo ta Kora giya a fusace,Linda tace ya rainaki danki, na Baki Shawara kinki ji,bazan haifi yaro yaki Bina ba da nice da tuni na kashe shi da bindiga komai son danake Masa.

Anty sama ta hau fiya fiya, Linda da Sahr suna tangadi sukayi waje ba kowa sai Ni kadai, a hankali na lallaba nabi bayan Anty zuwa sama.

Maganarta na jiyo sama sama tana waya, tace A.k wannan sirrinmu ne ba Wanda ya sani a gidan Nan,daga Ni sai Kai,naso ace kana Jin English ko wani yarenmu Wanda za muna magana babu me ganewa Amma Kai sai Hausa,hausarta marar fita sosai tace yarona nayi Masa tsafin..Amma tsafi baya Jin Sa,baya so na,shi ma Dr who nayi na gaji sun rike wasu banzan iyayensu na tsanesu nayi nayi yaki yi,ita kanta Asiya da kyar na maidata baya a gidan Nan,miji baya ko kallonta, Karimatu ce kadai na kyaleta itama Dan Ina Amfani da ita ne watarana, so yanzu abun ya Kara lalacewa,Maganar Dana fada maka din Nan wacce har ka bani Shawara ga allurar da za ayi Masa kasan nayi,to wlh sakinsa yayi fa ya dawo tuntuni, Ak yace tabbas sai dai in yaronki Aure yayi Baki sani ba sannan ya sadu da Matarsa,Amma in ba Haka ba wannan Allurar ta tsafi Bai karyewa Dole sai in aure yayi Kuma yayi sex da Matarsa ta sunna, ihu ta kwala Wanda ya firgitani, Amma ai na Baki wata in ya dawo hayyacinsa ki Masa wannan dayar wacce zai Kuma canjawa,da sauri tace yes tunda ya kirani a waya a jirgi na hada Baki da wani Likita da yaje gani a turai yayi Masa Allurar Amma ba abinda ya canja,bana so Naga yaro na Yana Ciwon hauka Ina sonsa,wancan ma fa ban San Ina yaje ba,kawai a gidan Nan ance ya tafi turai na boye Zancen.

Ok Ak kasan Maganar Nan wlh bana so ta tashi Naga kamar yaron zai iya dawo da ita, ka kawo Idea pls,dariyar mugunta ak yayi yace akwai sabon shiri dana hada Miki Nan da 2wk Zan Aiko yarona Yana kawowa ki aikata abinda nace na sharadi na,sannan ki samu doctor da zai Masa wannan a Karin ruwa za a sa Masa a hospital.

Kuka kawai nakeyi,tausayin Danbature ya kamani wannan wacce maganace ake Masa

wannan rashin Imani a kanta kuwa,Amma ban San Zancen ba,Jin kamar zata fito ta Gama wayar na sauka da sauri kasa na bar part din Baki daya,a Dan lungu na labe na share wayena na daidaita kaina,nayi part din Karimatu azzaluma.

Daga ita sai Kaninta Shehu Niga Yan Matan nata duk basa gida sun fita gantali, Zan Shiga Palon kenan naji Muryar Karimatu tace ai Ina Nan Ina target Shehu sai na Kori Maryam daga gidan Nan indai tsafi ne muma sai mu fara gwadawa ai mun San malamai muma tunda na hada muguntata taki ci Naga yanzu tsafi ke tashe Mata ko wacce tasan gidan Malam,kalli munafukar Nan Asiya wlh badan Allah ta mallake Ice ba,sai yanda ta juyashi Dan kawai taga shima me dukiya ne Bayan na Babansa,sannan yarinyar Nan ban yarda da ita ba, Danbature da Alama Asiya akwai target da take hadawa,in ba Haka ba ka taba Jin zukekiya Haka yarinya kamar ita tayi kanta ga iya kwalliya ta waye Yar University tace Wai itace Yar girkinta da Ice,yarinya Ido a soye,ka duba Dr who shima fa kusan yanzu can wajen Asiya yake, Meenal ce kawai a wajen mamanta,to Nima Naga Ana Bari na a baya,baza ta Sabu ba Dole na mike tsaye.

Naja Cilla wacce shugowar ta kenan tace Umma mu dai ba ruwanmu wlh Yan uwanki ne mu Amma baza mu je wajen Malam ba,wannan fagen babu mu,da kin tsaya iya muguntarki da yafi cewar Shehu Niga sarkin tsoro me Maganar Dan daudu yace oh Yaya Wlh mu Kam bada mu ba,yo me yayi zafi Dan Allah Dan Annabi malaman Nan fa idan ba waazi yake ba kalallahu kala rasulu to kusan bokayene ki fada wuta,ki siyi jahannama da kudinki,to Allah ya shiryeki,duk zaluncin da kike Bai Isa ba kinga Ni nayi Nan,Shehu Niga ya fito na buya yanda bazai ganni ba,Umma tace lusari dandaudu ai Kai kayi asara da Kai gwara Babu dama barinka akayi yafi sauki.

Cilla tace gaskiya fa ya fada haka rannan Ma fa nasan me kika hadawa Daddy kika saci kudi masu yawa,haba sister ace Daddy yanda yake rikeki da yaranki,gamu muma gaba daya dangi mun tare a gidan Yana biya Mana schl masu tsada,ci,Sha, sutura,komai munfi masu gidan ma mulki Amma sai kina satar Masa kudi me zakiyi dasu harfa kudin Ice dollars kike satowa Kuma masu yawan gaske Haba.

Ashar Karimatu ta dura Mata Wanda yasa Cilla ta haura sama da gudu tasan Yar uwar Tata yanzu tayi Mata duka ko tasa Soja ya zaneta.

Zaki fito ne cewar Karimatu.

Da sallama na Shiga Palon,tana ganina ta harareni, da faraa ta na gaisheta,tace to atsugwi anzo gulma ko,Dole ai Asiya ta koya Miki kinibibi, Haba Umma gaisheki nazo yi Naga na Dade ban shigo ba, tsaki taja tace to an gode idan Dan Allah ne.

Sama ta hau ta barni Ni daya na gaji na fito kawai na koma part dinmu, gobe in Allah ya kaimu zanje sauran part din.

Ina Shiga part dinmu Nanee tace ke kuwa Ina kika shiga ko yau baza muci Dinner bane? Murmushi nayi a nutse nace Umma da Anty na gaisar, ok muje na tayaki Nima na motsa jikina, muna kitchen da Nanee Ya Aliyu ya shigo kitchen din ya mikawa Nanee wasu files yace Nanee ajiye min wannan takardun wasu gidaje nane ki hada su a wancan, Ok Cewar Nanee ,Ni Kam dadin muryarsa nake ji ban so Kuma na kalleshi sabo da warning da Nanee ta min Bai son

kallo,nasan hakan lokacin yana kauye a Mahaukaci.
Takardun Nanee ta karba ta fita daga kitchen din,fuskata ya leka yace Yau ba kallo ne,matar wani tana kallon Namiji Wanda ba sadakinta a kansa,dariya ta na danne ba tare Dana kalleshi ba nace Namiji baligi Yana kula matar aure matar wani wacce ba muharramarsa ba Yana neman Jin muryarta sabo da yaji dadi subhanallah Allah shirya.

Ke me Zan kalla a Nan murya kamar ta zakara matar da Zan aura ai sai anzo kallon ta from different countries,kishi naji ya taso min na Bata Rai, Bai ce komai ba ya fita waje Yana ki shirya Nan da 2wks muje na taimaka Miki a Nemo mijinki kin takura Mana a gida.
Farin ciki da murna ya mamayeni burina kawai muje kauyenmu Naga dangina,sannan yasan Lallai shine aka daura min Aure dashi,tuna maganganun Anty Maryam Mum dinsa yasa lissafina ya rushe Baki daya, Amma Zan Kara dagewa nasan mene makarin next Allurar tsafin da zasuyi Masa.
Ita kanta Mum dinsu ta fara bincike ko da gaske danta Aliyu yayi aure to yaushe? A Ina? Wace matar tasa,ihu ta kurma tace karya ne,is a lieeeeeeeeee wlh ko wace sai na kasheta.

Waya ta latsa tare da Kiran Ak tace Ak ko wace Matarsa ayi min duba a gano ta,sannan pls a daure Mata mahaifa karta haihu har abada.
Ak yace aiki da tsada,tace Zan biya,yace ai tun Allurar da akayi Masa idan ya dawo hayyacinsa to Matarsa baza ta haihu ba, good Anty ta furta Amma gano min matar.
Da dare Ak ya kirata yace yarinyar tana kusa daku sosai Amma anyi anyi Dodo ya kasa nuna ta ko sunanta babu wani alamarta da za a gane, Anty ta fashe da kuka tace asirana zai tonu Ak pls helf me, gobe Zan turo yarona da kayan aikin.
Godiya ta Masa ta zauna hankalinta ya kasa kwanciya .

Washe gari da yamma naci kwalliyata sannan na fito zuwa part din Hajjo, tana zaune Ana matsa Mata kafafu kamar Babar sarki, Shekara tana zaune ta kawo Mata tsegumi Banda gulma ba abinda sukeyi, Hajjo tace Wai Alhaji Nasiru shi zaiyi gogaggaya da Dana Sulaiman, Shekara tace Wai Alhj Nasiru makwafcin mu? Hajjo tace shifa nawa ya Tara Dan ubansa,abinda motocinsa basa wuce na million biyar duk irinsu yaransa ke Hawa,shi Kuma ta million takwas,waye shi a kasar Nan sai ciki kamar an kifa kwarya cewar Shekara, Dariya Hajjo tayi tare da furta ai gani yake yafi kowa arziki musamman Yar Nan tasa Layula matsiyaciya,Ina zaune Ina jinsu suna ta zagin mutanen gida da makwafta, Shekara ta mike ta bar Palon tana waya,sai ga Yar Misisi ta zo ta zauna Nan ma ita da Hajjo suka Fara gulmar Shekara ai ta Zama Karuwa Shekara talatin da biyar taki aure waye waye,yi suke Naga abin bana karewa bane nace Hajjo na tafi to Algunguma saura naji kinyi gulmarmu ba tsoro nake ji ba ki fadawa Asiya nayi zancenta,dama itace ta aikoki na sani,ban ce komai ba nayi waje Misisi tana cewa Ni na tsani Yar Nan wlh Sam hankalina Bai kwanta da ita ba.

Hmm yarinyar data Fadi halin uwarta Wai Masifaffiya ce ai daga ji ba mutanen arziki bane ko daga Ina suke oho sai wani iyayi take a gidan Nan Wai ita me kyau cewar Hajjo.
Part din dangin Daddy naje duk basa Nan maza da Mata Wai sun tafi biki wasu suna cenema, part dinmu Zan koma motocin Ya Aliyu guda biyu rada radan gaske sun hadu masu

Masifar tsada suka shararo suka wuceni har kofar part dinsa Naga an tsaya sai da ya Gama Izza sannan ya fito cikin Shadda light blue yasha kyau kamar ka sace shi,ko wacce Shiga hawansa take ya iya wanka, labewa nayi Bayan flowers na dinga kallonsa Ina samun nishadi da farin ciki,har ya kule ciki sannan na tafi Ina Jin wani farin ciki.

Tunani na kusa kwana yau inayi akan ya zanyi Kar na Bari 2wks tayi suyiwa Danbature wata Allurar daban Kuma,ban San ya Zan bullo ba gashi lokaci na ja,Dole na rage zuwa schl,Ina Gama aikina Zan tafi part din Anty Maryam duk da basa kulani shaye shaye kullum shine aikinsu,wani mutum ne kazamin Arne yayi Sallama da bakar Leda a hannunsa,lokacin Ina zaune kusa da Anty daga Ni sai ita su Linda gaba daya basa Nan,sama suka hau suna wani nuku nuku,suna Shiga bedroom tasa key tace ya Haka? Ak yace tun last WK zai Aiko Kaya Shuru,da sauri na labe a jikin kofar, Maryam Anty tace yaushe za a yi Masa Allurar? Saurayin yace Nan da 3days karki Bari ya wuce 3days ba ayi ba,sannan sharadi Zaki bamu sperm naki Wanda ba na sex ba,Ok tace ya za ayi a baka Taya sperm ba sex, ya Ciro wani dogon roba ja yace da wannan zakiyi Amfani da kanki har kiyi realising ki bani na tafi dashi yanzu,ba kunya tace Shiga toilet,ya Shiga tasa key yanda bazai ganta ba,ita kuma ta bargaje a saman gado tayi amfani da kanta ta samu abinda take nema sannan ta budeshi ta sallameshi,tuni na bar part din cike da alajabi.

Addua kawai nakeyi na rasa ma ya zanyi karfa kwana uku su cika,Ina ta faman tunani na shirya Dining naji kamshin Ya Aliyu Yana baza wajen,Bai ko tsaya ba yace gobe tafiya get ready, da sauri na sha gabansa nace dan Allah Kar kace tare zamuje unguwa,kace Abuja zaka je meeting,Ni Kuma Zan sanarwa Nanee zanje ganin gida sai mu hadu a airport mu wuce ba tare da kowa ya sani ba bare azo Ana Mana wasu tunani daban.

Ashe da ragowar hankalin naki no wahala ya fice abinsa,Nanee na sanarwa gobe zanje kauyenmu Yayana baida lfy jiki yayi zafi,tausaya min tayi tace Allah ya kaimu Idan na shirya na sanar Mata,amma kar na dade,.

Abin murna da dare Ice ya sanarwa Nanee zai je meeting Abuja tace Fadila zata tafi kaima Haka da wa zanyi Hira,dariya kawai yayi yace ai bazai dade ba.

Inda Allah ya taimakemu Ice iya Nanee kawai ya sanarwa zai je Abuja.

Babu wanda ya sani,nayi Shirin sosai kayana kala biyar da tarkacen abin bukata,Shima gogan da nasa ya hada Driver ya kaishi airport ya sallami Driver Dan kar ya ganni,Nanee kudi da atamfa shadda ta bani na Kai gida tsaraba,naji dadi,taxi na Shiga zuwa airport, zaune na hangoshi yana Shan ruwa Eva yaci uwar wanka.

Yaga yanda Nasha kyau ya zuba min Ido kamar ya sanni,tunawa yayi matar aure ce sai ya dauke Kai gefe, Arabian gown nasa black and sky blue nayi kyau karshe kamar zanje Dubai ko wata kasa Haka na cakare,kana Nan Kaya yasa white crazy Jean da shirt sea green yasha kyau babu Wanda zai ce Dan kasar Nan ne ko girman Nan.

Yau Fadila za a Shiga jirgi, Bai ce komai ba yace muje Ina binsa a baya aka Gama screening muka Shiga jirgi,Ina kujerar baya Yana ta gaba Wai sabo da ina da aure bazai zauna kusa Dani ba.

Ni kuwa Dadi kamar ya kashe Ni gani ga Danbature sabo da rashin zuciya irin tawa,sai dai bana nunawa kawai mazewa nayi Ina Danna waya,Abu kadan zai juyo ya kalleni,idan Allah yasa mun hada Ido sai yace daina kallona, kan waye ya juyo Yana kallon matar wani? Banza yamin,Inda muke a jirginma daban ne wajen masu kudi babu Wanda zai ganka ko kaga wani, ,an fara bamu lemo,ruwa,ko tea,da abinci kafin nayi Maganar me nake so sai yace ruwa take Sha a Bata ruwa.

Takaici ya kamani shi Kuma harda kaza da fried rice da wani juice yace a bashi, yawu na hadiya Ina ta cika Ina batsewa ko kallo ban isheshi ba Yana ta ciye ciyensa Ni kuwa yace Kar a bani komai sai ruwa,ko Sha banyi ba.

Sai na tuna sanda Ni nake Nemo Masa abinci ko ta halin Kaka sai yaci,na bashi ma a Baki.

Bamu Dade ba jirginmu ya sauka a Kano state, Jakar kayansa ta Yan gayu ya Mika min wai ya gaji ansha tafiya me Nisa bazai iya dauka ba,nasan muguntarsa ce kawai, Aiko Haka na karba ga tawa wata rantsatsiyar mota na gani tayi parking a gabanmu ya Shiga Nima na zauna kusa dashi driver yaja mun kame a baya,muryarsa naji yace matsa can, Ina fa jikin kofa Ina kake so na matsa,rashin kunya zaki min Dan ba a Baki abincin jirgi ba sai fushi kikeyi, Murmushi nayi nace Akan me zanyi fushi,ke kika sani dai.

Tahir guest palace Naga an kaimu Hotel,nace da Rana Haka har zamu tafi masauki ai kamata yayi mu tafi neman Danbature gidajen mahaukatan idan mun Gama sai muje masauki ko?

Duk wannan gajiyar da gwajab jagwab din hanyar Zan iya fita wani neman wani Dan iska can,sai gobe yanzu Ni na gaji Hutawa zanyi,Kai sai kace mace gaka da kirar cikakkun maza Amma sai lalaci, Harara ta yayi dama nasan kallo na kike Kullum, dama Ina so na Miki Nasiha na manta,Sanda na kawo Miki mutane nace ki nuna mijinki,a gabansu kika ci musu fuska sabo da hankalin ki kadan ne,Dan Adam daraja ne dashi,kowa da baiwarsa,Basu sukayi kansu ba Allah yayi su,ki daina aibata mutum halitar Allah ne,kema da kika ganki haka ba Wai kin fisu bane,kin ci musu fuska Wanda a Haka sai da na Basu hakuri sannan na Basu kudade masu yawa,karki sake ganin mutum ko ya yake ki zagi halittarsa.

Nasan Gaskiya ya fada nace to na daina Astagafrllah, Ustaz na gode.bai ce komai ba.

Room biyu ya Kama nawa da nasa Ni tsoron Hotel nakeji Amma Haka na daure,Abinci yayi Mana order me tsada lafiyayye naci na Sha nayi wanka na kwanta saman lafiyayyen bed,bacci ya kwashe Ni ban farka ba sai Magrib,nayi sallah cike da nishadi nayi shirina sosai kamar zani wani party Nasha kyau na fito Zan zaga gari, arba nayi da Danbature ya fito daga mota shi da Driver alamar wani waje yaje, yasha kyau shima,kishi naji ko wajen wata yaje,haushinsa ya kamani na fice fuuu ta gabansa shima Bai nuna ya sanni ba.

Ko Ina ban iya zuwa ba kawai Dan tafiya nayii da kafa na dawowata na kwanta,da dare naji anyi knocking na bude Ashe abinci ya bayar a kawo min.

Washe gari ma 9am sai ga lafiyayyen breakfast, na shirya 11am yace na fito mu tafi,a motar jiya Driver ya kaimu asibitin masu rangwamin hankali.

Nasan ba Wanda Zan gani,aka bude muka Shiga,da yaga fari zai ce wannan ne ko? Nace

A'a, Muka Gama zaga har Private hospital na mahaukata babu,yace to muje Hotel Ni na gaji bazan iya zuwa katsina yau ba sai gobe nace to.

Mun sake kwana sannan muka sake Shiga jirgi zuwa katsina, yau ya daure yace mu zaga a yau mu tafi Gombe sai Murna nake zanje gida.

Mun Gama zagaye babu kowa Nan ma motar da aka kawo daban da Driver.

Muna jirgi zuwa Gombe yace Kai kirki da tausayina Sunyi yawa sai taimakonki nakeyi,kudina da lafiyata abin a jinjina min ne,Amma ko yabo na bakiyi ba,sabo da ke na fuskanci raini Ne dake.

Dariya nayi kadan nace  sai wani yabon kanka kakeyi Ni me zance tunda kayiwa kanka.

Muna zuwa Gombe na dinga Murna, yace to wannan garin zamu kwana biyu sabo da Dan iskan a Nan zai labe da Alama ma yaudararki yayi ya ganki wawiya.

Motoci a Gombe rantsatsun gaske biyu da securities suna binmu a baya,Wai baya Shiga kauye ba tare da tsaro ba,mutanen kauye suna da matsala aje a dakeshi a banza,sai na tuna sanda su Ya Musa suka Masa duka Yana Mahaukaci lokacin.

Har kauyenmu Ina nuna musu hanya.

Readers anan za a yita fa.

AsmaBaffa

[8/15, 11:46 AM] +234 813 228 4370: 🏕️HADIN KAI🏕️

36-40

Official

By
AsmaBaffa

Page dina ne Asmabaffa🤣 Allah ya ji kan Baffa Ameen.

Motocin kawai ake bi da kallo a kauyen Ana tunanin ko wani Senotor ne,ga tint ba a iya ganin kowa na cikin motar, a hankali ya kalleni yaga Ina ta washe Baki, Baki ya tabe na kalleshi nace na gode Dan Albarka Murmushi yayi kawai ba shiri,nace zaka ji Ana ce maka Danbature Dan Allah ka rufa min asiri kace Kaine kawai,ka yarda a Kaine Mijin nawa,idan ba Haka ba Ina cikin tozarta a kauyen Nan,ko me sukace kace are hane, ko kaji na fada Dan Allah kace hakane kawai,Bai ce komai ba kawai na dinga rokonsa Amma Bai ce zaiyi ba baice bazaiyi ba,Haka na hakura jiki na yayi sanyi nasan idan yace ba shine ba dariya za Amin ayi ta gulma.

A kofar gidanmu nace ayi parking,Bayan mun tsaya na hango Ya Salman,Mahmood,da Musa a majalasarsu da suka Saba zama sunyi kyau da kiba,da sauri na fita a motar,Ya Salman na Kira tun kafin na Karasa.

Suka juyo gaba daya suka ga wata balarabiya da kyar suka gane nice,Ina karasawa na Mikawa Ya Salman hannu muka tafa,yace ko waya babu? Nace surprise na muku,Musa yace

kin ganki kuwa haduwa,Mahmood yace da alama an manta da Danbature tunda Baki Kara Mana zancenba ko a waya ga kiba da kyau,wannan ya nuna tunaninsa ya Kare,nace hmm da bako muke fa Bari na kirashi,Motar na koma nace ya fito,yau shigar Wani Yard yayi me tsadar gaske,fadar kyansa Bata Baki ne, kafin kace me Mutane da Yara sun Fara cika wajen ganin Fadila da motoci harda securities.

DanBature ya zuro kafara daya daga mota Bayan an bude Masa Kofa,takalminsa kawai ya Isheka kallo,kamshinsa ya feso a garin,fitowa yayi daga motar kowa yace wlh Bature ne daga kasar waje,wasu suka Fara Fadila tazo tare da Bature,wasu suce ai kasar waje taje watakil suka taho tare,Amma da suka kalleshi sosai sai sukace mijinta ne Danbature Mahaukaci ya warke,ta Nemo mijinta.

Gari ya dauka ko Ina, Danbature kallonsu kawai yake yana Jin duk me ake cewa,to Wai shi yaushe yayi Ciwon hauka ne? Ya Salman gaba dayansu da murna suka tarbi Danbature suna Alhmdllh ya warke,sannu ya jiki? Fadila ya akayi ya warke? Nace ai tunda ya bar garin Nan ya warke gidansu ya koma,Ni Kuma a Lagos naje gidansu a Yar aiki me dafa Masa abinci sai muka hadu muka sake jonewa,yanzu yace muzo yana son yaga dangin Matarsa da garinmu.

Sukace Alhmdllh gaskiya munji Dadi,Danbature Yana gefe yayi galala kawai Yana ji Yana tunani shi ya za ace yayi aure,kawai Shuru yayi yace in sun gaji sa gane gaskiya.

Cikin gidanmu muka Shiga har Danbature Yana gaba kamar yasan gidan,na matsa kusa dashi muka jera Dan ace gaskiyane maganata.

Hajiyarmu ce taji kamshi ya bude gida,tana daga daki take kwallawa da karfi tare da masifa Kai Musa turaren da Hajiya Yabi ta kawo min tsarabar Makkah ka sace min ko,sai da na gargadeka to ka dawo dashi ko naci mut.....Sallama Danbature yayi cikin kasa da murya, kunya duk ta kamamu har su Ya Salman Sabo da yanda Hajiyarmu ke faman zazzago masifa daga dakinta, Sallamarma da fada ta amsa,Dan Palon da Abbu ke karbar Baki muka bude yasha gyara kuwa Yana kamshin turaren wuta gashi carpet ne me kyau kawai a ciki,sai wata makekiyar katifa sabuwa ga tudu ga Fadi Tasha bedsheet,Dan Bature ya zauna gefen katifar, ya Salman ya Kira Hajiyarmu,Anty kuwa tana dakin Abbu suna tare,Ya Musa ya kirawosu.

tuni nayi waje zanga Hajiyarmu,tana ganina tace Fadila kece kika dawo Haka? tana murna sosai muka gaisa sannan nace tazo da bako nazo,Abbu da Anty sun fito suka ganni,da kyar suka gane ni,Abbu Fadila ce fa da bako muke,Nan na tsuguna na gaidasu, Anty ta rasa ma Ina kanta yake ko me zata ce ma ba Baki.

Suna Shiga Abbu,Anty,da Hajiyarmu numfashinsu daukewa yayi na wucin gadi da suka gane Danbature Haka,Abbu a fili yace Lallai yanzu kake Danbature ba da ba,ikon Allah cewar Anty,Hajiyarmu tace Kai Dan Nan yaushe ka warke Haka? Abbu yace Sannu da jiki kasha jiki, Anty kuwa ganin Danbature me kudi haka tace oh ai mun Sha fama da Kai,har na tuna sanda muke tallafa maka da abinci, oh sai da jarin Zobo na da kunun Zaki ya karye a kanka,Haka Fadila take zuwa ta kwashi na dari uku taje ta tarairayeka kamar jariri ta baka ka zuke.

Allah sarki ai ansha fama ka godewa Allah ka rugurguza jarin bayin Allah da dama, Yaron Nan Talle me Lemo kankanarsa kullum ba yankewa, Abbu ya kafe Danbature da Ido yace to yaro Wai ya akayi ne Fadila yi Mana bayani Yata Ina kika tsinto abinki? Yanda na bawa su Ya

Salman labarin karya Haka na sake bada labari.

Abbu yace Allah me iko Yar Nan a kansa kika kaini Kara wajen Yan Hisba oh...yiiii Abbu ya fashe da kuka yaga kudi Wai Dan a tallafa masa,Shi dai Danbature kansa ya kulle Haka kawai a dinga kala Masa cutar Hauka,Ba yanda zaice su yarda kawai sai ya karbi taimakona ya sauka kasa sosai ya gaishe da Abbu dasu Hajiyarmu kamar gaske,Dadi ya kamani, yace Alhmdllh na gode kwarai da kulawarku a kaina na warke yanzu Kuma Allah ya hadani da wife dina nazo dama na ganku ne na kawo gaisuwa.

Anty tace ba komai wlh sannu da kokari ai kasha jiki,Hajiyarmu tace jarin goro da yarinyar Nan ta karya min a kanka ya baci,Dan kudina ta bankada pillow ta dauke ta siyo maka kayan dadi,kunya ta Kara kamamu yanda iyayenmu ke zubar da mutuncinsu gaban suriki, Ya Salman tuni Sunyi waje sai gasu da lemo kala uku harda Maltina,Ruwan roba.

Hajiyarmu tace gashi tuwon shinkafa mukayi miyar kubewa danya ban sani ba ko baya ci,Murmushi nayi nace ai wannan da kike gani saukin Kai gareshi zai ci.

Haka na kawo Masa tuwo Nima na ebo nawa,baya son ci Amma sabo da Kar suji Haushi na dinga Masa signa da Ido da kyar ya daure yaci kadan, yace to in kin Gama mu wuce ko? Abbu yace Haba Haba kawai ku kwana gobe sai ku tafi Amma kuzo yau ku koma yau bazai yiwu ba sai Gobe,kamar yayi kuka Haka yaji.

Abbu mamaki ya hana zuciyarsa sukuni tunda ya fita waje yaga motoci da Sojoji, Anty da Hajiyarmu suka leko suka Sha kallo, Allahu Akbar kaga kudi inda suke ,kudi na inda suke cewar Hajiyarmu yaro kamar shi yayi kansa,nayi dacen suruki,Anty bakin ciki tuni ya cika Mata zuciya Yar kishiyarta ta samu me kudi,Hajiyarmu ta kalla shekeke tace ke mene bakiwa mahaukacin ba? Kin manta Sanda kike cewa karta zuba Masa abinci a kwanonki me kyau sai dai ta dauki tsohuwar langa wacce ta farfashe tayi kwatsa kwatsa shine yanzu anga kudi ko? Hajiyarmu sarkin fada Nan suka fara musayar yawu sai da Ya Salman yazo ya musu fada,Ina dakin da Danbature yake muna Jin fadansu rangadadau kunya duk ta rufe ni,Abbu ma Yana ji muna tare ya mike ya fita Yana kaci abinci Aliyu kaji,tunda Danbature ya shugo baiyi ko digon Murmushi ba sai sau daya da zai gaishe da iyayena.

Su Ya Salman ma ganin ba wata magana yake ba sai Izzar tsiya sukayi waje abinsu,Ya Mahmood yace cuta ma fa tana tarar da Hali,ko sanda yake da tabin kai karku manta haka yake,baya magana sosai sannan baya wata dariya sai in Fadila ya gani itama ba sosai yake Mata ba.

Shuru yayi Yana ta faman tunani shi yaga ta kansa har yaushe yayi Ciwon hauka aka Masa aure karya ne bashi bane da sauri ya kautar da tunaninsa cewar karya ne kawai dai zai taimaka a bar kauyen a Haka.

Abincin fa?nace Masa kadan ya kalleni yace kin san Ni bana cin tuwo ko dazu ma karfin Hali nayi naci, a gida Kuma Haka nake bawai ko wani abu ba, ledoji bakake na ebo a jaka ta na shirya su tuwon da aka kawo Masa na kwashe rabi a leda,miyar ma Haka na daure nayi Leda cikin Leda yanda baza bule ba na bude Yar jakata ta kayan sawa na saka a ciki na zuge idan

min fita sai na jefar.
Na zauna gefe naci nawa,na kwashe kwaninkan na maida musu kaf,sai Murna Hajiyarmu take ta bude kwanonsa tace yaci Ashe Kai gaskiya baida kyankyami,waya yayiwa securities kawai su koma cikin garin Gombe gobe sai su dawo,shi ya zaiyi ance sai ya kwana, shi ya jawowa kansa daya biyo Ni yazo kauyen.

Da yamma Abbu yace sai mu fito mu zaga dangin iyaye,ba yanda ya iya Bayan munyi Sallar laasar muka fito, sai da muka Isa can Bayan gari daga Ni sai shi da ruwan roba a hannunsa yace jira Kuma ki juya bayanki fitsari zanyi,nace da ka Shiga toilet tun a gida yace bazan iya ba ko wanka bazan yi ba har mu tafi gobe, Shuru nayi kawai na juya bayana yayi fitsarinsa da tsarki yace muje.

Muna tafiya Ina Masa labarin irin yanda mukayi rayuwa da Danbature na Yana mahaukacinsa Ina nuna Masa wuraren da yake Zama da yanda yake komai,nayi hakane Dan ya tuna Amma saima dariya da yake kwasa watarana kuma yaji tausayina,Gidan da me gari ya bamu mukayi rayuwar aure na kaishi Ya Salman na Kira a waya nace ya karbo min aron key wajen Mai gari zamu dauki wasu Kaya, Aiko cikin sa'a ya bayar na bude gidan duk yayi kura komai namu Yana Nan inda yake nace ga gidanmu da muka zauna dashi kalli komai Yana Nan,muka Shiga na nuna Masa ko Ina,Yana mamakin rayuwa da Mahaukaci.
Shuru Aliyu Bai ko San munyi rayuwa a gidan ba,yace na jinjina Miki da kika iya kula dashi Haka,Allah ya dawo Miki dashi Kuma Allah yasa ya soki shima kamar yanda kike sonsa,Allah yasa ya Miki son da yafi Wanda kike Masa.

Ameen nace na Ina goge kwalla ta a boye Kar ya gane,tausayin kaina nakeji Bai gane komai ba,na rufe gidan muka tafi zamu Fara gaida me gari,Mutanen gari Majalisa majailisa kowa har Yara Ana ta tayani murnan ganin Danbature ya warke,ko Ina Zaka ji Yara Suna kwalawa Aliyu Kira Danbature... Danbature sai binmu sukeyi,manyan Kuma hannu kawai suke bashi suna gaisawa Ana Masa murnar warkewa, shi dai kallonsu yake a mahaukata Yana biye musu da Faraa kamar ya sansu ana gaisawa,Ni kuwa murna nake ya rufa min asiri banji kunya ba,duk inda muka je kawai kudi yake rabawa Yara da manya ba ji ba gani,wasu Kuma ya zuba min a jakata yace ungo kina bawa wasu.

Ta wajen Talle me Lemo muka bi Yana ganinmu ya mike tsaye yace jar uba Ashe da gaske ne me kudi ne Kuma ya warke,Kaga Danbature wlh da gaske ikon Allah,Dariya Danbature yayi Bai mikawa Talle hannu ba Talle ya fito daga rumfarsa sai gani mukayi ya cafki Hannun Dan Bature yayi gaisawar Dole dashi,Yana yashe Baki yaki sakin hannun Yana girgiza hannun Danbature Yana jero gaisuwa muna Ify,ya gida,ya aiki,ya birni,ya mutan birni,ya aiki,manyan naka kalau,Kuna Ify kun samemu Ify, Danbature yace Ify ya gaji da amsawa gashi yaki sakin hannunsa,gashi tafin hannun Talle duk kaushi,da kyar Ice ya janye hannunsa ta karfi,Talle yace oh hannu kamar adduga haka Kuna Jin dadinku,kudi ya bashi da Dan yawa, Talle sai Godiya yake harda cewa Lallai Dole ka kasa ni a wajenta. Lemo ya zuba a Leda da yawan gaske yace za a Aiko muku dashi gida,nace ka barshi baza mu cinye maka jari ba.

Gidan me gari muka je,Me gari ya dinga mamaki da murna,nace shine ya bamu gidan da muka zauna,Nan Danbature ya dinga zuba Godiya kamar gaske ya bawa me gari Dubu Dari kyauta.Me gari kamar zai haukace sabo da murna.

Bayan Nan Munje wajen Wanda ya bamu kayan abinci,Wanda yayi min kayan daki sosai ya musu kyauta ta ban girma,sai Addua da murna suke Mana,Ya Mahamood na nuna Masa nace shi ya biya Sadaki,shima Dubu dari biyu ya bashi,sannan yace ya bashi takardunsa zai canja Masa wajen aiki a Gombe,Haka nace Ya Salman farko aure shi ya dinga kawo abinci lokacin da iyayena suka gujeni,Shima ya bashi nasa,Ya Musa Haka,sannan duk ya karbi takardunsu, harda wasu kannen ya Mahmood yaran Kawu Usman da kawu Salisu mutum shida ya karbi takardunsa da suka Gama degree yace aiki a Gombe city inshallah, Kawu Salisu ma sunsha kyauta,matansu gulma ta koma ciki,Haka Kakanninmu,danginmu kaf sunci arzikin Danbature harda mutanen gari.

Ni tsoro ma naji irin kudin daya kashe ya wuce tunanin me tunani,ko na hanashi sai yace ba ruwana.sai dare muka dawo gida.

Ya Salman ya shirya Mana liyafa Gasashiyar kaza,Yan Shila,lemuka,fresh yo,ga chips hadadde.

Saman katifar ya kwanta Yana huce gajiya Bayan yayi sallar Isha a masallaci tare dasu Ya Salman har Hira suka danyi ba laifi.

Ina wajen Hajiyarmu muna ta Hira ta uwa da yarta, shi kuwa tuni yaci duk abinda Ya Salman ya kawo,ya kwanta Yana Hutawa sannan ya fita waje inda Suke taruwa ya zauna cikinsu Ana Hira jefi jefi yake Sa Baki,Bayan ya gaji 10pm kowa yana gida,ba yanda Ya Musa Basu yi dashi ba kan ya Shiga toilet dinsu yayi wanka yace bazai yi ba,Wai kunya yake ji gidan surukansa ne,dariya sukayi sun zata gaske yake yi,Ni kuwa nasan kawai fada yayi.

Da dare nayi Shirin bacci dakin Hajiyarmu tace in Banda haukarki Fadila ai wajen mijinki zakije ki Taya shi kwana,shi kadai a daki ba kowa ai bazai ji Dadi ba,ga su Ya Salman Suma ba dashi zasu kwana ba, nace kyaleshi Ni a Nan Zan kwana,Hajiyarmu ta dinga masifa ta koreni Dole nasa hijab na tafi dakin Anty itama tace can Zan tafi ta koreni da gorinta iri iri.

Na Dade a tsakar gida to ya zanyi Ni Kam,Zama nayi a tsakar gidan kawai sai ga Aliyu ya fito ya gaji shi kadai kamar maye, a waje ya ganni yace an koroki ko? Ke karamar kwakwalwa gareki kamar Baki sanni ba ai da sai ki zo ki fada min sai ayi wata dabarar, taso mu tafi,Mikewa nayi nabi bayansa yace muje zamu je yawo sai mu rage dare a waje can wurin 12am mu dawo sai ki kwana a zaune a kasa,ni Kuma Ina saman katifata tunda ke kika Jaja min masifa Allah ya gani kina matar wani Zaki sa Allah ya konani.

Haka muka je can waje ga sanyi anayi muna zaune kowa yayi Shuru shi waya kawai yake latsawa.

Mun Dade nace zaman Nan bashi da amfani kawai mu koma gida,muna komawa gida kowa ya kulle kofarsa Shuru gidan,hanyar dakin Hajiyarmu na bi yace bakya Jin magana ke ko?na dawo na bi bayansa Yana zuwa ya fada saman katifa ya kwanta.

Nima na kwanta can karshen dakin a kasa saman carpet.

Tunawa nayi da rayuwarmu ta baya yanda Muke kwana Shimfida daya,da Romancing dinmu na wani Feeling nake ji,Shaawarsa ta darsu a Raina sai mutsu mutsu nakeyi na kasa bacci na tsurawa bayansa Ido ji nake kamar na kwanta a bayansa na rungumeshi,a Raina nace Kuma ace ba Kaya a jikinmu Wai da naji Dadi,tsaki naja kadan na Kara juyawa baya,shi Kuma ya juyo ya tsurawa bayana ido,Yana tunani yanda ake cewa Ni Matarsa ce,duk da Hijab din dake jikina Bai Hana shape dina fitowa ba Nan ya Kare min kallo,ji yake kamar ya sanni tin da,Kuma ma me yasa idan Ana cewa Mijina nane yake Jin wani farin ciki da nishadi, Wani birgeshi yaji nayi,tunani yayi matar aure ce yayi sauri ya sake juya baya can.

Can dai yaji tunanina yaki barin zuciyarsa sannan ga wani Abu dake Masa yawo a zuciya abin yayi Masa yawa,can abinsa ya ciyoshi a hankali ba tare da ya juyo ba yace kika Ce Ni mijinki ne dai ko? Ina jinsa na juyo Ina kallon bayansa nace ae Mana da can ba Amma yanzu na gano Ni ba matarka bace, ba Kai bane Sam,yanzu na gane Kuna da banbanci,Haushi yaji sosai yace to me yasa Yan garinku kowa ya sanni,Kuma ma ai ke kika fada da kanki Yar rainin hankali makaryaciyace Dame ke tuntuni?

Nace ae ai dama Ni watarana nakan tsokani mutum na Shimfida masa karyata,yace to karya kike to nine Nan tunda kowa ya tabbatar nine kawai dai ban San me yasa ban tuna komai ba,Amma na fara ji ajiki na nine,Hmm ai nace na gano fa ba Kai bane,takaici ya kamashi yace to a nemoshi ya sakeki tunda baida mutunci.

Nace Nima abinda nake so kenan da Zan ganshi ya sawwake min kawai ko na Samu na auri wani,idan ya sakeki wa zai aureki nufinki? Nace samari ne Dani fa a schl fa da yawa.

Tsaki yaja kawai yayi Shuru abinsa Yana faman tunani shine ko dai ba shine ba har bacci ya dauke mu.

Mum Ice Bata San Ina Dan nata ya tafi ba ta Gama bincike ance Yana Abuja,bakin ciki kamar ya kasheta yanzu ya zatayi ga allurar zata yi expired gobe idan har ba ayi Masa aikinta ya rushe.ta gigice ga wayoyinsa basa tafiya.

Ni kuwa murna nakeyi Dole sai Bayan 3days zamu dawo lokacin Maganin Allura baida Amfani.

Washe gari da Asuba ya farka ya fita ba tare da na sani ba yaje masallaci tare dasu Abbu sai ladan yace liman baida lfy sai yau Abbu ya jasu sallah dama watarana shi ke jan sallar idan Liman bai samu damar zuwa ba,Aliyu yace Bari yaja sallar kawai,yau kowa yaji sabuwar Qiria na tashi a speaker kamar Shureim na Saudiya, Ni kaina karatun ne ya tasheni na rasa Muryar waye aka samu Haka kwaro a iya karatun Qurani,su Hajiyarmu ma da mutanen garin Ana ta tunanin waye wannan Haka sai Wanda suka je masallacin su suka tabbatar wa mutane cewar Danbature ne Mijin Fadila,lokacin Ina dakin Hajiyarmu ya Salman suka bamu labari Mijin Fadila ne yaja sallah yau,na dinga mamaki dama Ashe da ilminsa Lallai.

Bayan ya dawo ya samu bana dakin yayi kwanciyarsa yaci gaba da baccinsa Bai tashi ba sai 11am, Brush yayi ya wanke fuskarsa da sabulu a jikin fanfom gidanmu kamar wani mace,shi dai bazai Shiga toilet ba,muna kallonsa ya Gama,lokacin aka kawo Masa tea,doya da kwai da egg into egg,baisha tea ba kawai doyar yaci da kwai yasha ruwa faro ya Gama komai, Ni kuwa ban sake bi takansa ba suna tare dasu Ya Salman abinsu,nayi wankana na shirya tsab komai nayi

naci kwalliya sosai kyau dai nayi matuka,atamfa nasa Light blue Riga da skert ya kamani cif Ni,lokacin 12pm ya Kira Driver dinsa Wanda suka kawomu jiya sun dawo daukanmu, nace zamu tafi Amma Zan dawo Ni kadai,Hajiyarmu tace yaushe zamu zo aga gidan naku na Lagos,gabana ya Fadi na kirkiro karya nace ai iyayensa har yanzu Basu San da auren ba,da kyar idan zasu yarda sai dai a Taya mu da Addua Amma har yau Ina a matsayin Yar aiki a gidan daga Ni sai shi muka sani.

Hajiyarmu da Abbu sukace Allah ya kyauta,Anty kuwa sai cewa tayi Allah kiyaye Kar su sa ya sakoki cab kice aikin banza ne Ashe kina ruwa.
Shuru na Mata ya fito yace muje,nace Zamu tafi har Mota suka rakamu Bayan Danbature ya musu bulala da kudade.
Da gudu matakan tsaro daya ya bude min kofa na Shiga daya Kuma ya bude wa Danbature ta daya side din ya Shiga muka musu sallama Ina daga musu hannu muka bar garin,sai da Naga mun bar kauye naja ajiyar zuciya Ina godewa Allah da Danbature da ya taimakeni ya rufa min asiri na tsira da mutuncina.
Tunda muke a mota yake ta faman kallona nayi kyau da yawa,Abubuwa da yawa yake tunani a kaina,Ina kallonsa ta gefen Ido na.

yau kwanakin allurar Anty Maryam hudu lokacin yinta ya wuce tuni,tana ta faman Jin haushi ta gama Tara masifarta sai Danta ya dawo Aliyu zata ci ubansa zaiyi tafiya ya kasa sanar Mata tana uwarsa wacce ta haifeshi sai wajen Asiya zata ji labarin Yana Abuja,Bata San Abujan ma karyace daga Ni sai shi muka San inda muke.

Bacci ne ya kwashe Ni a motar Dankwalina ya sabule ya zame ta bayana gashina Baki sidik Wanda yasha gyara wani ya kwanto a goshina gashi har Dan saje ne Dani me santsi.
Yaune kadai ya tsaya yake ta faman Kare min kallo,mayafina ya zame kirjina luwai luwai ya bayyana,har gefen Boobs dina Ana hangowa,wani waje ya Danna a motar sai ga wani labile ya sakko ya raba tsakaninmu da Driver, sai da ya gaji da kallona ya tuna Ina da aure fa ko dai ba shine Mijin nawa ba.

Tuban muzuru yayi Yana ta istigifari Yana Kuma ci gaba da kallona,ganin Haka yaja tsaki yasa yatsunsa ya danne idanunsa na mintuna ya bude kayansa tar,ganin ya kasa dainawa sai kawai ya dakko dankwalina ya rufamin a kaina ya dakko gyalena ya yafa min a kirjina.

Ina bacci ban sani ba na Fado saman kafadarsa na kwantar da kaina baiyi wanka ba Amma ba Wanda zaice baiyi wanka ba,ga kamshinsa Yana tashi wani shock yaji a jikinsa Wanda Bai taba ji ba a duniya,na farka tuni naji Ni a kafadarsa wani farin ciki ya kamani ga kamshinsa me sani nishadi,wani shock nake ji Wanda bazan iya tashi a kafadar ba,sai kawai naci gaba da baccin karyata.

Shi Kuma ya kasa motsi sabo da abinda yake ji a jininsa,ga wani slow music dake tashi a motar me shegen dadi, kwanciyata na gyara tare da yin Mika a jikinsa, kamar zai Kama da wuta Haka yake ji a jikinsa tsabar feeling.

Ya kasa ko motsi gashi Yana so ya janyeni a jikinsa gudun shedan tunda yasan Ina da aure,Amma Kuma ya kasa katabus,Kara mika nayi na mirgina kirjina na fada Kirjinsa na lafe, wani Uban Hands-,up yayi Yana ta Mar mar da idonsa kamar Wanda kwaro ya fadawa a Ido,Wai Dan kar ma shedan yasa ya Kai hannunsa jikina shine ya dageshi sama, ji yake kawai kamar zai mutu, ganin Zan dauki hakkin bawan Allah na Kara zamewa na koma da kaina saman cinyarsa ban San anan balain yake ba,na dunguri abar Ashe tunaninsa duk a bacci nake yi ya wani ja ajiyar zuciya yace ya Allah Zan mutu.

Mikewa nayi da sauri Ina Sosa wuyana Ina bude Ido da kyar irin Nasha bacci,nace auzu billah kasan ba Kaine Mijina ba kana gani na kwanta jikinka cikin magagin bacci Amma baza kaji tsoron Allah ka tasheni ba,Bai iya magana ba kawai ya rufe Ido Wanda ya Gama komawa red.

Har Munje airport zamu Shiga jirgin Lagos yace an fasa bin flight muje a mota,mamaki ya kamani Ashe kawai ji yake baya so ma muyi sauri a koma gida mu rabu,nace in hakane ai bamu duba me kama da Kai ba a Gombe,mu koma aje lungu da sako,Nan take ya daure fuska yace babu me kama Dani a duniya kawai nine na yarda,kukan karya na saka nace Allah ba Kaine ba,to muje Lagos a jirgi zanje kawai na fadawa saurayina Dana ke so ba a ga Mijina ba kawai aje kotu ta kashe auren a daura Mana aure dashi, tsaki yaja ji yake kamar zuciyarsa zata fashe sabo da Jin haushin kalamai na,Alama na gani nasan ran maza ya baci nayi Shuru kawai.

Kuma yace mu tafi a mota nace hanyarfa ba kyau,Harara ya zabga min kawai yace muje Amma sai da ya tsaya a Hotel zaiyi wanka.

Shi kadai ya Kama room a hotel muna jiransa a mota yaje ya dinga darje jikinsa,brush ma kamar zai Ciro makoshinsa,ya Gama ya shirya cikin wasu shegun kananan Kaya 3qtr da Riga t-shirt harda wata pcap ta Yan gayu,ba karamin kyau yayi ba kamar a sashe shi kayan daya cire a hotel din ya bar musu,ya fito hannunsa daya a aljihu daya Yana Danna waya,kallonsa nake tayi kamar na lasheshi Haka nakeji,sai naji dama yanzu na kwanta a jikinsa ba Dazu ba,kafin ya shigo nayi sauri na dauke kaina ko kallonsa banyi ba irin Bai dameni ba.

Driver ya shigo tare da Miko Mana wata Leda yace Sir gashi abinda kace a kawo.

Karba nayi na Mika Masa ya karba Naga Guava,Apples, yogourt lafiyayyu,juice,Chewgum orbit,ya ajiye muka tafi Bai fasa ba yace a tafi a mota,na dinga murna ko banza zanga hanyar Lagos gani ga masoyina Yana kusa Dani Ina Jin dadina.

Securities din Yan Gombe ne ganin zai Basu wahala ya sallamesu da makudan kudade yace su koma aikinsu zai tafi a mota daya ta Isa shi da Driver.

Tafiya muke ba tsayawa tun Ina kalle kalle har na gaji,nayi bacci na gaji,munje tsakiyar Wani daji wasu Yan Fashi Ashe sun datse hanya Ana ta fashi muma harda mu,Na tsorata Ina Jin labarin Yan fashin Lagos kisa sukeyi,karfin Halin Aliyu ko firgita baiyi ba a nutse ya fita Ni kuwa gaba daya jikina rawa yake Ina adduoi,Driver ma ya kusa tsuga fitsari,Mata da maza ansa kowa yayi flat a kasa muma Haka mukayi sai da suka Tara mota da yawa suna karbar kudi suna sallamar mutane,Wanda baida su a harbeshi.

Aka zo kanmu,suka tashe mu,suka ce kudi, Aliyu yace nawa za a baku? Ogan yace au tambaya ma kake ku fada ko nawa ne Zan rubu ta muku check,Dariya sukayi Hhhh Lallai me

kudi ne,daya a ciki yace na ganeshi ana nuna shi News yafi karfin kudi wannan ko nawa ne oga,Oga ya kalleni yace Matarka Ce wannan?yace aa Kanwata ce,sai Oga ya Kira wani matashi a wata motar yace Kai yace Yi Amfani da wannan,kayi Mana kaca kaca da ita gabansa,kuka na fashe dashi Ina rokonsu wlh Ina da aure Kar ayi raping dina,Wani ciki ya kawo Hanu zai kwada min Mari,Aliyu ya rike hannunsa,su kansu kwarjini Aliyu ya musu sosai sai zasu yi Masa Abu sai su kasa,Oga yace wannan yaron akwai raini,ko Yan mafiya ne wlh dodo bazai Sha jininsa ba.

Matashin suka dakawa tsawa ka aikata abinda mukace,matashin ya taho kaina gadan gadan a firgice Yana sabule wando.

Yana zuwa ya finkoni da karfi ban San sanda na mareshi ba sabo da takaici da aurena wani banza zai rikeni,Bindiga ogan yasa ya saitani Dam ya saketa Aliyu kafin bullet yazo ya tare bullet ya sameshi ya zube Nan cikin jini.

Innalillahi wa Inna ilaihirrajiun na furta tare da Ihu na saki na fada kansa Ina kuka Ina Ihu da tumami,Driver ma yayo kansa,Sai mukaji jiniyar Yan Sanda,Nan Yan Fashi suka watsu a Daji da gudun tsiya.

Idonsa Ice ya bude da kyar ya Mika min Atm dinsa tare da fada min code number yace a jakana da International passport Ina da visa Usa kaini can,duba wayata zakiga suna Ayman ki kirashi ki fada Masa,close frnd na ne.. Nan ya lumshe Ido kamar ya mutu Ina kuka.mukayi sauri da Driver muka sashi a mota.

Wani private hospital muka kaishi can wani garin arna,kuka kawai nake Ina Addua Allah ya taimakemu Harbin a hannu ya sameshi aka cire bullet ya farfado,sai lokacin na Samu damar Kiran Ayman na sanar Masa,cikin kankanin lokaci sai gashi. Har yau dai Aliyu bacci yake Bai San me akeyi ba har mukayi kwana daya da yini.

Lokacin Ayman ya karbi komai a hannuna tare da tafiya Dani kawai yasa aka yi min passport da visa,nace nifa bazan je ba,yace ban San wace ke a wajensa ba Amma bani da time da zanyi jinyarsa a can ki taimakemu Zan biyaki kudin jinya pls, tunani nayi wata dama ce a guna nace na yarda Amma nawa za a biyani? Yace 1million karki Bari wani Dan gidansu ya sani kinji?nace to an Gama.

Aliyu yaki dawowa hayyacinsa numfashi kawai yakeyi Amma Bai ma San me ake ba,Haka hankalina a tashe muka tafi a jirgi har Ayman, wani katafaren Hospital muka tsaya a Usa bana kwanciyar hankali shi yasa ko kallon gari banyi ba bana ganewa kawai dai gani a turai dare daya,sai da yayi settling komai ya tafi tare da bani ATM yace Kar na taba kudin Aliyu ga ATM da kudi ko me ake so ko nakeso nayi Amfani dashi,sannan ga waya da number dinsa ko me ya faru na sanar Masa zai Kuma dinga Kira shima.

Wasu turawa biyu ya hadani dasu mace da Namiji masu taimaka min.

Ya hau jirgi ban San wacce kasar yayi ba Kuma.

Can gida Kuma Anty Maryam ta koma wajen tsafi an sake yo Mata Hadi Wanda za ayi,sannan ta koma gidan boka anyi mugun aiki an gano sunana Fadila Yar aikin Asiya.

Sosai Anty ta gano nice matar Aliyu,an Hado balai iri iri Ana jira na dawo Aliyu ya dawo a

Gama damu.ga aikin Dole sai muna Nan gidan za ayi shi, ita Kuma Karimatu ta shiryo nata kan Aliyu ya koma part dinta ya bar Asiya, ita zata mallakeshi, hhh Allah ya San gaibu mu Kuma kaddara ta Fado mun Cale turai Allah kenan me yanda yaso yasan kaza zai faru da Kai a wancan waje sai ya canja ma waje ta hanyar wata Kaddarar wacce Kai kana gani anyi ma ba daidai ba kana bakin ciki da kuka,Ashe baka San Allah yafi sonka ba.

🤣🤣🤣

AsmaBaffa